 SANYI DA ZAFI

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM

✍M SHAKUR

EPISODE 1

Anatse yayi sallama yashiga wani babban falon wanda suke kira da Shakallo dan sirri kadai kesa a shigo cikin falon, wani irin kirar samfarin gini akama dakin kaman wani museum, yanada fadi da kirma dakin ga wasu ado na gwalagwalai sai babban carpet daya lullube ko'ina a girman falon, sai filoli na tumtum dasuke jejjefe akan carpet din na kishingida anmai ado na sarauta a jikinsu.

Mutane biyar ne zaune a falon maza hutu sai mace tsohuwa guda daya, Mai Babban daki wacce take tsohuwa ta manyanta dan akalla zatai 76 da idanunta sukai jazur tana sanye da Alkaybba hannunta rikeda tissue dakuma charbi tanaja, sai Waziri, Wambai, Makama dakuma Sarkin dawaki, chan kuma saiga wasu Manyan dattawa maza guda biyu dake kama da Mai Babban daki sun shigo sun zauna suma, dan faduwa gabanshi yayi dan haduwan mutanen nan wanda bayan sarki sune masu fada aji a fadan nan kasan babban abune, karasowa yayi tsakiyan dakin sannan yasami waje yazauna yakalli Mai Babban daki yace "Gwaggo kene kika aika akirani"? Girgiza kai tayi kafin ahankali tasa tisssue saman fuskanta tashare hawayen tasss sannan tace "aminan mahaifinka sukasa akiraka amatsayinka na babban dan sarki Kabeer" dasauri yadagokai yakallesu sauran jama'an dakin dake kallonshi yace "tooh" anatse babban cikinsu Makama yace "kannenka duka sun iso? Dan karfe hudu zamukai Sarki makawancin sa" cikeda kamala dakuma natsuwa yace "Yarima Halilu, Ibrahima, dama suna nan, Munir yanzu yakirani jirginsu ya sauka a Abuja, shikuma Umaru yanzu haka jirginsu yatashi daga lagos din shikuma….." yay dan shiru, atare dukansu yan dakin sukace "Yarima Riyad fa"? Adan hankali yasauke yar boyayyen ijiyan zuciya yace "nakirashi ba adaddi bana samunshi" salati mai Babban daki tasaki tace "bantaba ganin gantalallen yaro irin Riyad ba, yau yana Egypt, gobe yana Cyprus, jibi yana Oman gata yana zanzibar, citta yana China ko Iceland, ohh ni Shatu, chanake yau yana France ka gwada number shi ta chan kuwa Dan Buri? Idan baka da number kaje wajen Fulani ka amsa" cikin murya mai laushi Dan buri (Kabeer) yace "Gwaggo kema kinsan baitaba yin cikakken wata daya agari dayaba yabarta yatafi wata, kuma har ita mahaifiyarshi Fulanin batasan inda yayi ba dan nasameta itama tana kiranshi baya shiga, ni narasa mecece matsalan Riyad da ya gwammace yayta yawon duniya daya zauna akasarshi inda aka yankemai cibiya, ya girma baisan……." Hannu sarkin

Wambai yadagamai yace “ya isa” yadan sauke ijiyan zuciya yace “yanzu dai sabida shi bazamu jinkirta yima sarki abinda yakamata ba, nasan duk inda yake aduniyan nan zaiga news na rasuwan mahaifinshi dan haka zamu ganshi, yanzu tashi katafi” tashi yayi ahankali yamike yawuce yafita yanajan dan tsaki aranshi bayan yakai waje.

Cikeda bacin rai daya daga cikin jama’an dake falon yace “Gwaggo I’ve said this time without number to Mai Martaba he should call Riyad to order, duk cikin yaran Sarki babu gantalalle kaman Riyad, yaki zama ya koyi komi na al’addun mu, yanzu me za’a gayama jama’a akaga shine kawai bayanan” kowa na dakin binshi yake da kallo sai dayan dake kusada shi da ake kira da Usmanu yace “a’a Yaya Riyad yarone mai natsuwa dukanmu nan munsani sana’o’inshi ke kaishi kasashen nan kuma Mai Martaba shiya ya aminta da hakan ya bashi go ahead tunda yaga yaron nada passion for business, Riyad yaro ne mai matukar kyawun hali ga tausayi dukkan mu anan munsan da hakan” cikeda zuciya yace “kai ina magana harka isa kabani amsa Usmanu” cewan yayan da ake kira da Hambali, zasuhau gardama Mai Babban daki tace “shup! Hambali Usmanu kunsan dan uwanku ya rasu kuwa? Fada kuke kokarin yi sabida danshi?” Shiru duk sukayi basu kara magana ba…

Direct flat din mahaifiyarshi Dan Buri yayi wacce take uwargida, wani irin babban gidane da is as if daga inda yake zuwa side din zaije wani anguwa ne, kana ganin Masarautan kasan akwai kudi bana wasaba, dudda ga mata ana koke koke bai hanashi yawuce su yashiga cikin flat dinsu ba. Tana zaune tsakiyan mabiyanta tana kuka yamata alamu da idanu datazo yayi sama, mikewa matar da akalla zatai 48yrs tayi tana gyara lullubi tabishi idanunta sunyi jazur, dakinta yabude kofa yashiga dasauri itama tashigo yamaida kofan yarufe yana manna key, cikin rage murya irin ta munafukai kaman ba itace ke kuka afalo yanzun nan ba tace “ya akayi? Me suka cemaka” Dan murmushi yayi yace “har yanzu ba’a sami Riyad awayaba Mama, abin yamin dadi” dasauri ta dunkulle hannu tawani watsa a iska tace “da kyau Alhamdulillah! Nifa dama Riyad ne kadai matsalata Dan buri dan duka yaran sarki kafisu kudi, kafisu ilimi sannan kafisu connection, gaka kafito daga tsatso mai kyau tsatsona, kuma kai akafi sani afadan nan, Riyad shikadai ne zai nuna maka arziki dakuma kwalin karatu tunda yanada PHD yanzu, amman banda haka meyafika dashi yaron da ko mata baidashi anata gulma ma ana cewa ba lafiya gareshi ba yanda yaki yayi auren nan, kowani Bafade ko jama’an Babbanka za’a tambaya wasukafi so yazama Sarki kowa cha zaiyi kai kai akafi sani kaine jagoran gidan nan kuma dan sarki na fari kasha kuruminka kaman kazama sarki kagama, yanzu dai bari a bunne sarkin anjima dakaina zanje wajen Mai Babban daki anjima, banda Riyad Baffanku Hambali shine mayen kujeran kuma zanyi komi na kaudasu, yi maza wuce katafi waje sabida jama’a su ganka ashaidaka, duk wani kaninka ko kanwarka dazasu iso ka tsaya ka rungumesu kanuna musu soyayya, kazama kaine tsaye akan komi kana kula da komi kaji hakan zaisa kasake farin jini, yanzu tafi tafi ko me ake ciki kadinga fadamin kodako awayane kaji, Mai Martaba yariga ya garzaya saidai

kuma mu hadu alahira Mulkin nan kuma tun kafin akaishi makwanci zan fara shige da fice saka akai, kaine d’ana dan fari kaine kuma magaji” Murmushi yamata sosai harda dan dariya yace “Mama kinyi ne arayuwa” da sauri ta shafa fuskanshi tace “kaga daina nuna farin ciki yi fuskan nan ne kaman kai kadai akama mutuwan nan agidan nan” gyadamata kai yayi yakoyi sakwa sakwa da fuska uwa zai fashe da kuka nan ko ranshi fess yawuce yafita daga dakin.

Komawa yayi waje inda dubbanin jama’a suka taru ga kannenshi su Halilu, Ibrahim, Shu’ibu duk sun iso da Iyalansu da akai cikin gida dasu Munir shine last person daya iso wajajen yana zuwa wajen da Babban wan nasu ke zaune yayi cikin jama’a tareda yayyinshi kafinma ya gaidasu yace “Dan Buri kasami Riyad?” Girgizamai kai yayi kaman salihin nan yace “no tunda kun iso yanzu za’a sallaci Baba bazamu jirashi ba kodama yana hanya ne sabida shi bazamu bari Baba ya kwana ba” Munir baice komiba yajuya yafito zuwa wani waje da ba mutane sosai yaciro wayanshi yashiga kiran Riyad danko jiya sunyi waya wuraren 1 nadare but numbershi baya shiga yanzu harzai maida wayan kunnenshi kaman wanda yatuna wani ba yashiga email nashi ya aikamai sako sannan yawuce yakoma ciki akai Alwala aka sallaci mai martaba aka bunneshi nan cikin fada.

Magana sai yawo yake kan duka yaran sarki sun sallaci mahaifinsu banda Yarima Riyad dan Sarki na biyar cikin yaran sarki maza guda shidda ran Dan Buri fess har wani kara haskakawa yake jin yanda rumors din ke flying.

Cikin gida Munir yashiga tareda yayyinsu zuwa babban falo da duka matayen Marigayiya Sarki ke ciki kowacce zaune sanye da hijabi idanunsu jazur ga yan uwa da abokan arziki duka aciki, wajen Fulani suka fara zuwa dukansu yaran anatse suka gaisheta amsa musu tayi suka wuce wajen Fulani 2 suka gaidata itama ta amsa su suka wuce wajen ta uku itama ta amsa ta hudun suna gaida aka dan zauna akai addu’a aka shafa sannan suka fice suka koma wajen maza dan karban manyan baki top politicians manyan kasa from across the world.

 SANYI DA ZAFI

EPISODE 2

✍M SHAKUR

Kusan gudu gudu, sauri sauri yake tafiya acikin airport din bai damu da bala’in gajiyan dayayi ba sabida economy ticket yasamu bama business ko first class ba, tunda aka haifeshi yaune first time daya taba flying economy, kafafunshi sun sandare abunka da mai tsawo sunma kumbura.

Fitowa yayi daga arrival yafara tafiya dan zuwa wajen parking motoci wasu mutane biyu biye dashi abaya dake sanye da suit bakake da glasses akan idanunsu, lift yashiga harya danna 2nd floor kofan zai rufe mutane biyun suka sako hannunsu ciki kofan yakoma yabude dan dago kanshi yayi yaga wani black mutum ne yana sanye da suit baki ga wanima exactly irin kayanshi suka shigo elevator din suka danna boturin dazai rufe kofan, kofan yarufe yafara moving sama, dauke kanshi yayi daga kallonsu yadaga hannunshi dake daure da agogo na Rolex dan duba karfe nawa yanzu hakanan yaji bai natsuba amman yadake yana tsaye inda yake rikeda bag pack din dake rataye shoulder nashi that is very fine and unique dan babu kalan su ma a Nigeria, hannu daya daga cikinsu yakai ya danna lock elevator ya tsaya chak tareda juyowa yana zaro wani wuka daga bayanshi in seconds yakai zai chakamai aciki chak Matashin yarike hannunshi yana kallonsu cikeda fargaba da tsoro da komima, dayan mutumin shima yaciro tashi wukar yace “au gardama zakayi bazaka bari mu kasheka ba salin alin mu karbi ragowan payment dinmu” shima yaciro wata karaman wuka zai chakamai kwasheshi yayi da kafa yafadi akasa wukar tafadi zai dauka yatake hannunshi da boot din kafanshi, yawani lankwasa hannun wanda yarike tareda sa kafa yadakeshi a balls dinsa cikeda azaba gayen yayi ihu yayi baya yakama gaban wandonshi yanaji kaman zai mutu da sauri guy din yasa hannu yabude kofan elevator din baimasan wani floor bane suke kawai yafice dagudu gudu sauri sauri dayan dake kasa yatashi yace “call the rest bari nabishi” yafice yabar wanda ke rike da gaban wando yana kokarin kiran waya, yashiga gudu shima yana binshi abaya, sosai yake gudu ganin daya yabiyoshi yanakai hannunshi cikin wando dan ciro wayanshi yakasa kawai yahau staircase yashiga sauka yana kallon baya jin gudun sahu dayawa ana biyoshi dudda baya ganinsu dan basu riga sun hayo benen ba ganin wani kofan restroom na mata dan ansa ladies ajiki yasa kawai yabude kofan yafada jiki wani kalan mugun karo sukaci dan tana shirin fita ne tai tangal tangal zata fadi da bala’in sauri ta dafa bango shikuma yajuya ya tura kofan bayin dasauri tareda saka sakata na sama da kasa yana kara murza jam lock sannan yajuyo daidai tana dagowa tana shafa goshinta cikin tsananin fushi dan tadan buge kuma taji zafi zatai magana, cikin a very soft yet anxious voice guy din yace “please ki boyeni some guys naso su kasheni ne and call the police” dudda taji zafin bigewan datayi amman ware manya manyan dara daran idanunta tayi kaman fitila tana kallon mutumin dayashigo cikin bayin mata da ranan nan Allah yaso ba kowa ciki ma, farin guy ne bawai irin fari sosai dan zata fishi haske but yanada normal fair skin not black skin, dogo wanda akalla zaiyi 34-35 ko 36yrs hakanan, baida kiba at the same time baida rama, yana sanye da riga na latest collection na Dior fari yadaura wani leather brown jacket asaman sa da

yabar boturan abude bai rufe ba hakan nasa kana ganin farin rigan ciki, saikuma yasa jean na Rick Owens, sai wani boot dake kafanshi brown na Tomford mai bala'in kyau da agogo daure a writs nashi na rolex, yanada very very dark hair dake nan kwance so wavy, dark eyebrows da eyelash nashi yamafi na wasu mata yawa, ga dan gemu dayake dashi da saje acike dudda gemun baida tsayi sosai looks like yana trimming gemun dan hair na wajen gabaki daya na dsame length, lips nashi are full irin asalin masculine lips that are a bit pinkish, idanunshi sunyi jaaa sosai, ganin yanda take kallonshi yasa yace "call security" hankalinshi atashe yadanna kofan da hannunshi yana kallon kofan jikinshi nadan rawa kana gani kasan da gaske he's in trouble jin gudun mutane dayawa haka ga maganan su yana tashi kasa kasa "baku ganshi ba? We have to kill him ance kar mubari yakai gida araye wannan kofan fa kunduba ciki ko ya boye wajen"? Hankalinshi atashe yajuyo yana dan zaro idanu hakan yasa itama gabanta yafadi bayin tashiga kallo kafin idanunta su sauka kan cart din garbage can dake wajen wanda take juye dattin bayi aciki ta gungura tafito dashi takai bola, daga kafanta tayi without making sound taje ta tsaya kusada can din tasa hannunta ahankali tabude marfin sannan tadago kanta daidai sun fara knocking kofan zaro idanu yayi da sauri ta nunamai can din da hannu alamun yazo yashiga nan da sauri yazo ya tsaya kusada ita yakalli bolan cikin can din wani kalan yatsinewa cikinshi yayi yaji kawai amai yatasomai da sauri yadaura hannunshi kan bakinshi jin aman zai fito, tazaro idanu tana kallonshi yau da babuma wani bolan kazanta sosai ma shine zaiyi amai lallaima, daidai an kara knocking dasauri da murya kasa kasa tace "kaga idan bazaka shigaba nifa ba ruwana, kafita ni nacigaba da aiki na, I don't have any security number I don't work here yau kawai an kirani nai replacing wata ne just for today" juyo da kanshi yayi yakalleta itama kallonshi tayi da manyan idanunta kusan iya kirjinshi tsayinta ya tsaya daidai anyi mugun knocking kaman za'a balle kofan baisan lokacin dayay tsalle yafada cikin trash dinba yasa hannunshi yana kama hancinshi lekowa tayi takalli ciki yanda yakeyi yasa tai dariya dayasa fararen hakoranta suka bayyana more of dariyan mugunta tace "yi bacci toh" kallonta yayi yanda take dariya dimples nata na lotsawa bama ta tsoro yanda kasheshi akeso ayi, bama ta tsoro tana mace itama sujimata ko su illatata, he's just staring at her da suprise, jakanta dake kan slap ta kalla saita wuce da sauri tabude taciro wani black gyalenta na abaya tazo wajen ta warware ahankali ta yafa kanfuskanshi, wani irin lumshe idanu yayi jin kamshi mai sanyi daya sauka kan fuskanshi mai ni'ima in this moment na wari dayake ciki sai kuma ya sauke gyalen da sauri ya kalleta yace "wat are you doing?" Tana kallon kwayan idanunshi itama ba kunya ko shakka tace "datti zan watsa akanka yanzu so brace up" takai hannun tadauki thrash can dake kasa wanda bata riga tajuye dattinshi ba kawai tajuye asaman kanshi tana murmushi ganin yanda yake kallonta kaman zai rufeta da duka tace "I am saving your life here it's your choice" wani kalan ijiyan zuciya yake saukewa tsigan jikinshi natashi da kyar yaja gyalenta yarufe fuskanshi dashi yana rufe idanun duka dan yakasa standing dattin datake watsamai akai ta ijiye can din tasa hannunta dake sanye da working glove nata ta kwashi sattın ta rurrufeshi da kyau sannan ta rufe marfin tadan sauke ijiyan zuciya cike da karfin hali tawuce tai wajen kofan tabude cikeda masifa tace "wai waye ke knocking haka

ina aiki”? Ganin maza kusan biyar yasa tadan koma baya kadan ta tsaya chak tana kallonsu dudda gabanta na faduwa bata nunaba dukansu kallonta suke ganin wata yarinya da akalla zatai 22yrs haka tana sanye da cleaners uniform riga da wando ash color tasa wani karamin farin hijabi daya tsayamata iya kirji hannunta sanye da glove kafafunta sanye da rain boot, cikin rashin tsoro tace “baku iya karatu bane duk girmanku ku gane ladies restroom ne nan”? Dukansu kallonta suke ganin yanda take musu magana gata wata kalan kyalkyawan yarinya fara sol saidai akwai uban baki ga rashin kunya ga muryanta shegen zaki kaman zai fasa dodon kunne, babban ne yahade rai yace “ke wani bai shigo nan ba”? Wani kalan matsiyacin kallo tamai tace “kai nan wajen yamaka kama da inda wani zai shigo”? Dukansu baki suka sake suna kallonta daya daga cikinsu yace “ke kinsan waye mu kike mai rashin kunya”? Tana kallonshi tace “kai kasan wayeni zakuzo ina tsakiyan aiki na bayan nayi stating agaban kofa working no entry kunzo kuna bubbugamin kofa kuna maza toh ubanme kukazoyi nan kuje men restroom mana, I will call security wlh” kallonta Oga yayi this loud girl can ruin work nasu ta tara musu jama’a yanda take this vocal ma killing her will never be easy still saita tara jama’a, they don’t want scene hakan yasa yace “please let her be she’s crazy, I don’t want problem, ku rarrabu kuje mu nemoshi ni nasan yana floor din nan” tsaki tayi tace “mahaukata kawai” dukansu su shiddan juyowa sukayi suka kalleta wlh ko dar batajiba tasa hannu ta maida kofan ta buga tarufe tadauki wayanta ta danna waka tamaida earpiece tacigaba da mopping kasan wajen wanda shiya rage mata dama tariga tagama wanke cikin bayukan yanda takebin wakan tana aikinta bata missing any verse wlh zaka dauka mawakiya ce kuma da karfi take wakan abinta……

Dudda yanajin warin bolan dayake ciki kaman zai kasheshi ga tsoron dayakeji but hakanan muryanta da yanda take wakan hold on na calming nashi down sosai, muryanta yamafi na asalin wanda yayi wakan dadi, what a voice! Tass tagama aikinta ta jingine komi inda zata jingine sannan tadauki jakanta tarufe tagoya abaya tasa hannu tabude kofan bayin hada ido tayi da maza biyu daketa sintiri awajen ta ballamusu harara tacire board na close dake gaban kofan bayin takoma ciki ta ijiye sannan ta gunguro garbage can din da kyar sabida nauyi amman ta daure tafita tafito dashi ko kallonsu batayiba saima wakanta data cigaba dayi abinta tawuce tasauka har kasa tazaga baya inda suke ijiye dattin saida ta jujjuya ganin babu kowa yasa tabude marfin bolan batare data kalli cikiba tace “you are safe yanzu you can come out” kafinma ya yunkuro tajuya abinta tahau tafiya dan sauri take is already 3:30 by 4 zata shagon abinci gashi this whole drama yabata mata lokaci, da kyar ya iya ya lallaba yafito daga bolan sai amai duk wani abu dayaci saida ya amayar dashi sai kakkabe jikinshi yake yadago zai mika mata gyalenta daidai tanashan kwana harta tafi, he wanted to say thank u dudda she’s a crazy wicked girl tana zubamai dirt tana murmushi but she helped him, hannunshi yakai aljihunshi yataba but baiji wayanshi ba kuma baisan a ina ta fadi ba wlh kuma shi

bazai duba bolan nan ba, daidai wani cleaner na gunguro nashi bolan dasauri yace “please bani aron wayanka nakira” binshi yayi da kallo ganin kaman ba lafiya yasa yabashi wayanshi Munir yakira kafin yayi magana yace “Munir kazo ka daukeni a airport pls karka fadama kowa kana zuwa katambayi wajen zuba bola ina wajen” kafin yayi magana ya katse wayan yabama yaron yazauna awajen kawai feeling terribly sick kusan 1hr yana wajen jikinshi yadau mugun zafi ga tsigan jikinshi na tashi kaman zai mutu yana zaune ahaka yaji ance. “Riyad” dasauri yadago kanshi da gudu gudu sauri sauri Munir yataho wajen yace “what happened to you like this? Wat are you doing here? Why are you so dirty”? Tashi yayi yana kokarin yima Riyad magana yace “someone tried to kill m…..” kawai ya sume da kyar Munir yasamu wani cleaner yazo kawo datti shima aka tayashi daukanshi suka tafi mota aka sashi sai gida bayan yakira Mom akira Dr.

Tawani special secret gate Munir yabiyo aka budemai already ga mutane tsaitsaye Gwaggo (Mai Babban daki) gawata black beauty mata dake sanye da hijab mai dan kiba (Mom), Wambai, Waziri, Kabeer da su Halilu, Ibrahim da Shuaibu, Baffa Mujitapa dukansu suna wajen da family Dr nasu, yayi parking agurguje Munir duk sukai wajen fashewa da kuka Mom tayi tace “what happen to yarona Munir? Wakeson kashemin shi daga shigowanshi garin nan? How did they even know ya shigo? Gwaggo jini a hannunshi look, Doctor do something” Mom tai maganan tana kama hannunshi ashe wukan ta yankeshi dazu, atare dukansu mazan suka ciccibeshi zuwa wani dabkareren flat na Mom Gwaggo tace “meya sameshi haka Munir? Jibi jikinshi? Meya faru Munir”? Dasauri Munir yace “Gwaggo nima bansani ba but kaman he was attacked ne, yana kokarin fadamin wai ana kokarin kasheshi ya sume ba wayanshi taredashi, shi babu akwati, akusa dashi, awajen bola naganshi da bag pack yana mota dawani dan kwali black, kafin yafadamin komi kuma yasuma” gam Mom tarike hannunshi har daki kan wani taskeken gado aka kwantar dashi Dr yashiga dubashi yanda skin nashi da fatanshi keyin wani bororo dahar wani motsi suke yasa yace “a chanzamai kayan jikin nan nashi maza, ku goggogemai jiki with clean towel, allergy ke damunshi, he’s allergic to dirt da kazanta right from small, kuyi sauri pls” fita kowa yayi daga dakin akabar Munir da Mom, Waziri da sauran duk suka zauna a falo yace “wazai attacking yaro daga durowan shi kasan nan?” Anatse Wambai yace “call the police I think sai anbincika airport din maybe ta CCTV za’a gani” faduwa gaban Kabeer yayi amman yadaure yaranshi always do a clean job he hope bazasu kwofasashi ba, fitowa Munir yayi yace “Dr an gama” dukansu komawa ciki sukayi Kabeer sai tsaki yake aranshi shida yakeso kowa yaji haushinshi amman jibi yanda kowa ke nan nan dashi, attention yakoma kanshi ma infact, skin nashi gabaki daya yakoma so red, drip akamai fixing da allurai ciki Dr yakalli Mom datafi kowa damuwa adakin yace “anjima kadan zai farfado don’t worry” dan murmushi tayi tareda gyadamai kai Waziri yace “ki zauna dashi” Gwaggo tace “nima ina nan kome za’a kawomai kowa zaizo yadubashi saina ganshi inga uban waye keso ya cutar mini da jika, bangama kukan mutuwan d’ana ba

yanzu halakamin jika za’ayi wlh jinina yasha karfin kowa” kallon Munir Mom tayi ahankali tace “thank you Munir” gyadamata kai yayi yawuce yafita daga dakin hakan yarage daga Gwaggo sai ita, dafata Gwaggo tayi tace “ki tsare yaron nan ki dage da addu’a akanshi, tun ranan da aka haifi Riyad akace yanada taurari masu kyau kuma babban mutum ne shi, kiduba kigani yaran marigayi maza shidda amman shi kadai akeso ahalaka tun yanzu kenan bama asan waye zai gaji kujeran sarautan ba kenan amman so ake akasheshi balle kuma ace shine zai gaji sarautan ki tashi tsaye Maryama, saikin tashi tsaye, kinyi zaman gidan nan basai na fadamiki hadarorin dake cikinsa ba, inde kalubale ne yanzu Riyad yafara gani, idan kuma yazama Sarki yadinga ganin kalubale iri iri kenan har abada, ki tsare yaron nan, kizama idanunshi kunnuwanshi uwa uba kizama inuwarsa dakuma lullubinsa” gyadama Gwaggo kai Mom tayi takama hannun Riyad tarike gam tana kallonshi tace “Gwaggo meya musu Riyad dako zaman gidan nan baiso, na tabbata baimason ya gaji kujeran nan, dan bata gabanshi” Gwaggo tace “kwarai” Mom tace “shi kadai Allah yabani, shi kadai gareni, Riyad kadai Allah yabani yau ana kokarin rabani dashi” kankame hannunshi tayi tace “Gwaggo zan iya zuwa bangon duniya sabida Riyad! Kuma nayi alkawari duk Wanda yace zai cutar da yarona saidai yafara dani dan daga yanzu zan zama shamaki tsakanin Riyad da komi na duniyan nan, zan zama inuwa hazo zan lullubeshi nakuma kareshi daga duk wata hari” sosai Gwaggo take kallonsu sai kawai tai murmushi tadauki charbi ta tacigaba da ja itama bini bini tana tofama yaron addu’a aka.

 SANYI DA ZAFI

EPISODE 3

✍M SHAKUR

4 daidai tashiga wani babban kanti na abinci irin local restaurant din nan, wata katuwar mata dake zaune a tsakiyan shagon kan kujera ga lalitan uban kudi a hannunta tana kirgawa ne ta kalleta tace “Allah yasoki baki latti ba” batace komiba kai tsaye tace “ina wuni Maman Miwa” batare data amsaba tace “nidai je ga wanke wanken ki chan na jiranki” bata damu da yanda tamata maganan ba dudda akwai mutane a shagon sunacin abinci tace “bari nai salla naje nayi” bata jira amsanta ba tawuce ciki chan bayan gidan shagon bayi taje tacire kayan jikinta tafito da dogon riga na abayan dake jakanta tana neman gyalen ta tuna tabawa mutumin nan tsayawa tayi chak sai kawai taja gajeren tsakiya saurin datake tazo nan yasa ta manta bata amsaba, karamin farin hijabin tasaka ta dauro alwala tafito tasami waje tai salla sannan ta cire hijabin tasa kan igiya fari ne batason ruwan wanke wanke ko mai ya bata mata taje gaban makwarara, ga wanke wanke zaka dauka na gidan biki

ne ga manya manyan tukunyan abinci, omo ta dauka ta tara ruwa abaho dukta kawo sannan ta dauki wayanta kirar vivo duk taci screen tasaka earpiece ta danna waka ta soke wayan aljihun dogon rigan tashigayin wanke wanken da sauri sauri dan tanada kuzari sosai batada kasala ko son jiki.

Wata yar budurwa ce tazo wajen ganinta tana wanke wanke tana waka kasa kasa like zero worries dinnan yasa ta harareta tajuya tafito tadawo cikin shagon tazo gaban mahaifiyarta dahar lokacin take kirga kudi tace “wai Mama Yar gidan HIV dinchan kikesa take mana wanke wanke har yanzu banace ki sallameta ba gashi gashi abinda ake cewa ita da Mamanta sunada shi” batare da maman ta kalletaba tace “koyar gidan kanjamau ce ba HIV ba ina ruwana ko kinada wanda zaki samo dazatamin wanke wanken nan ta share ko’ina har zuwa katon shagon nan akan dubu biyu kullum aduk fadin garin kanon nan?” Baki yarinyar tabude zatai magana Maman Miwa tace “kinga ki kyaleni fa, nagadai nace kiyi aikin nan bayi zakiyi ba” dasauri yarinyar tace “Mama ni kyamanta nakeji wlh, sunada HIV tana mana wanke wanke” dasauri Maman Miwa tace “wai sau nawa zan gayamiki Maman ta kedashi ba itaba yarinyar datake karatun likita, to koma tanadashi me ruwana nagadai ciwon nan ajini yake kuma baya kwarara acikin ruwan wanke wanke ko? Miwa dan Allah ki barni na kirga kudin nan kinatasa ina mance abinda na kirga” tsaki yarinyar tayi tawuce tafita daga shagon cikeda bacin rai.

Kafin 1hr tagama wanke wanken nan tass, tukunyoyin har bayansu ta wanke kal sai kyalli suke ta share ko’ina tashigo shagoma ta share tsaf tai mopping lokacin biyarda rabi sannan takoma baya tasa hijabinta tadauko jakanta ta goya abaya tafito tazo gaban Maman Miwa tace “nagama” kallonta Maman Miwa tayi tace “ohh kudinki ko”? Gyadamata kai tayi, kudin hannunta Maman Miwa tashiga kirgawa taciro 10k tabata tace “gashi na litinin zuwa yau juma’a” murmushi tayi for the first time dan gaskiya she hardly smile kaganta tana murmushi ko dariya to sai in tana tareda Mamanta, takirga kudin tass dubu goma chip chip tace “nagode Allah yabiyaki” tajuya tawuce kallo Maman Miwa tabita dashi ance duk muguntan ka kaji an maka wani addu’an saikaji ranka ya sosu harta fita waje Maman Miwa tace “Rasheeda!” Dasauri yarinyar tajuyo jin an kirata, komawa cikin shagon tayi tace “na’am gani” kallon sales girl dinta Maman Miwa tayi tace “samata shinkafa da tuwo a takeaway takaima Mamanta” wani kalan murmushi tayi dayasa wani hot dimples suka lotsa a kumatunta Ya Allah! She looks damn beautiful dasauri tace “nagode sosai, nagode nagode” Maman Miwa sai kallonta take dan wlh today is the first time in almost 3months data fara musu aiki take ganinta tana murmushi, yarinyar kam badai kyauba, ta tabbata badan cutan su ba da tuni wani babban Alhaji ya aure ta, kawomata abincin akai a leda ta amsa wannan karan saida ta duka tace “nagode sosai Maman Miwa” murmushi Maman Miwa tamata tace “sai Allah yakaimu gobe” gyadamata kai tayi tafice Maman Miwa tabita da kallo wani zubin she wants to be wicked amman kuma indai kai ba shaidan bane u can’t be wicked to this girl cus zata maka aiki tsakani ga Allah dabazaka taba ganin abinda zakai complain akai ba, wanke wanke take maka tsaf, tai shara tai moping kaga ko

ina na kyalli, banda haka daidai da tsinke bata taba sata a shagon ba wlh ko kwayar magi bai taba bataba dudda ko basudashi, kowa ya tsaneta kowa kyaranta yake sabida Mamanta but if u look at it ciwo nakan kowa, zata gudu tabar mahaifiyarta ne sabida tabada HIV? No, ba HIV ba ko HIVVV uwarta kedashi uwarta ce, dudda ma taji labari ance mai kudi mahaifiyarta ta aura but taje tai fasikanci tasamo HIV yakorota yace cikin ma ba nasa bane, hmmm tasauke ijiyan zuciya tace “Allah ya kyauta dai”.

Tafiyan datayi zaiyi nisan tafiyan inda zakaje kabiya 200 ko 300 kan adaidaita sahu amman akafa tai tafiyan nan tana shiga layinsu ta tsaya gaban wani chemist ta kirga 6500 tabashi tace “ga kudin maganin nagode” karba yayi yace “an dawo daga aikin Rashy” gyadamai kai tayi batace komiba ya karbi kudin yana kokarin kirgawa daidai ta juyo zata fito wasu maza guda biyu na zuwa wajen daya daga cikinsu yakalli mai shagon yace “kai Bala nagaya maka idan kana bari yarinyar nan na shigowa shagon ka bazaka taba yin ciniki ba ni nama fasa sayan abinda nazo saya mtswww yawa kake wlh gaye” yajuya harya fara tafiya Rasheeda tace “ko dabba yafi jahilin namiji mara ilimi daraja tirr, adaije makaranta akaro ilimi katon banza” chak saurayin ya tsaya saikuma ya juyo yanuna kanshi yana kallonta kur itama Rashida ke kallonshi yace “dani kike”? Dasauri Mai chemist din Bala yazagayo yana daga marfin kanta yafito yace “badakai takeba Rashida tafi gida kudin sun cika nagode” wani kalan kallo tama mai chemist din tace “akanme zakace badashi nakeba Bala? Inba dashi nakeba waye yamaka kama da jahili awajen nan”? Wani tahowa gayen yayi azuciye zai daketa yace “zan sumar dake wlh ke” dasauri Bala yatareshi yace “me haka kai Sani dukan mace zakayi”? Wani kalan dariyan daru Rasheeda tayi tasauke jakanta dake goye abayanta ta ijiye ledan abincin hannunta duka akasa tanuna kanta tace “nizaka daka?” Tasake dariyan keta tace “billahillazi yauka tabani saidai uwarka ta haifo wani zan gwada maka ni dakake gani kaman maza dari ce anan, try me I will make sure namaka abinda baxaka so ka karabin hanyan danake bi ba” tai maganan azuciye cike da fushi da masifa da rashin tsoro, dasauri Bala mai chemist yakalli abokin Sani yace “please rikeshi ku tafi dan Allah Kamal” kamashi abokin yayi yace “muje Bros shareta pls ba riba a fada da mace” Rasheeda tace “kasan Jahili baida ilimin sanin hakan wannan dahar yanzu ake raba shayin safe dashi agida” haba wani kalan fizge kanshi yayi yakawo mata duka da duka karfinshi kaucewa Rashida tayi da sauri yasami bango batai wata wataba ta daga kujeran dake wajen na zaman mutum plastic chair ne ta rapkamai a fuska kafan kujeran ya yakushi bakinshi haba bakinshi sai jini ganin jini abakinshi yayo kururuwa zaiyo kanta da sauri abokinshi da Bala mai chemist suka rikeshi, itama Rasheeda cikeda fitina ba tsoro azuciye tace “ku sakeshi yazo bakaga komiba duk bakin dazai kokarin bullying dina wlh saina fasa bakin, kai kayi kadan kahanani sakewa agarin nan sabida ka ganka namiji, akan wani dalili zaku hanani sakat bazan iya zuwa nasai abubu? Shaguna nawa nadena zuwa na layin nan? Wannan danake zuwa yanzu shima kuce ban isaba sabida wani dalilin ku na banza da wofi, cuta

nakan kowa, babu wanda yasan karshen shi, yes Mamana nada HIV and so what? Kubi duniya a sannu kai kanka bakafi karfin kasami cutan ba dakiki kawai mahaukaci, katon banza wanda ake gutsurama buredi agidansu har yau akasa dashi da kannenshi sabida baida zuciyan nema, kar Allah yasa ka kara zuwa shagon siyan abu, jahili kawai" cika shagon akayi da mutane sabida yanda Rashida ke zubamai zagi shikuma yana kokawa dasu Bala asakeshi ya daketa ganin yanda ta fasamai baki, cikin taron mutanen wani dan tsoho ya leko ganinta sai kawai ya shigo cikin shagon yakai hannu ya karbe kujeran ya ijiye gaisheshi mutanen wajen sukahau yi. "Barka da yamma Baba Liman" cikeda hikima na manya ya dubi Sani yace "ayakuri Sani, kekuma wuce mutafi" hannunta yakama yace "wuce mutafi" batai musu ba akumbure cikeda taurin kai tace "ni jakata" sakinta yayi yana kallonta taduka tadauki jakanta ta goya abaya da ledan abincin tarike a hannu tana nishi kaman kirjinta zai fashe sabida fushi saikuma ta dago azuciye dan tanada naci wani zubin kaman mayya, takalli uban mazan dake wajen duk ana kallonta tace "Baba Liman kagayama yan anguwan nan su kiyayeni nida mahaifiyata, bamu shiga gidan kowaba munyi sata, Mama harni baya shiga gidajensu sabida yanda kowa ya kyamace mu, bamu rokesu kudi ba, banzo nacema kowa yabani kaza zankai mahaifiyata asibiti ba dan haka su fita daga rayuwata dana mahaifiyata Baba, sufita na gayamusu, I am enough for Mamana! ni kadai zan iya kula da ita, nayi girma kuma Alhamdulillah inada karfin yimata komi kowa yafita harkana, ban nemi fadan kowaba ban shiga hurumin kowaba dan haka duk wanda yashigo tawa koshi waye wlh sai inda karfina yakare kagaya musu Baba Liman" tayi maganan with a sound warning, ahankali tsohon yace "ya isa!" wucewa tayi fuuuuu tafice daga shagon kowa na wajen jikinshi yayi sanyi wani dakeda shago kusada na chemist yakalli yaron yace "kudaina abinda kukeyi mutanen nan ba akanku suke zaune ba, wlh Allah zai iya saka musu, shidai cuta nakan kowa, yau dauka fasikanci matan tayi tasamu Allah masani amman ina mai tabbatar muku, gulma, keta, rashin mutunci da sa'ido da menene menene kukema matan da yarta kadai ya kore zunubansu" anatse Baba Liman yace "muji tsoron Allah, mun kyamaci mutanen nan shi kadai ya isa wlh kudena takura musu kar Allah yakamaku, kar Allah yakamaku" yawuce shima yatafi, dasauri Bala yace "nima kada ka kara zuwan mini shagona kaje wani chemist din" tsaki Sani yayi yace "ka dinga shiganmata ko zaka mutu iyayyenka dai damuka sani bazasu taba barinka auren tijararriyan yarinyar me kanjamau dinchan ba" yayi maganan yana ficewa dağa shagon abokinsa na binsa.

Gidansu na wajajen karshen layin, wani dan karamin gidane sosai ciki da falo daya ne sai bayi ba kitchen a tsakar gidan suke girki, ko'ina kal kal agidan, maida kofan tayi tarufe tasa sakata tasauke ijiyan zuciya sannan tai murmushi dan bataso Mama tagane ranta yabaci daganan zaure tai shouting "Mamaaaaa, Mama nadawo" tai ciki da gudu labule ta daga Maman na zaune kan dadduma kaganta kamansu daya sak da Rasheeda itama tanada haske but ba kaman Rasheeda ba, batada kiba ko kadan ta rame ta bushe sosai, duka duka bazata wuce 40 ba but she looks kaman

wacce ta tsufa, tana zaune kan dadduma tanajan charbi, ijiye kayan hannunta Rasheeda tayi saikuma tai tagumi tana leka fuskan Mama tace “Mama kiyi sauri kigama kimin sannu da zuwa niii” tafadi a shagwabe, hannu Ammi tasa ta shafe addu’an datakeyi sannan tajuyo kawai saita kama kunnenta ta saman hijabin jikinta tace “dan kaniyanki ba alwala yakamata kiyo ba kizo kiyi salla ba” dariya sosai tayi tana yarfe hannu tace “wayyooo kunnina Mama zai cire” sakin kunnin Mama tayi tana murmushi looking so happy tace “imaza to jekiyo alwala kafin lokacin magrib yafice baki salla ba” tashi tayi tafito tsakar gida alwala tayi tadawo tai salla kusada Mama sannan tadauki jakanta tabude taciro kudin tasa a hannun Mama tace “Maman Miwa tabiyani, hotel din nan gobe suma zasu biyani kuma manager tace nakawo zanen tagani idan na iya sosai zasu saya” karban kudin Mama tayi tana kallo tana murmushi Rashida tashiga fito da abincin tace “nabiya nabawa Abdul kudinshi Mama ga abinci Maman Miwa tace nakawo miki” bubbude komi tayi ta tashi tafita dasauri tadauko ruwa a bowl tadawo tazauna takama hannun Ammi tasa aruwan tace “wanke hannun muci” wanke hannunta Ammi tayi ta ijiye kudin agefe ta gutsuro tuwon instead takai bakinta bakin Rasheeda takai dasauri Rasheeda tace “Ammi ke kici” ahankali tace “ni naci abinci namana shinkafa, keko nasan tun safe bakici abinci ba banda karin dakikayi ko kinci wani abu”? Hadiye tuwon bakinta tayı tana fikifiki da ido most of the time idan tana aiki mantawa da abinci take, hararanta Ammi tayi tace “bude bakin, kidena wasa da abinci kinji Doctor” gyadama Ammi kai tayi tana murmushi Ammi nasa mata tuwo abaki tace “ko biscuit ne buy and eat kinji” sake gyadamata kai tayi, haka Ammi tadinga feeding nata kuma sosai taci ita bama tasan takusan cinye tuwon ba saida takalli takeaway dasauri tace “Ammi nacinye miki tuwon” murmushi tayi tace “haka nakeso dama Doctor” tass tacinye tuwon Ammi kuma taci shinkafan ba sosai ba dan batajin yunwa, sannan ta tashi taje tayo wanka da alwala tareda Mama sukai salla ta shiga tattara yan kwanukan zata wanke Mama tace “kibarshi jekiyi zanen ki zanyi wanke wanken” dasauri tace “Mama ni kidaina aiki, bayawa yanzun nan zanyi nagama zanyi zanen” kafin Mama tai magana tafice daga dakin biyota Mama tayi dudda haka tana wankewa Mama na dauraye wa suka gama suka dawo daki tayata Mama tayi ta kwaso board na zanen da colors nata da pen ta zuzzuba tafara zanen kome takeso Mama na mikamata suna cikinyi aka dauke wuta torch light Mama tadauka ta kunna Rasheeda tai murmushi tacigaba dayi sai wajajen 12 tagama tabarsu su bushe gobe zata sasu acikin frame, zama tayi anan danta huta kafin suje su kwanta sai bacci itakuma Mama na tattare brushes din tana dauraye mata su aruwa, munsharin ta da Mama taji yasa tajuyo takalleta ganin yanda take baccin azaune kanta na lilo.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 4

She just wished all this ayyukan wahalan da suffering da yarinyarta yar karama keyi just to take care of her itane keyi mutane bazasu gane rahama ne Allah yamaka lafiya sannan yabaka karfin nema ba gashi tana neman wannan karfin ita tafita tayo aiki ta kula da diyarta daya tak a duniya tarasa, Rasheeda ce zuwa ayyukan shara da wanke bayuka, da wanke wanke just to get paid suci abinci ga school duk ita kadai dan yanzu ma suna hutun school, yarinyarta batasan menene dadin rayuwa ba tunda ta taso sai wahala, Rashida doesn't deserve to be born like this, ta zaman ma yarta bakin tabo arayuwanta waye zai taba auren Rashida yanzu? Ko anzo ma gulman yan anguwan nan koransu suke, babu kalan sherin da ba'a musu, kowace budurwa irin Rashida nada kawaye ita batadashi kota fara kawance iyayen yaran zasu raba abotan sabida ansan diyar mai HIv ce, yar fasika ne gantalalliya dan haka babu iyayen dakeson yaransu suyi mu'amala da yarta, hawaye masu dumi ne suka gangaro daga idanunta dasauri takai hannunta ta share fuskan tass tareda sauke ijiyan zuciya ahankali tace "Allah na yarda ka kasheni da ciwon nan, Kama karomin cuta daban daban duk na yarda, amman Ya Allah kabama diyata farin ciki arayuwanta, Ya Allah ka kawomata karshen wahalan nan, Ya Allah idan mutuwata zai zamto abinda zaisa Rashidana tadena aikin wahalhalun nan just to take care of me Ya Allah ka dauki raina dudda banson na barta, Ya Allah spare my daughter this harsh way of living and take me instead" tasake share hawayen dasuka zubomata sai kawai tadaura kasan rigan atampanta kan fuskanta tai shiru takai 2min ahaka sannan ta mike taje inda take tallabota tayi tace "Raudah oya muje ki kwanta" ina batamasan anayiba baccin yayi nisa gajiya kuma kesata baccin kaman tamutun nan, kamata Mama tasakeyi tace "tashi muje kinji Rish-rish din Mama" Mama tai maganan tana dagata da kyar ina bamata iya tafiya kaman matatta, kakkamata Mama tayi tasata ajikinta tana tafiya da ita ahankali tanajan kafa kaman irin wacce tasha giya tai tatil din nan, uwar dakin babu komi banda wata yar katifa datake a gyare akasa sai kuma manyan ganamasgo guda biyu na kaya sai dan rio na kayan kwalliya da wasu kodaddun hodon makeup da gorunan turaren humra suke ciki saikuma wata benci haka da littafai ne cike na school akai saikuma lab coat da aka makala a nail na bango jikin aljihun an rubuta Dr Rash ajiki Mama ta kwantar da ita ahankali.

Karfe 4:30 daidai tabude idanunta adduan tashi daga bacci tayi sannan takalli Mama wacce taganta kan dadduma idan da sabo ta saba agurguje ta tashi waje taje tahura wuta tadaura ruwan wanka sannan tashare tsakar gidan taje ta wanko bayi ta watsa ruwan sanyi ita tafito tai alwala tazo ruwan yayi zafi tahadama Mama a bucket tadawo daki dan kaita bayin dan kafafunta na bala'in damunta tace "Mama

muje kiyi wanka” tana rike da Mama har bayi Mama tace “karki jirani jeki salla” batai musu ba salla taje tayi sannan tafito ta daura tuwo a wuta ta kwashe kayan da Mama tasa sharp sharp ta wanke ta shanya tasake wucewa hanyar bayi tadawo da Mama dakin dahar ta gyara tafita waje takarasa tuwo tai miya tazuba komi a kula takawo daki sannan ta shirya cikin wani dogon rigan abaya baki wanda stones din duk sun ciccire tadau gyalen zata yana kenan ta tuna jiya saitahau dariya Mama dake shafa mai tace “ke lafiyanki kike dariya ke kadai?” Dasauri tajuyo ta taho wajen Mama tace “Mama wani dan gayun mutumi nasa a bola na zuzzubamai shara bakiga yanda yake makyarkyata ba kaman da zinare aka yishi ba kasa ba” yanda take murmushi tana dariya yasa Mama tace “wa kikasa a bola Doctor?” Dan tsagaita murmushin tayi tabama Mama labari kunnenta Mama taja tace “Rauda wai mesa bakiji ne inda sun kasheki ke fa dakike musu rashin kunya ina kikeso nasa raina why mesa you are always putting yourself in trouble ne eh? Mesa bakiji wai kin dauka wani karfi gareki wai sabida wani baitaba chasaki ba ko” kaman zatai kuka tace “Mama yakuri to kisaki kunnena” sakejan kunnenta Mama tayi dudda bada karfi sosai ba tace “saina cireshi duka, wai mesa bakiji eh? Why wat if wani abu yasameki?” Ganin yanda takeyi da fuska kaman zatai kuka alamun jan kunnen namata zafi yasa Mama tasaki kunnen ahankali saikuma takama kafadanta cikeda damuwa sosai tace “Doctor kinason duk idan kin fita yanzu hankalina yadena kwanciya ne?” Dasauri ta girgizakai, ahankali Mama tace “to yimin alkawari u will not put kanki in any trouble again” murmushi tayi tace “I promise Mama bazan karaba” ijiyan zuciya kawai Mama tasauke dan tasan is impossible cus Rashida and trouble are besties, tashi tayi tawuce takarasa shiryawa ta yana gyalen akanshi ta kwashi uniforms nata tasa ajakan ta sannan tazauna tahada zanen tasaka musu frames Mama sai kallonta take kawai saida tagama tass sanan tazo kusada Mama lokacin 7 daidai tace “Mama maganin safe” tadauko magani bama Mama maganin tayi sannan tacire yar wayanta daga chaji tadauki earpiece dinta tace “Mama bari inje” cikin kudin data kawo jiya Mama tazare 1k tace “ga wannan kihau abin hawa kidena tafiya da kafa hotel din nan da nisa” dasauri ta girgiza kai tace “Mama ki ijiye duk nazuwa asibiti ne next week ni dakafata zan taka ai ba nisa ko ciwon kai kikaji ki kirani zanbar kome nakeyi na dawo zanyi aiki a hotel har karfe daya biyu yau ba airport zandaiga alert, sai karfe 4 ina wajen Maman miwa bye Mama na” dasauri Mama tace “to baxaki daure ko Lipton kisha ba tunda baki iyacin abinci dasafe” dukowa tayi ta rungume Mama tace “Mama zanyi latti ne nakai zansha a hotel din ai ana bamu coffee da biscuit bye Mama kinji” ta shafa fuskan Mama tana kallonta saikuma ta manna ma Mama kiss a goshi tace “Mama kinyi kyau wlh atampan nan zaki bani ita” dan maketa kadan Mama tayi tace “ba Dr yace kidena min irin abubuwan nan ba saina shafamiki ciwo” haderai Rashida tayi sosai tai sauri zata tashi hakan yasa Mama tarike mata hannu tace “zo to fushi kikayi banso kibar gida da fushi yakuri bazan kara miki maganan ba” hawaye idanunta suka tara saikuma tahadiye hawayen saikawai ta rungume Mama tsamtsam kaman yar yarinya tace “Mama ko duka ciwon duniya kikedashi ni zan fiso su dawo kaina ke naganki lafiyanki kalau, Mama kome kika dawo ko menene ajikinki you will always be Mama na nikadai, koda zan samu I don’t mind ni ko mutuwa yazo nafiso mu

mutu tare ma” dasauri Mama ta daki bakinta tace “bazaki mutu yanzu ba sainaga yaranki jikokina” turobaki tayi tasaki Mama tace “Mama ni banson maganan nan I hate maza to the core bazan taba aure ba, dana auri miji irin wanda kika aura danni ba Babana bane gwara na mutu ahaka banyi aure ba, matsiyac…….” “Doctor!” Mama takirata azafaffe hakan yasa tai shiru tadauke fuska, ahankali Mama tace “karki kuskura ki zagi Babanki” kallon Mama tayi irin why are you still protecting him sai kawai tayi hanyar fita daga uwar dakan cikin sanyin murya Mama tace “he’s your father” jakanta tadauka ta goya tace “Mama he’s not my father ko sunanshi dakikasa nake amfani da dan babu yanda zanyi ba, Mama na tsani mutumin nan and I hate all men naduniya, nidai mudaina maganan banmasan maisa kikemin maganan maza ba to mezasumin? Akwai wani hanyar neman kudi daban iyaba? Mama namafi mazan karfi laaaa nama manta ban daga karfe ba yau” tajuya dasauri zata fita daga dakin Mama tace “kika daga karfen nan saina mammakeki wlh waike namiji ne yau naga bala’i a hannun yarinyar nan” dariya Rashida tayi ta tsaya daga bakin kofa tana kallon Mama tace “Mama bakiga saisa babu me kawomin raini ba sabida ansan inada karfi Mama dan Allah kibari nadaga kinji Mama 2mins” da hannu Mama ta nunata tace “wlh zanci kaniyanki, sokike ki mummurde ki koma namiji? Wannan harkan karfen wlh bazan yarda dashi ba jira nake rannan lahadi idan Lawali yazo ince yatafi dashi” dasauri Rauda tace “wlh Mama karki bayarmin da abuna da kyar nasamu mutanen garejin nan suka saidamin da abin nan dubu uku” baki Mama tabude tace “yanzu bakisa dubu uku kin sayi sutura ba sai karfe kikaje kika saya agareji tafi aiki ki dawo zaki gamu dani wlh agidan nan” dariya tayi sosai saikuma ta buga kafa tace “to kice bazaki bayarba wlh Mama kowa kikaba sai naje na karbo abuna kota katanga ne saina haura” haba Mama tarike tace “to wani daban zan bamawa ba Lawal ba sai inga idan tsafi zakiyi ki gane wana bamawa, wuce kitafi” tace “bye Mama na, Mamana kyakkyawa mai gashi, Mama haryau gashina yaki kamo naki narasa maisa” kaman jira Mama take tace “sabida kin soma daga karfe ne saisa” dariya Rashida tayi harda kama ciki tace “laaaa Mama wlh wannan zuki tamallo ne” baki Mama tasaki tace “ni Mamanki ke karya Doctor”? Dan sosa kai tayi kaman mara gaskiya tace “uhnnn” kwapa Mama tayi tace “wuce kitafi zan gamu dake kika dawo ai anan zakizo ki sameni” nokekai tayi tana danne dariya tawuce tafita Mama itama tai murmushi ta daga murya daganan daki tace “ayi addu’a dai kafin afita daga gida Allah bada sa’a” tsayawa tayi tai addu’a sannan tabude kofa tafita abinta tana rike da frames na artwork datayi guda uku ga jaka abayanta she’s just a young lady da kana ganinta kaga strong, bright hardworking young lady, Nisan daga gidansu zuwa hotel din kusan tafiyan awa daya cur tabar gida bakwai takai hotel din by 8, Babban hadadden hotel ne shima gyare gyaran daki take da da bayika su wata wata suke biyanta 30k office na wajen da uniform nasu taje ta chanza kayanta taciro uniform din tana sawa Riga da wando ne tana kokarin saka karamin farin hijabinta wata tashigo dakin hakan yasa dasauri tajuyo hada ido sukayi da yarinyar tana ganin gashinta tace “Innalillahi Rashida kinasa attachment ne”? Dan zaro manyan idanunta Rashida tayi dan bama tasan gashinta ya warware ba hannunta yarinyar tadaura kan gashinta bakin kirin gashi da sulbi ga tsayi sosai tace “wlh gashin kine Woww Rashida hala ku ba yan Nigeria bane” fizge gashinta

Rashida tayi kaman fada tashiga parking tace “kada ki kara tabani” baki yarinyan tasaki tace “ohhh nidai bantaba ganin masifaffiya irinki ba daga na yabi gashinki Rashida sai fada” saka hijabinta tayi tace “aiki kikazo yi ko yabon gashi”? Tana maganan ta kwashi frames din tabar wajen yarinyar tabita da kallo har cikin ranta tanason tai kawance da Rashida but Rashida irin mutanen nan ne mafadata and too protective is as if batason mutane su shigo space nata because she don’t wanna get hurt oho, u can’t complement her, u can’t say anything to her fada but batada neman tsokana, bata shiga mutane ba ruwanta da kowa itadai tazo tayi aikin datazo yi lokacin tafiya nayi ta tafi ko minti daya bata karawa.

Sosai manager ke kallon zanen saikuma ta kalli Rashida tace “anya kene kikai zanen nan kodai satowa kikayi”? Zaro manyan idanunta tayi tace “tunda nake bantaba sata arayuwana ba idan baki yarda ninayi ba bani paper da pen da color namiki exactly irinshi agabanki” murmushi manager tayi takalli abin saikuma tace “zan saya akan 10k each sannan ki dingayi kina kawomin ko guda nawa ne zan saya” bakaramin dadi Rashida tajiba dudda zanen zane ne da har 100k zaa iya saya awani waje but bata damuba 10k is huge 30k ta kirgo tabata sosai Rashida taji dadi bata taba sanin zata iya saida zanenta ba kaman fa wasa taji ana maganan sayan frames tace ta iya manager tace takawo tagani jibi anbata 30k akan guda uku anatse tace “nagode Ma Allah kara arziki” dan tabe baki matan tayi tace “tafi kifara aikin ki” wucewa tayi tafita manager ta kalli frame din tace “zan gayawa Oga 150k each nasaya wayyooo this girl is talented bata sani ba inhar Oga yasosu zance muyi ma all rooms na hotel namu nabama yarinyar tamin I will be fucking billionaire nabata 10k each ni na karbi 150k for each awajen Oga wow look at her work”.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 6

Wallahi kanshi ma sarawa yafarayi jin maganganun da Mom kemai, first of all duk wani abun na sarautan su bayaso saisama baya iya zama agarin, baison hayaniya baison how they do things cus is always fighting, makirci and politics, and baijin tunda ya girma yatabayin cikakken 2months like good 60days agidan ba bini bini yabar country, lokutan salla ne yasan dole yake dawowa sabida yanda Baba ya maida abin mandatory yanason duka yaranshi to be home sabida hawan salla and other activities na al’adu, shi mutum ne da baisan mulki he prefer business nashi, he derive joy a business, it gives him purpose, for aure kuma dudda yasan culture

nasu ne amaka aure abaka mata but shi kwata kawata baitaba sanin Mom zatamai hakaba cus Mom is highly educated and expose, itama bata cika biyema culture ba saisa ma take barinshi to live his dream life, ko kadan bai shirya aure ba cus bayason commitment for now, his plan is nan da 2yrs zaiyi aure yanzu kawai aure baya lissafinsa, dukawa yayi ahankali gaban Mom yadafa kafanta kaman zaiyi kuka yace “Mommmmm” ahankali itama Mom tana kallonshi tace “Riyaddddd! You don’t have to say abinda zaka fadi kasan nasanka sama da kowa aduniya ko?” Gyadamata Kai yayi Mom tace “I know how you despise sarauta, mulki infact bakamasan komi akaiba, I know for auren zakace baka shirya ba bakasan damuwan mace da sauransu” sai kawai takai hannuwanta tai cupping face nashi cikin tattausan lafazi tace “dama akwai abinda zan taba so aduniyan nan dabaza ka iyamin ba Riyad”? Ahankali Mom tace “I thought nine number 1 dinka like you always say”? Dasauri cikin raunin murya Riyad yace “Mom u are my number 1 kema kin sani” kai tsaye Mom tace “inhar nine number one din naka then karka karamin gardama kan maganan nan it’s an order allow me to do everything am I clear?” Yadade yana kallonta yanda take kallonshi babu wasa kan idanunta yasa ya sauke kanshi kasa alamun dai baiso but baice komiba, baya iyama Mahaifiyarshi gardama, cikin fushi Mom tace “kamin shiru? Ban isa dakai bane ko ban isa nace maka haka nakeso kayi kayiba”? Tai maganan tana shaking leg in anger, abu yahadiye awuyanshi har saida taga motsin adam apple nashi asanyaye yace “okay” tsayarda shaking leg din tayi tai murmushi sai kawai ta matso ta mannamai peck agoshi tace “I wish kowacce uwa zata sami d’a mai mata biyayya kaman Riyad dina data zama very very lucky, Allah maka albarka kaji, Haleema is a good girl tana matukar sonka tun tana yar yarinya, she will keep my son happy I’m sure of that, so karka damu, zancen sarauta kuma I will teach you everything and you will do well kaji”? Gyadamata kai yayi zuciyanshi duk ba dadi duka duka kwanan Babanshi nawa da rasuwa but kowa is after kujeranshi, look at matayensu kaman ba mazajensu ne suka rasu ba dukansu kokarin daura yaransu kan Sarautar suke sunma manta da rasuwan shima yanzu yazama sarkin one day haka matarshi zatayi kenan itama yana mutuwa all focus dinta will be yanda danta zai gajeshi bamatada lokacin yimai addu’a tashi kawai yayi yajuya yayi kofa.

Mom tabishi da kallo ranta fess, dolema Riyad dinta yadinga intimidating kowa, yafi duka yaran sarki kyau ga kwarjini ga haiba ga natsuwa, ga jan aji, ga kudi, ga rashin magana, ga rashin shiga mutane, gashi baida kallon mata shi kadai keda qualities na sarki and bazata hutaba saita maidashi sarki wannan alkawari ne!.

Dakinshi yashiga Munir dake danna laptop yabishi da kallo ganin yanda mood dinshi ya chanza tashi daya, Wucewa yayi yafada gado yakife cikinshi tareda lumshe idanu Munir baicemai komiba yacigaba da abinda yakeyi abinshi.

Yana fita Mom ta daga wayanta takira matan Waziri da ake kira da Mariya ringing daya ta daga wayan tace “ranki shi dade Uwardakina, Allah yaja zamaninki Umman Riyad” dan murmushi Mom tayi kafin cikeda isa da jiji dakai tace “dole gobe Haleematu zata koma makaranta ne”? Dasauri Mariya tace “ai Uwardakina ko makarantan kikace karta kara zuwa saita zauna” jinjina kai Mom tayi tace “tom inaga bazata tafi goben ba dan zan turo Riyad yazo ya ganta inaso nahada su aure inyaso bayan yaganta zata iya tafiya” wani ihu Mariya tayi cikin waya saikuma ta zube kaman tana gabanta tace “nagode nagode Uwardakina da wannan karamci naki, kidubi kowa na gidan nan amman kuka zabinma Yarima Riyad Haleematu nagode, namiki alkawari bazaki taba samin matsala damu ba, I will forever be loyal to you, Haleema zata bautamiki Uwardakina, kuma da yardan Allah kujeran sarautan nan ta Yarima Riyad ce ai naji jita jita, da yardan Allah shine magajin sarki” dan murmushi Mom tayi tace “Waziri ya shigo yakirani” tana maganan ta katse waya wani ihu Mariya tayi tamike da gudunta tafice zuwa dakin Haleematu kai tsaye tabude kofan yarinyar na zaune sanye da rigan bacci tana kokarin hada kaya Maman kawai ta dagata tana juyawa tana rawa abinma saiyasa Haleematun dariya tace “Mommy menene kike murna haka”? Cikeda jin dadi tace “yanzun nan Sarauniya Maryama takirani tace tanason hada aurenki da Yarima Riyad gobe ma zata aikoshi gidan nan” wani kalan zaro idanu Haleema tayi she can’t believe abinda taji tun tana yar yarinya takeson Yarima Riyad yahadu ne over wlh, lips nata rawa suka fara farinciki yahanata magana tace “Mommy mekikace? Yarima Riyad mene? Dan Allah maimaita”?Kyalkyacewa da dariya Mama tayi tace “dalla cewa nayi za’a aura miki Riyad zaki zama matan sarki dan ina mai tabbatar miki shi za’a bawa Sarautan” ihuuuu tayi tareda wani kalan tsalle ta rungume Mamanta sai kawai tahau tsalle sosai lekowa dakin Waziri da shigowan shi kenan yayi ganinsu yayi murmushi waya na kunnenshi Mama zatamai magana yadaga hannu yace “inajinki ranki shi dade” wucewa falo yayi yazauna Mama da Haleema suka biyoshi a speaker yasaka wayan dashi da Mom ke magana suna shirya komi kaman ba mutuwa aka musu ba, planning auren da yanda zasu sami kujeran suke hankali kwance.

**

Wuraren 10 yafito daga dakinshi yana sanye cikin wani farin yadi da akamai dinkin jumper yamai kyau sosai sai kamshi yake zubawa kaman zaije gasan turare, binshi da kallo Mom tayi tana murmushi tace “Son katashi? Munir yashigo yakai sau uku nacemai bai isa yatasheka ba, bayan kunyi sallan asuba tare a mosque” karasowa yayi yazo kusadab da ita yazauna ahankali yace “morning Mom” as usual pecking nashi tayi a goshi tareda shafa kumatunshi tace “morning Riyad, yaya jikin? Zakai

breakfast yanzu ne”? Girgiza mata kai yayi alamun no, dasauri tace “to maza je Gwaggon ku ta aiko dazu akiraka kadawo saikai breakfast kafin kafita fada ko”? Dan gyadamata kai yayi yatashi ahankali yayi kofa haryasa hannu zai bude kofan tace “idan tamaka maganan auren Haleema kai naam” dasauri yajuyo da kanshi ya kalli Mom dauke kai tayi kafinma yamata wani maganan, dan jim yayi sannan yabude kofa yafita ma’aikata fada sun cika wajen yawanci Mom bata barinsu falo so anan waje suke yashe kaman kaya, gaishe gaishe da kirari sukahau mai ya wuce abinshi ko kadan baison zuwa wajen Gwaggo shi kadai hakan yasa yaciro wayanshi daga aljihu dailing number Munir yayi ringing daya yadaga yace “kana’ina”? Daga dayan bangaren yace “ganinan daure da towel wanka zan shiga” dan yatsine fuska yayi yace “be fast to” ya katse wayan baiso ya koma ciki dan baiso Mom tasan baijeba kuma baison yayita tsayawa awajen hakan yasa yawuce flat din su Munir wanda da dan tafiya sai gaidashi ake bai amsa kowa har gaban flat din tsayawa yayi jimmm awajen sai chan yasa hannu yabude kofan da sallama ahankali hada idanu yayi dawata mata dake zaune a falon sanye da hijab da charbi a hannunta kaganta kaman ita tai kakinshi ta tofar sunyi kama sosai, itama tanada haske kaman shi, sauke kanshi yayi kasa da sauri sannan ahankali yashiga ciki tareda maida kofan yarufe yama kasa magana, tadade tana kallonshi sannan tasauke kanta kasa tace “Munir nasama kaje ka sameshi” gyadamata kai yayi sai chan kaman me tsoron magana yace “ina kwana Mami” batare data kalleshi ba tace “yajikinka dafatan basu maka komi ba”? Dan dago kanshi yayi yakalleta ganin kanta akasa yasa shima ya maida kanshi akasa yace “I’m fine” daidai lokacin Munir yaleko daga sama daure da towel yace “ina fitowa daga bayi naji kamshin turarenka wlh daukomana breakfast kataho dashi” mugun kallo yamai saikuma kawai yawuce dinning din yazauna yana bude warmers din saman table din, ganin shayi dayaji kayan kamshi mai zafi dasauri ya zuba a cup ya debi waina da pepper soup yadade rabon dayaci traditional food kawai yahauci bini bini Mami na dago kanta tana kallonshi dudda yabama falon baya, sosai yakecin abincin dan yanada ci yana cikin ci wayanshi yahau ringing ganin Mom yasa yahadiye wainan bakinshi da sauri yakai wayan kunnenshi kafin yayi magana cikin kakkausan murya strictly Mom tace “kana ina Riyad?” Kasa magana yayi yay shiru cikin masifa sosai Mom tace “okay sabida na barka tareda Munir shine yanzu gidansu kake zuwa kasan nida matan nan bamayin juna but you keep going there kana ganin gidan nan kowani yaro najin maganan uwarsa ni ban isa kaji nawaba ko ai shikenan kayi duk yanda kakeso…..”
“Mommm!” dip ta katse wayan dasauri yatashi yajuyo sauke kanshi kasa yayi cikeda girmamawa yace “Mami bari naje in Munir yafito yasameni awajen Gwaggo” ahankali Mami tace “okay” kofa yayi dasauri yabude yafita tabishi da kallo sai kawai ta sauke ijiyan zuciya, wajen Gwaggo yawuce, Babban flat ne uwa gari guda, ga hayaniya ana shiga da fita masu aiki sai gaidashi ake kaman anga sarki amman ko kallon mutum daya baiyiba harya shiga dankareren falon Gwaggo, dudda dakin yacika da mutane yana shiga Mai Babban daki ta sallami kowa falon yarage daga ita sai shi yawuce wajenta yazauna yayi shiru, fuskanshi Gwaggo ta taba sannan takama hannunshi tabi da kallo tana dube dube tace “yaro jiki uwa na baturai kai kenan baka isa kaga kazanta ba” murmushi yayi ya fizge hannunshi yace “Gwaggo

ni na warke kidena dubamin jiki dan Allah” tsuki tayi tareda hankadeshi tace “kaga shashasha” Hararanshi tayi tace “ni shiga dakina ka dauko huran dana dama maka daga babanka sai kai kap cikin jikokina keson furana” jikinta yayi sanyi shima haka sai yayi shiru ganin yanda yayi yasa da sauri tai murmushi tace “bance kamin fuskan mara lafiya ba, Allah shiya bani babanku kuma shiya amsa Alhamdulillah d’ana yayi abubuwan alkhairi da dama aduniya yayi shukoki daban daban, ya gina makarantu, rijiyoyi, gonaki dan haka banda nadama Allah ubangiji yakai haske kanarinsa jeka dauko” tashi yayi ahankali yadauko kwaryan fura yazo yazauna yafarasha anatse tana kallonshi harga Allah itama zatazo Riyad yazama sarki cus yarone mai tausayi mara hayaniya ga kwarjini ga biyayya sannan ga kwazo, baida sa ido, shine yaro na farko kap yaran sarki daya fara neman nashi da kanshi, tun ana gulma ana cecekuce but marigayi yace abarshi yayi abinda yakeso dudda kalan kudi dayake dashi baitaba raina wani ko yadingaji yafi kowaba gashi da tausayi ya tsani yaga wani na fushi ko kunci sanadiyanshi dan haka itama Riyad ne zabinta daman tariga ta jefamai kuri’a. Ahankali tace “zabinka ne diyar Waziri ko zabin Mamanka Maryama dan nasanta da tsinannen taurinkai, dason saka kabi ra’ayinta sabida taba Allah ya yoka me biyayya, kaika zabi Haleematu”? Abu yaji ya tsayamai awuya but ya daure ya gyadama Gwaggo kai batare dayayi magana ba, Gwaggo tace “ai shikenan za’ai magana idan anyi bakwai na babanka muji, zanma Baffan ka Muji magana nama kirashi daman” daidai nan Munir yashigo yana zama akai sallama Mujitapha yashigo yana sanye da manyan kaya daya fito da katon teban daya ijiye sai kyalli shaddan jikinshi yake kana ganinshi kasan yasha kudi ya koshi waje ya samu ya zauna hakan yasa daga Munir har Riyad suka gaidashi atare. “Ina kwana Baffa” binsu yayi da kallo shikebin mahaifinsu yanason yaran wanshi baida matsala dasu, yanason ya gaji sarautan but then again idan baisamu ba no big deal idan any of yaran wanshi suka samu, adai dauko wani sarki ne daga cousins nasu da sauransu shine bazai yarda ba, anatse yace “kai yajiki? Kasami lafiya?” Gyadamai kai Riyad yayi Baffa yace “har yanzu ana kan investigation koma su waye sukai kokarin kasheka za’a kamasu, so don’t worry, it’s good zakai aure koda bakai maganan ba ma yana cikin plan dina nace kafito da mata you need to settle down shi lokaci baya jiran kowa mutuwa ake kullum” Munir ya kalla daketa sunnar dakai yace “kaikuma fa yaushe zaka fito da taka matar?” Dasauri Munir yadago kanshi saikuma ya nuna kanshi foolishly yace “Baffa ni” akufule Baffa yamai dakuwa yace “a’a ni” Gwaggo ta zubamai rankwashi tace “dan kaniyanka kaima kafito da mata akace” kabar da hannun Gwaggo yayi yana turo baki yakalli Baffa yace “toh Baffa zan fara nema daga yanzu” gyadamai kai Baffa yayi yace “kutashi kuje toh lemme speak to Mama” tashi sukayi suka fice daga dakin.

Direct dakin Mom yayi yana bude kofa Mom tace “get out Riyad” gaban kofan ya tsaya yace “sorry Mommy please Munir naje kirafa yarakani wajen Hajiya”

Cikin fushi Mom tace “tell me Riyad akwai abinda kataba so daban maka ba? You showed me duk cikin yan uwanka Munir kakeso dudda ban shiri da mahaifiyarsa but nabarka dashi but na gayamaka kadena zuwa side dinsu banso banso yare nake maka daka kasa fahimtata eh?” Ahankali yafara tafiya yakai inda take sai kawai ya rungumeta ashagwabe yace “I am sorry Mommyyyy bazan karaba kinga banda lafiya karki fushi dani please am missing Dad already abin zaimin yawa” shiruu tayi saikuma ahankali tace “okay nahakura but baka ba ita that woman is the reason har Babanku ya rasu baya shiri dani she come between ni da shi, allow me to plan your wedding and coronation in peace kaji” sakinta yayi sai kawai ya daura kanshi kan cinyanta ahankali yace “Mom kimin auren na yarda but please Mommy banson nazama sarki dan Allah I am too young to be Sarki, Mom I want to tour round the world with my wife in peace” cikeda fada tace “kaje sama da 58 countries wani tour round the world ne yarage bakayi ba? Is time kayi taking responsibility naka Riyad, you are royalty Riyad, kai Royal blood ne ba normal samari out there ba, duk wanda aka haifa a royal family akwai high possibility zai iya zama king so accept your calling, and Babana zai turo bodyguards dazasu dinga binka anywhere and everything” dasauri yatashi yace “Mom banso wlh banso” wani kalan kallo tamai tace “did you even know su waye da waye ke kokarin kashe ka?” Kallonta yayi yace “suwaye?” Tana kallonshi tace “I don’t know but my gut is telling me Yayanku from the way yake eye service dan he’s everywhere, da yarinyar nan bata cecekaba I don’t know what would’ve happened” dan ijiyan zuciya Mom tasauke cike da damuwa tace “kullum bana baccin dare sabida tunanin wasu out there are trying to kill my son” dan lumshe idanu Riyad yayi ahankali yace “Mom lemme see the footage” iPad dake gefenta agadon tadauka ta bashi daidai lokacin akai sallama yar aiki ta gayamata tai baki tashi tayi tawuce tafita shikuma ya kwanta ahankali kan gadon tareda playing footage din da aka samo daga airport din yana kallo kusan footage biyar ne daban daban tun na shigowan shi arrival hall dana elevator saina bayin wanda shine na ukun, tsare cleaner yarinyar da ido yayi, a lokacin da abin yafaru bai wani kalleta ba dan yana cikin tashin hankali sai yanzu yake kallonta on this footage dudda is not that clear video karkar dinnan but yanda ta turashi cikin sharan yakala da yanda tarufe da how she handled everything ahankali yace “who is this feisty gurl”? The way takebin music yake kallo, he was actually watching the footage to see kozai gane criminals din but yana fara kallo attention nashi kawai yadawo kan cleaner, har footage data kaishi wajen dumping shara yakala da yanda take tafiya sai kawai yayi pursing video tareda zooming face nata yace “who are you? You saved my life.”

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 5

Ahankali yake bude idanunshi kadan kadan sama sama yaji ance “Son” dudda idanunshi akulle but ahankali bakinshi ya furta. “Momm” shafa mai kai matan tayi ta duko ta manna mai kiss agoshi cikeda tsantsan so tace “gani nan yarona open yourself Riyad no one is gonna hurt you again” gently yake bude idanunshi kafin ahankali ya saukesu akanta gently ya yunkuro ya shige jikinta kaman dan karamin yaro yace “Mommm” bayanshi ta shafa tana murmushi tace “meya sameka what happen? Who did this to you”? Murya chan kasa yace “wasu mutane wanted to kill me….” Kankameshi tayi sosai tace “babu wanda ya isa ya cutarmin dakai ko yadauki rayuwanka as long as ina raye, u are safe already ana investigating abun sai inda karfina yakare” takara kankameshi kaman dan karamin yaro tace “I love you Riyad kaine kadai sanyi idanuwa na”lumshe idanu yayi saikuma ya yunkuro yatashi daga jikinta yakalleta da muryanshi da bata fita sosai yace “Baba”? Kallonshi tayi saikuma ta sauke dan ijiyan zuciya tace “tashi kaje kai wanka ka shirya kafito ka gaggaisa da mutane idan zaka iya, sannan kaje kama Babanka addu’a a makwancin sa” dan runtse idanu yayi abin yamai ciwo yaso Ya sallaci mahaifinshi, fuskanshi Mom ta taba hakan yasa yabude idanunshi dasukai ja yakalleta murmushi kadan tamai tace “nasan yanda kakeson mahaifinka but he’s in a better place yanzu trust me, all abinda yake bukata awajenka is addu’a, jekai wanka za’a kawo maka kayayyakin dazakasa” gyadamata kai yayi agajiye yace “Mom please ke kikawomin banson hayaniyan kowa” tsayawa tayi ta kalleshi ahankali tace “tom zan kawo maka da kaina” dagoshi tayi yatashi tsaye ahankali yawuce bayin dake nan bedroom din, girman bayin yayi girman wani gida, wanka yayi yayi brush yadaura towel yafito yana kallon saman gadon inda tundaga kan takalmi har zuwa kan agogo an jeramai akan gadon tsaf dazai saka wasu kayan sarauta ne masu kyau sunsha aiki, anatse yake komi ya shirya cikin kayan da aka musu aikin royalty ya feffesa turare yadan juya yakallo kanshi amadubi yayi wani irin kyau na ban mamaki hulan dayasa yasake maidashi wani cikakken mutum bude kofa yayi yafito daga bedroom din wasu bayi ne ma’aikata a falon suna ganinshi suka duka dukansu. “Takawanka lafiya Yarima Riyad, taho a sannu dan kwalisa abin begen Sarauniya Maryama, barka da fitowa, Allah yakara maka lafiya, makiyinka fadawanka, duk wanda yaja dakai ya shirya yasha kasa….” Wucewa yayi fuuuu yafita danshi bayason wayan nan surutun nasu, da Munir yaci karo yana kokarin shigowa flat dinsu hakan yasa ya tsaya yahade rai kaman suna fada Munir yace “katashi, are you feeling better can you walk”? Gyadama Munir kai yayi yay gaba kawai, Munir yabishi abaya direct inda aka binne sarki yayi yana zuwa ya shiga wajen batare da an hanashi ba yayi shiruuuuu idanunshi sukai ja, almost everyday indai Mai Martaba baida wani uzuri saiya kirashi da daddare yaji yayake ina kuma yake, kullum cikin fada yakemai daya daina yawon kasashe yakan yawan cemai yanda yake gudunma gidan nan da alamu shine wanda gidan nan zai rike kuma gam, ana cewa sarakuna basu da lokacin yaransu shidai mahaifinshi nada lokacinshi, Baba ya fara koyamai business how to make 1naira yakoma billions, Baba guides him through everything, duk business dazai fara saiya kira Baba, sai Baba ya amince zai farayi, kuma bai taba takura mishi ba, hawaye yaji sun taru a idanunshi da sauri ya runtse idanun yana fuzar da iska dan baiso suma zubo but

he’s deeply hurting, da ace yasan Baba zai rasu dabaiyi tafiyan nan ba, sosai yama mahaifinshi addu’a sannan yafito Munir yagani awajen da Kabeer dasu Shaibu yan uwanshi dukansu yajiki sukamai ya amsa sai kallonshi suke Kabeer yace “kasha magani kuwa you still look sick? Ko zaka koma ka kwanta ne”? Gyadamai kai yayi ahankali yace “nasha, I’m fine thank you” dannewa Kabeer yayi ganin yanda yakemai magana kaman alfarma yakemai dayake amsashi yadai daure yace “to mutafi fada” atare dukansu suka wuce fada, sauran yayyinsa da yan uwansa natamai hira da uhm a’a kawai yake amsasu cus gashinan ne kawai, gaida mutane sukayi sai yima Riyad gaisuwa ake ana kiran sunanshi shi baimasan ya akayi akasanshi hakaba dan baicika zama ba, su Waziri dai duk suna kallon komi, kowa yazo saiyamai gaisuwa amai yajiki, yanda ma ake kallonshi sai abin yasa yaji sabon zazzabi na nema ya lullubeshi.

Mom nazaune afalonta tana jan charbi ita dawasu kawayenta wanda suke mata Sarkin daga wasu garin dasuka kawo mata gaisuwa aka shigo flat din Matan Waziri ne da babban diyarta Haleema da ake kira da Lims, tana sanye da doguwan riga abaya black ta yana gyalen akanta, tanada tsayi da dan jiki kadan duka duka bazata wuce 24, 25 ba, tana shiga dasauri tawuce wajen Mom kafinma Mamanta tai gaisuwa tace “Mom ina kwana” takalli sauran matan wajen cikeda girmamawa tace “ina Kwanan ku” amsawa sukayi Mom tamata murmushi tace “Halima ba kina school ba yaushe kika dawo”? Mahaifiyarta tace “nima ganinta nayi agida da safen nan ta iso daga London wlh na aika driver yaje yakawota tunda taji rasuwan Mai Martaba hankalinta yakasa kwanciya” sosai Mom ke kallonta akunyace Haleema ta sunnar dakai Mom tace “school fa idan kikai missing exam ko test fa” Maman ta tace “project ma fa takeyi this month zasu gama komi da komi” babu wasa kan muryan Mom tace “kibi first available flight ki koma school gobe kinajina” gyadama Mom kai tayi ahankali tace “to Mom” Mom bata sake cewa komiba tacigaba da magana da manya, ahankali Haleema kebin dakin da kallo gabanta na faduwa addu’a take Allah yasa suhadu ta ganshi, Allah yakawoshi side din nan dudda tasan ba lallai yadawo ba barinma yaji da baki adakin amman tasan inhar yana gari yafi zama wajen Mom da bangarensu na samari.

Kallonta Mamanta tayi tace “tashi kije wajen su Batul mana” juyowa Mom tayi takalleta tace “tashi kije wajen yan uwanki” batai musu ba tashi tayi tawuce tafita Matan Madaki tabita da kallo tace “yarinyar akwai natsuwa ga kunya ga kawaici ta dace da Riyad sosai yanda shima baida maganan nan” wani kalan dadi Matan Waziri taji Mom tai dan murmushi batace komiba.

Ahankali take tafiya ita kadai tana danna wayanta kamshin turaren dataji yasa ta dago kanta dasauri Riyad tahango yafito daga fada yana shigowa nan compound din Mom wlh kusan duka yaran sarki tasansu da yaran yan uwa dan afadan nan aka

haifeta anan ta girma bata taba ganin yaro mai kyau da farin jini da aji irin Riyad ba kap gidan nan babu wanda yakaishi kyau, ga tsayi ga gayu ga jidakai ga miskilanci ga kudi kudinshi na kanshi bawai kudin Baban su ba dan babu wanda yakaishi kudi a yaran sarki, gashi Mai Martaba na sonshi, ga kakanshi na bangaren Mom Attorney General yafi kowa tsatso mai kyau da gata ayaran sarki.

Faduwa gabanta yayi sosai amman tadaure ta tsaya awajen jikinta har bari bari yake, tahowa yayi wajen batare daya kalle inda takeba zai wuce dasauri tace “Yarima Riyad!” Tsayawa Riyad yayi chak batare daya juyoba dasaurinta Halima taje ta gabanshi ta tsaya adan kunyace tace “ina yini ya hakuri?” Dan kallonta yayi trying to remember waye ita, shifa wasu kannin nashima ba saninsu yagamayi ba dan baya shiga lamarin gidan nan baison komi game da sarautan, dauke kanshi yayi ganin yanda take murmushi tana kallonshi, kaman ance dole yayi magana yace “who are you”? Wow the way he talks is super adorable, da kyar ta iya controlling zuciyanta dake neman fitowa ta danne kome takeji tace “Haleema” dan kallonta yayi irin kallon okay but still baigane ta ba and he doesn’t care din nan yajuya zai wuce dasauri tace “Ya Riyad sabida kai nazo gobe zan koma school” dan tsayawa yayi wannan karan yajuyo kalleta da kyau shifa har yanzu bai santaba and sabida shi tazo? Akan wani dalili? Are they related in anyway? Infact baida karfin bude baki ma yayi all this questions hakan yasa yadan tabe baki yace “thanks” kawai yawuce ya shiga flat din Mom……

Jin akwai baki abangaren Mom yasa yajuya yagazaya ta baya yashigo gidan yaje ya kwanta.

Yana zaune adakinshi dashi da Munir har yanzu bai gamajin sauki ba yana sanye dawani 3quater da singlet wayanshi yahau ringing kallon wayan yayi ganin Mom yasa yadauki wayan kai tsaye tace “kazo dakina ina son ganinka” ahankali yace “okay Mom” tashi yayi ahankali Munir dake taba wayanshi yace “ina zaka?” Slippers yashiga sawa yace “Moomm” yadauki wani farin t-shirt yasaka kawai yawuce Munir daya gane abinda yake nufi wato Mom nakiranshi hakan yasa yacigaba da abinda yakeyi ahankali yabude dakin Mom tana zaune kan couch din dake dakinta ganinshi yasa tanunamai gefenta tace “taho nan” shigowa yayi ya maida kofan dakin yarufe yataho wajen kujeran zama yayi saikuma ya kwanto yayi filo da cinyanta he’s really feeling mutuwan mahaifinshi so duk walwalanshi bayanan, hannunta Mom tadaura saman kanshi ta shafa tai shiru kafin tasauke ijiyan zuciya tace “kasha magani kuwa? Dr zai zo anjima” ahankali yace “nasha” dan ijiyan zuciya tasauke tace “da banson namaka maganan nan yanzu cus nasan kanajin mutuwan Babanka, I know

how much you love mahaifinku Riyad but I have to dan kowace matan sarki maganan da datake ma danta maza kenan, nima dole nama nawa” dan dago idanunshi yayi ya kalli Maman nashi baice komiba, ahankali tace “inaso kai aure Riyad!” dawani irin sauri Riyad yatashi zaune daga jikin ya kalleta yama kasa magana cus maganan yazo mishi ne bagatatan, Mom dake kallonshi itama looking damn serious tace “and bakowace kalan yarinya nakeso ka auromin ba Riyad, inaso ka auri yarinyar da zuciyana ta aminta da ita yarinyar da nice na zabeta, all yammatan zamanin nan yanzu burinsu is suyi aure su raba yaro da mahaifiyarshi I will never allow you marry such girls, I have a girl a mind dina gaskiya” haderai yayi kana ganin fuskanshi kasan bama yason maganan dasauri yace “Mom aure!”? Wani mugun kallo tamai tace “kaga Riyad banson shirme don’t even start all abinda kakeso kace, I supported you duk yawace yawacen dakake kana touring round the world bantaba hanaka ba dan nasan it’s your hubby, bantaba takuraka ba dudda normally normally ba tun yau yakamata kai auren ba, but yanzu lokaci yayi it’s an order you have to settle down, aure zakayi and i have a girl danakeso ka aura diyar Waziri Haleematu, ita nakeso ka aura!” Wani kalan tashi yayi dasauri yamike tsaye yana kallon Mamanshi da babu wasa akan fuskanta itama tabishi da kallo tazubamai idanu rass aka tace “kaine the most successful child acikin yaran sarki, you’ve archived alot Riyad at a very young age, ga ilimi kwali daban daban gareka, ga businesses da companies daka bude, ga natsuwa ga kamala ga kwarjini, naji kishen kishen dama mai Babban daki kaine zabinta sabida yanda mahaifinku ke sonka, Waziri shima nasan kodan yanda diyarshi ke sonka kuma yana mata kwadayinka kaizai dangwalamawa, to yaji maganan kuma kanason auren diyarshi komi yazo cikin sauki idan yana bangaren mu zai mana aikin yima sauran manyan fada maganan a zabeka, instead of su Kabir yan uwanka ko kannen babbanku dake neman kujeran sarautan, gwara kai dana kaikafi kowa chanchanta and bazan hutaba saina maidakai sarki, ai tsoron kada ka zama sarki yasa daga shigowanka garin suna neman halakamin kai amman Allah bai basu iko ba, kuma naji dadin abinda yafaru hakan yanunama jama’a cewa an tsaneka ana tsoron kada ka zama sarki saisa har anfara yunkurin kasheka, saisa saida na tabbatar kowa yasan abinda yasameka”.

□ SANYI DA ZAFI □

✍M SHAKUR

EPISODE 8

BAYAN 1YR!!

Cikeda natsuwa wasu manya manyan fadawa ke bude wani hamshakin kofa da girmanshi zaiyi girman wani karamin gate daidai karfe sha daya na safe, sannan dukansu suka fadi suka zube suna daga hannu irin yanda dai fadawa ke gaisuwa suka fara zuba kirari.

“Lafiya jakadan Baba Ali dan Baba Ali! Lafiya mai kiran gabas da yamma! Lafiya jinjirin wata sha kallo! Lafiya kwankwason jimina mai wuyar shafawa! Lafiya Garkami Wandon Karfe! Lafiya jijigen addini! Lafiya toya matsafa! Lafiya baya goya Marayu! Lafiya toron giwa! Lafiya tufaniyar gabas! Lafiya jinjirin wata shakallo! Taaaakawanka lafiya sarkin mu sarkin Riyad zakaran gwajin dafi mai hasken zuciya da hasken aura!, lafiya dan lellen Mai Babban daki.....”

Tunda suka fara kirarin nan kusan good 10min sai yanzu wani dogon mutum yafito yana sanye da wata milk kokuwar alkyabba dahar walkiya takeyi tsabagen kyanta ga rawani dawani white yadi mai kyau dake walkiya akamai, inda farare tarrr na idanunshi kake iya gani, hannunshi yarike wata sanda mai kyau, rabon da mutanen gari da yan fada suga fuskanshi shekara daya kenan, tun kafin yakaraso inda suke turarenshi yagama gauraye wajen da kamshin dadi dake dauke da yalwataccen ni’ima, ahankali yake tafiya kaman baiso yataka kasa, wani irin kwarjini shiganshi ke dauke dashi da bamaka iya kallonsa, har ya iso inda suke ya tsaya chak na kaman 5secs ya kallesu one by one to check idan kowa is healthy fine and present wanda hakan yana daga cikin abinda yasa jama’a ke sonshi, kaman baiso ya furta magana yace “kun tashi lpy”? Kaman jira suke. “Lapiyanmu kalau Sarkin mu mai adalaci, sannu sannu toron giwa tsintsiya madaurinki daya!” yanda jikinsu har rawa rawa yake sunamai kirari suna yabashi ya kalla sannan kawai yawuce duk suka biyoshi abaya, direct fada suka shige inda mutane suke cike makil wajen zama yayi ya zauna, batare daya hada ido da kowa ba this is mostly method dayayi adopting dayake samai natsuwa cus dazaran ya shigo fada he sees love hatred envy a idanun mutane da dama barinma yayanshi Kabeer, but koda wasa baitaba disrespecting yan uwanshi ba, and so far so good Kabeer din has been supportive bai bashi wani matsala ba haka ma yayyin babbanshi da Waziri ana koyamai komi everything is going smooth Alhamdulillah.

Munir sai kallonshi yake bayan yazauna, yadade baiga sarkin da mabiya keso kaman Riyad ba, anason Baban su but son da akema Riyad daban ne, har lakabi akamai da Sarki me farin jini, dudda akwai yan adawa but wlh ana sonshi barin yan cikin gari, cus kafin ma yazama sarki yana taimako sosai yasaka yara a school da dama, yanzu kawai dan he’s not happy about zama sarkin sai the whole abu yasa

he hardly talks, yakara miskilanci da wulakanci fiye da da, he’s so angry sabida he’s feeling kawai responsibility akasamai akai da baya so, responsibility daya tsaya and funny enough he’s doing so good da leadership din saisa har yanzu an kasa fadin wani negative abu akanshi ko kokafadi babu wanda zai yarda ma though yasan alot of people na jiransa to just make a mistake ne and he pray dan uwanshi will not make that mistake dasukeso suke kuma jira yayi.

Almost 2hr yayi afadan sannan aka tashi yakoma side nashi, bayan an bude katon kofan nan kaman gate still akwai tafiya kafin asalin babban gininshi, baya mulki like others, he hardly let anyone a side nashi, daga Muneer sai Mom da Haleema.

Shida Muneer suka jera fadawa na binsu abaya ana kaiwa gate din kowa ya tsaya dan babu bafaden dake shiga ciki ko matarshi bata isa tashigo side dinba without izininshi, sake bude another door sukayi that will lead them to compound din da interlock ya cika ko’ina ga bishiyan mango dake wajen da flowers ko’ina sai wata arniyan jeep bulletproof dake compound din gawani secret gate dayake wajen any private outing tanan yake fita.

Shiga mainflat din sukayi WAN’ı irin crazy sitting room ne dakeda fadi na bala’in yasha funitures that are very beautiful, zama Muneer yayi yadauki laptop dake kan table yace “almost 2yrs bake leka hotel ba Riyad, its only right kaje mana” wucewa sama yayi dan yaje ya cire kayan nan dasuka isheshi.

Binshi da kallo kawai yayi kafin ya shiga replying mails, kai tsaye aka shigo falon dasauri Muneer yadago kanshi dan mamakin waye ya isa yayi hakan ganin Mom tana sanye da wani alkyabba da akayi da crystal yasa yadan taso yace “ina yini Mo….” Baima karasa gaidataba tawuce stairs tai sama fuuu.

Riyad yariga yasaka wandon wani yadi brown da farin singlet ajikinshi yana kokarin saka rigan aka bude kofan bedroom nashi, dago kanshi yayi suka hada ido da Mom data haderai kana ganinta kasan ranta abace, dan lumshe idanu yayi yakarasa saka rigan Mom takaraso ciki har zuwa gabanshi dab dashi ta tsaya cikin tsananin bacinrai tace “yau kwanan ka nawa rabonka da shiga turakan Haleema Riyad”? Hannu yamika ya dauki agogo daga saman bed yana kokarin sawa yace “Mom kinsan I’ve been busy dealing with lot of things, my business, this sarki thing, everything ma” “and so?” Mom tai maganan da fushi tana daga murya tace “sabida business da sauransu bazaka kula matanka ba kusan 1months da 1week baka shiga gidan ta ba, and baka bari ta shigo nan ba, sai gulma ake tell me menene banbancinka da su Muneer da basu da mata”? Dan yatsine fuska yayi still baice

komiba yadauki links na hannun riganshi yana kokarin sawa Mom ta fizge links din cikeda masifa tace “Riyad wlh zan mugun sabamaka I hate this new attitude din naka, I’m talking to you baka kulani, ka shiga turakan Haleema koka kirata tazo nan your choice, people are watching and you know that, 1yr kenan kunyi aure ba ciki and it’s all thanks to you, ni bantaba ganin mai gudun mace har mace ba sai kai, badadan na tambaya tacemin kalau kake functioning ba dana fara tunanin kokai mace ce” sauke kanshi yayi kasa yayi shiru why will Mom be asking Haleema irin this kinds of question? Ahankali kanshi na kasa yace “kiyakuri Mom” cikin fushi tace “nayakuri nayakuri me? Get your wife pregnant nagayamaka dagayau nakaraji kun raba kwana” ta ijiye links din akan gado tajuya zata wuce hartakai wajen kofa zata fita ahankali yace “Mom” juyowa tayi tamai wani mugun kallo saikuma ahankali ta tako zuwa gabanshi ta tsaya tana kallon kwayan idanunshi, ahankali takai yatsanta tadaura kan kirjinshi cikin kakkausan murya tace “ni mahaifiyarka na umarceka dakai tarayya da matarka, make her pregnant within period na this sabon month da aka shiga, inba hakaba wlh saika gamu da fushina sosai Riyad” tajuya fuuuu tafice yadade tsaye ahaka idanunshi sunyi jaaa mode nashi ya chanza, he hates yanda Haleema tells Mom literally everything about marriage nasu, koma yace he hates yanda Mom ask everything akan aurensu, he hates both kawai, yana bala’in son sirri, he loves everything about shida matarshi nazama about them, anytime yakalli Haleema he doesn’t even feel like shine mijinta, he feel like Mom ne mijinta, kokarin saita muryanshi yayi yadauki wayanshi dake kan gadon, Munir yakira cikin muryanshi da bata fita sosai tsabagen bacin rai yace “ka aika akiramin Haleema pls” yana maganan ya katse wayan, tashi Munir kawai yayi yafice bayan yabada sakon yashiga mota yabar gidan cus yaji komi da Mom tafadi he just pity his brother, Mom is just over controlling Riyad, she’s in his matter, and baya iya cemata no, itakuma Haleema akanme zata dinga gayama Mamanshi komi gameda aurensu? Sabida taga baya iya tsallake maganan Mom ne, haba it’s annoying mana, Riyad dakeda kunya tagama fallasashi, it doesn’t matter koda Mamanshi ne some private mata barinma harkan auratayyan su baikamata Mom tama sani ba, the girl is sick wlh batasan menene boye sirrin mijinta ba, dashine matarshi tamai haka Allah he will deal with her, yayi tsaki aranshi.

Office yawuce abinshi inyaso yasameshi daga baya.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 9

Zaune take a arnen falonta takara kiba yanzu ba kaman da datake so skinny ba, tayi bulbul taciko alamun Riyad ya iya kiwo tasami kwanciyan hankali, wasu bayi ke

gyara mata farcen kafa jakadiya ta shigo zubewa tayi tace “Gimbiya Mai Martaba ya aiko akiraki chan bangaren sa” wani irin farin ciki daya lullubeta batasan sanda ta karbe kafanta ba ta mike da sauri tai sama bedroom nata ta shiga tana kiran wayan Mom awayanta kiran iPhone 15, ringing daya Mom ta daga Haleema tai wani ihu tace “Mom I love youuuu, you’re the best Mom, Mom wlh ina sonki sama da tawa Mamar ma, Mom dabanda ke da narasa gata, dana shiga uku, kinga Mom yanzun nan Mai Martaba ya aiko akirani kinmai magana ne?” Dan murmushi Mom tayi mai sauti kanta nawani swelling yanda Riyad baya tsallake dokanta, she just wish kowace uwa zatasami yaro mai taushin zuciya da jin maganan mahaifiyarshi irin Riyad kawai baya jure fushinta ko kadan ne, koyaya tace yayi abu kobayaso sai yayi, shi kawai baison commitment ne da nauyi akansa baison damuwa baison hayaniya but tace yayi kaza saiya yayine, murmushi tasakeyi tana wani ji da kanta tace “Madallah! sai a kimtsa aje, ki farantamai rai” gyadama Mom kai tayi cikin mugun farin cikin dan tana mahaukacin son Riyad tace “Mom banda kamarki me sharemin kukana, Mom thank you for making my husband to call me, bye Mom I love you” katse wayan tayi itakuma Haleeman cikeda jin dadi ta shiga shiryawa, tasha wasu magungunan da Jakadiya ke hada mata ta shiryata tsaf cikin wani hadadden atampa golden, ta daura Al kyabba akai ta feffesa turare sannan sauko kasa, Jakadiya da kuyanginta jaka biye da ita har zuwa side dinshi dayake da dan tazara tsakaninsu, tana zuwa dayake ansan da zuwanta aka barta ta shiga ciki Jakadiya da kuyangin kuma suka tsaya waje, shiga flat nashi tayi ko’ina na falon kamshin shi yake, murmushi tayi ta maida kofa tarufe sannan tacire Al Kyabban ta ijiye kan kujera tawuce sama tsayawa tayi gaban bedroom dinshi tai knocking.

Kusan 2min tayi wanda inda sabo ta saba jira haka duk sanda tai knocking, chan taji muryanshi ciki ciki cikeda isa yace “come…..in” bude kofan tayi gently ta maida kofan tarufe ta shiga dakin dakin tana tafiya ahankali sabida duhu gaske but tana iya ganinshi zaune bakin gado ya tsareta da idanu dake shinning even in the dark saida gabanta yafadi tadai daure ta maida takaraso zuwa gabanshi cikin yar kankanuwan murya dake cikeda yanga da iyayi tace “barka da warhaka Mai Martaba, kayi aike akirani gani” mikewa tsaye yayi yazuba mata ido, chan yace “how many times nagaya miki kidena kaima Mom maganata?” Faduwa gabanta yayi ta daure bata nunaba, cikeda makirci tace “ni kuma?akanme zankai karan mijina?” Wani kallo dayake mata yasa batasan lokaci da lips nata yashiga rawa ba, ganin yariga yagane ita tafadi tace “yes nagayama Mom baka zuwa wajena kuma ko nazo baka bari a barni na shigo? Kayakuri nayi kuskure bazan karaba, wlh bana iya bacci ne, narasa yanda zanyi dakaina” saikuma asanyaye tace “i need youu…” wani kallo ya mata yace “and sabida hakan saki hadani da Mom”? Ahankali tace “magananta kadai kakeji saisa nagayamata amman kaya kur…” bata karasa maganan ba yawani kalan hankadata kan gado dasauri ta juyo ganin yana bude mazariyan wando wlh har cikin ranta taji kaman tai ihun dadi tadai daure tai shiru

tana jiranshi, kafafunta yaja cikin fushi yace “you reported me sabida this I hope nabaki shikenan” ya kwashe skirt nata sama yadage rigan sama addu’a yayi yashiga ciki, runtse idanu Haleematu tayi tanaji kaman zata shide, wata daya babu abinda ya shiga tsakaninsu sai yau.

Almost 1 good hour yayi cur akanta not because of kanshi but her, ya sauke hakkinta daga kanshi tunda harta fara kai karanshi, saida yaji ta bushe ya tabbatar idan yacigaba zafi kawai zataji sannan ya kyaleta sannan yatashi zaune kafin chan yamike tsaye yawuce bayi ya barta kan gadon wani mugun bacci na daukanta tana numfashi haryau takasa gane kan Riyad, zai iya 2month bai nemeta ba yawanci saitasa Mom a case nasu yake nemanta and he’s so damn good in bed Innalillahi! The way he’s this quiet bazaka taba tunanin zai iyacin mace ba, but en anytime yayi having wani abu da ita jitake kaman she’s the luckiest gurl on earth, Riyad is good on bed, she don’t even know how to explain, yana wasa da jikinta wani kalan dirty play fa, yauma haushin abinda tayine yasa bai tattabata yanda ya sababa, wlh haryau takasa gane yanajin dadin ta ko bayajin dadinta oho ko gurnani bayayi bai tabayiba, he’s just super wired guy data kasa fassara halinshi haryau, and wiredness dinshi ke kara mata sonshi sosai aranta wlh, ahaka tana lumlumshe idanu bacci yayi awon gaba da ita.

**

Around 5 Mama ta tadata daga bacci, da kyar ta tadunma Mama, Mama tace “ke yarinya sai nauyin bacci kaman wani kato, tashi kin manta yau zaku koma makaranta eh? Hope kin dauki permission wajen aiki an baki shift na yamma”? Gyadama Mama kai tayi cikin gajiyan bacci, hannu Mama tasa tadagota ta taro kafadanta hakan yasa Rashida tasauke kanta akan kafadar Mama tana kara lumshe idanu still cikin bacci, dan jijjigata Mama tayi tace “Rashida” ahankali tabude idahunta tass takalli Mama dasu Mama tace “I think drop most of ayyukanki tunda kin koma school kinga yanzu year 5 kike you need to study well, nakosa naga diyata tazama likita, saura 1yr yanzu, Allah ya aramin rai, ranan super wax zan saka amin combination da super lace” dan murmushi kadan Rashida tayi tanason taji Mama na maganganu haka it makes her happy, Mama tace “yanzu dai kinga kina bukatan lokacin hutawa da lokacin karatu bakiga yanda kike gajiya ba da kyar kike tashi, ki saki sauran ayyukan ki rike na hotel din nan kadai tunda anfi biya, su Maman Miwa da sauran wajajen nan ki sakesu” dan murmushi tayi sai kawai tahau yunkurin tashi ahankali dan muryanta baya fita sosai sabida daga bacci ta tashi tace “Mama so kike na bar aiki sabida mudinga karban abincin sadakan da yan anguwan nan suke kawo mana out of pity?” Tadanyi shiru daidai takarasa mikewa tsayen batare data kalli Mama ba tace “this year is clinicals, zamuyi aiki a pediatric da

obstetrics&gynecology, I can manage everything Mama trust me, Alhamdulillah kome aka koyamin sau daya ya zauna akaina, sannan daga yanzu koda ranan Sunday ne zan dinga zuwa library duk sati sau daya nayi muraji'an duka abinda aka koya mana na that week, I can study Mama, I can do my duties na kula dake da siyamana kayan abinci da kudin magunguna, I can manage my work also" tana maganan tayaye labule tafita daga dakin tawuce waje saida tafara sa abinci awuta sannan tawuce bayi tayi wanka tafito lokacin har sanwan yayi tazuba taliya sannan takoma daki tashiga saka kaya Mama na zaune kan dadduma tana kallonta, tana kallon yanda taketa ciro kayan ghana masgon dasuke agoge daga gani kasan dan kaya mai kyau take nema na zuwa school abu Mama taji ya tsaya mata a wuya sai kuma ta daure kawai ta dauke kanta daga kallonta.

Wani doguwan rigan atampa maroon ta zaba ta maida gefe, taciro lab coat nata dayake a goge shima ta ijiye gefe sannan ta maida sauran kayan ta shirya tsaf tawuce tafita tasake juya taliyan sannan tadawo tasa hijabi ta kabbatar salla.

Tana idarwa bata tsaya yin azkar ba ta fita ta juyo taliyan a kula tasama Mama ruwan zafi na wanka sannan tadawo tasake zama kan dadduma tafara azkar tana gamawa ta kalli Mama dake kallonta tace "Good Morning Mama na nikadai, Mama naji dadi nikadai kika haifa nake moreki banda kanni dazaki dinga raba attention naki akanmu" most time tana maganan ne idan taga abu na damun Mama dan tasata tai murmushi, ganin Mama batai murmushi ba yasa takama hannunta tarike dasauri ahankali tace "Mamaaaaaaa" tai maganan ashagwabe tana lankwasa kai, ijiyan zuciya Mama ta sauke tace "babban burina arayuwa shine ki zama likita Rashida, banson wani abu dazai hanaki zama, kina bukatan lokacin dazaki karatu, banson ki fadi, banson ki sami carry over, nasan kinada kokari but dudda haka karatu yanada amfani, kina all this ayyuka bazaki sami lokacin yi ba, ki manta da kula dani Allah daya tsaga mana baki bazai hanamu abinda zamusa abakin ba, after this year next year zaki gama, please Rashida kibar ayyukan nan and focus a karatu" tunda Mama ke maganan take kallonta batason sata cikin damuwa hakan yasa tace "to naji Mama amman tunda kinga satın nan muka koma karatu da practicals bazasuyi serious ba kibari nayi aikin zuwa karshen wata abiyani kudina saina dena kinji, zancen night shift ai HOD mu tasan dani bata taba sani a night shift ba sabida ke Mama, so ko yanzu ma bazan bazanyi night shift ba, kinga na karbi albashina saimu ijiye, kuma Mama kidena damuwa yarki ta dauko brain dinki bazan fadiba In sha Allah bayan kinamin addu'a, to yanzu kin hakura na karasa zuwa karshen watan nan duk sai na saki aikin nabar na hotel din?" Shiru Mama tayi tana kallonta Rashida da taurin kai da kafiya hmm, ijiyan zuciya tasauke tace "okay! Yau sha uku ga wata, karshen wata zaki sallame kowa, next month banson ganinki kina zuwa ayyuka nan" gyadama Mama kai tayi tace "naji" tashi Mama tayi tace "ai shikenan" tawuce sip wani akwati zata dauko dasauri Rashida ta tashi tace "Mama stop ki kirani na dauko miki" dasauri tasa hannunta tadauki akwatin tasaukar dashi kasa Mama tazo wajen ta zauna itama Rashida ta zauna gaban box

din tana jiran tadauki abinda zata dauka tasake daukan akwatin ta maida sama, wata yar jaka Mama tadauko acıkın box din tamika mata tace “gashi ungo” dasauri Rashida ta kalli jakan data bata tace “na menene Mama”? Tasa hannu tana karba, zage zip din box din Mama tashigayi tace “naki ne kibude” da sauri taciro bakin ledan data gani cikin jakan dayake a kulle tashiga budewa saiga crocs a ledansu pink color mai kyau ba asalin designers one dinba but irin normal wanda ake saidawa a market yan 5k-7k dakuma stethoscope pink shima mai kyau, da mamaki take kallon kayan dakuma murmushi akan fuskanta tama kasa cewa komi Mama ta kalleta tace “bakiso ne oya bani kayana, last month danaje clinic wata Hajiya tarabamana kudi a envelop naduba naga 20k ne shine na shiga kasuwa na siya miki crocs naga shi likitoshi kesawa a clinic dimu duka likitocin wajen shine akafansu shine na shiga kasuwa na sayomiki ashe haka takalmin keda tsada dubu takwas aka saidamin na hada miki da wannan abun gwajin nace nima y’ata tai kaman yan gayun likitocin danake gani a clinic dinmu” hawaye ne yacika idanun Rashida tana kallon Mama na bata labarin Mama takare da “nazo naboyesu nace bazan baki ba sai ranan dazakuyi resuming school” daidai lokacin hawaye ya sauko daga idanunta Mama tace “ke mehaka kuka kikemin”? Kawai rungume Mama tayi da gudu ta kankameta ahankali tace “thank you Mama thank you” shafa bayanta Mama tayi tace “gabaki dayan rayuwanki Rashida nine na cinye miki ita, bakida lokacin kanki, komi kika samu ni, kome kikeyi sabida nine, konace ki sayawa kanki abu bakiyi saisa na saya miki kema ki shiga sahun yan gayu aga y’ata fess fess akara kallonta sabida yanda tai kyau, Allah yakawo miji na gari” cikin shagwaba ta ture Mama tace “ni bazanyi aure ba Mama, bazan taba iya barinki ba” baki Mama ta kama tace “ke kodai zan kaiki gidan zumane amiki rukiya kaman me aljanu bazaki aure ba” gyadama Mama kai tayi tadauki takalminta tana budewa daga leda tace “inhar ban samu mijin dazai yarda na daukeki muje gidanshi tareba ina ganinki ina baki kulawa wlh gara na kare rayuwana ahaka” da sauri Mama tamata dakuwa tace “kinci mai garinku Rashida” dariya Rashida tayi sosai tace “wlh Mama da gaske nake bazan taba rabuwa dake ba Allah Mama” ganin Mama zatai magana yasa ta tashi da sauri tace “bari nasa takalmina” fararen kafanta ta zura cikin crocs din sun mata bala’in kyau Mama tace “Masha Allah Tubarkallah komi kema yarinyana kyau wlh, kinga kafanki aciki kuwa dudda kafan fara ba lalli amman yayi kyau” wani juyi tayi cikin takalmin tace “Mama inason takalmin thank you so much Mamaa, bari na tafi” tawuce tasa doguwan rigan data fito dashi yakamata ya nuna her flat tummy sosai da very full chest nata cus she has boobs kaman Mama, itama Mama harda rama yasa ba’a ganin nata yanzu, dan kwali ta daura tayafa gyalenta tai arranging lab coat nata a bag pack da books da stethoscope da Mama ta siyamata da komi ciki ta goya abaya tasa yar wayanta a aljihun riganta da earpiece tace “natafi Mama” Mama tace “dan Allah kici abinci kinji kada ki manta” dasauri tace “to Mama zanci, bye Mama” Mama tace “ubangiji Allah bada za’a Allah ya taimaka Allah ya tsareki Allah yakuma baki miji nagari”.

Shagon Maman Miwa taje ta gayamata ta koma school da safe zata dinga zuwa aiki, nan da nan tayi wanke wanke ta share ko'ina tai mopping after 8 tagama komi Maman Miwa tabata 2k saikuma ta bata 200 tace "kihau adaidaita kitafi makaranta baki takaba" murmushi kadan tayi tace "nagode Maman Miwa" sannan tawuce tafito MamanMiwa tabita da kallo tace yarinya ga kyau har kyau ba miji.

Bucket na moping din tadauka da gudu tawuce bathroom na office din ta tara wani ruwa ta taho da sauri jikinta duk rawa yake zata fara mopping ruwan kunfan kasan jikinta duk yana tsiyaya kaman daga sama taji sassanyar muryanshi yace “stop!” Dasauri tadago manyan fararen idanunta ta kalleshi, hada ido tasakeyi dashi for the second time da sauri ta dauke kai aranta tace “sai shegen kallon mata mtsww” fitowa daga dakin yayi ahankali, cikeda tsantsan kulawa yace “step aside” dasauri ta matsa gefe ga mamakinta sai kawai taga ya tsugunna yadauki bucket na mop din ya matsar gefe da vacuum cleaner, yashiga nannade carpet din na tsakiyan office din yadaga yadauka yawuce wajen kofa yabude yafitar dashi ya ijiye bakin kofan nan yashigo yasameta tana kokari fara mopping wajen cikin kwantacciyan murya yace “go and change” dan kallon daga kasan riganta har zuwa crocs na kafanta tayi dake tsiyaya tace “karka damu I can do it banda wani uniform, zai bushe ai” yanda take kallon jikinta tana maganan yake kallo with her voice dake piercing kunnuwa sabida dadinsu, calmly yace “go take them off kisa kayan gida” kawai dan tasan office din mai hotel dinnan ne, sannan shita gani cikin offive din so dole tai assuming shine mai hotel din banda haka data gayamai me ruwanshi da yanda zatai aikinta yabarta tayi abinta tagama mana ha’a, sai gwadamata yanda zatayi yake, sai kawai tawuce kofa batare datace komiba tana zare handglove din, tabude

kofa tafita yabita da kallo kafin kawai yazaga yazauna kan kujeranshi na office yayi shiru.
Changing room dinsu tawuce ta chanza kayan tasaka doguwan rigan atampanta brown ne da milk just straight gown babu wani ado ajiki, dan kwalin kayan ta daura aka sannan ta zari gyalenta brown ta yafa daya kara haskata hasken fatanta yayi bau aciki, ta kwashi kayan bayinsu na staff ta shiga ta dauraye kayan ta wanke cinyanta da kafanta da takalmin tama wanke fuskanta kawai gaba daya hakan yasa tai wani haske mai kyau dinnan na bayan ka wanke fuska, tawuce baya ta shanya kayan sannan tafito tana tafiya da sauri sauri sabida tasamu tai sauran ayyukanta tabar office dinshi, tashiga elevator zuwa 5th floor tawuce office din kofan office din ta bude ahankali tashigo tunda ta bude office din ya kafamata ido, the first time daya ganta uniform ne jikinta, yauma haka yanzu ne yafara ganinta da kayan gida, kasa dauke idanunshi yayi akanta, ta taho direct cikin office din batare data kalli wajen dayake bama, zubamata idanu yayi yana kara tantancewa itace dai wannan mara kunyan ta airport, bai cika manta face ba idan yasan mutum, hade fuska tayi batacemai komiba dan jikinta yabata kallonta ake, tadauki moping stick din tafara moping wajen ahankali tana gamawa tadan juyo ta kalleshi karaf suka dake hada ido dauke kai tayi tace “zan iya shiga dakin na gyara”? “Yes” ya amsa calmly hakan yasa kwai ta shiga ta sharo tai arranging bed din dataga ba’a gyare ba, ta wanke bathroom din, kusan 5min tayi sannan tafito tawuce bayin nan office ta gyara shi in 3min sannan tafito tai arranging abubuwan datai amfani dasu tafita dasu waje sannan tadawo tazo gaban table dinshi tasa hannunta tana kwasan wayanta na wajen yanabin white long fingers dinta da kallo that looks so feminine, ahankali yace “wat is your name?” Batare data kalleshi ba tace “Rashida Almustapha” tana maganan tajuya dasauri zata wuce kaman daga sama yace “is your back hurting you naga kin fadi tabaya”? “No it’s not” tabashi amsa atakaice tacigaba da tafiya da sauri bataso yayi wani maganan kuma, hartakai kofa tasa hannu zata bude yace “Rasheedahhh!” Wlh batasan meya faru ba hakanan gabanta yafadi chak ta tsaya takasa motsi sabida yanda yakira sunanta, kawai she felt something strange in her dayasa dasauri tajuyo ta kalleshi sake hada ido tayi dashi saikuma ta dauke kai tace “na’am” kusan 30secs yayi shiru saichan ahankali yace “Thank You” Da sauri ta kalleshi zatace thank you for wat saikuma ta tuna maybe na gyaran ne hakan yasa ta gyadamai kai kawai tama kasa magana sabida yanda heart nata yafara racing tajuya tafito dasauri ta kwashi komi tawuce kasa ta maida komi store tawuce taje dakunan dazata chanza duvet nasu takai washing machine takai sannan tahau gyara Allah yasota bata hadu da Madam ba balle ta tambayeta ya akayi tasa kayan gida ba.

Wuraren 6 tafito daga hotel din sai fama take da wayanta dayaki kunnuwa sai cire battery tana maidawa take sabida ya kunnu yaki kunnuwa, ga jakanta goye abayanta. “Hi Rashy” Aisha receptionist dake night zuwanta kenan tai waving nata tana murmushi awkwardly tadaga hannunta saikuma ta maida ta gyada mata kai kawai tawuce tafito waje tana hure huren waya, Munir da Riyad na tsaye awaje

wannan karan ya chanza kaya zuwa jumper na milk yadi suna magan kaman daga sama ya hangota tafito tana hura wayanta, yanda hankalinshi da attention nashi yatafi wajenta saida Munir yajuya dasauri dan yaga meyake kallo haka ganin wacce yake kallo wacce kallo daya yamata she looks like worker nasu not guest yasa yace “who is she?” Batare daya dauke kanshi daga kallonta ba yace “my savior” dasauri Munir yadauke kanshi daga kallonta ya kalleshi dasauri yace “kaman ya your savior?” Yana kallonta yace “the girl that saved me from those goons a airport” dasauri Munir yajuya ya kalleta yace “wow the clearner damuka dade muna nema wat a small world ashe anan hotel namu take aiki, but did you tell her”? Girgixamai kai yayi daidai tasha kwanan layin yadauke kanshi yace “No bangayamata” Munir yace “why?” mota yashiga yace “bata ganeni ba” tada motan Munir yayi yace “ai da saika gayamata, How will you reward her yanzu?” Kai tsaye yace “I will ask her kome takeso arayuwa i will grant her any wish take da shi she’s part of the reason I’m alive today” murmushi Munir yayi yace “wat got you so angry today?” Yatsine fuska yayi yace “I don’t wanna talk about it” ahankali Munir yace “to mutafi gida? Mom tasa an sanar bakada lafiya just to manage situation din harda kiran Dr, tace na tabbatar mun dawo gida tare” hannunshi yasa yasauke glass na window ya lumshe idanu bai sake cewa komi ba, ganin baison magana yasa yace “azumi saura 7days fa bakai approving fund na kayan abincin daza’a rabama al umma da ma’aikatan ka ba” dan ijiyan zuciya yayi yace “i forgot bani file din da pen lemme sign” ahankali Munir yace “bari mukai i will

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 13

Gida tashiga around magrib agurguje tai alwala tashigo ciki Mama nakan dadduma hakan yasa ta tsaya kusada ita ta kabbatar sallan.

Tana idarwa cikeda damuwa tace “Mama ruwa yashiga wayana taki aiki wlh” tai maganan tana jawo jakanta taciro wayan cikeda damuwa itama Mama tace “garin yaya meya sameta?” Cikin damuwa tana kara huhhure wayan tace “faduwa nayi ruwa ya kwaromin shine ruwan yataba har wayan” dasauri Mama tasa hannu ta karbi wayan itama tana huhhura duk wani huji na wayan ta maida battery din kozata kunnu amman bata kunnu ba hakan yasa ta tashi tawuce chan wajen yan kayan abincinsu tabude ledan shinkafa tasa wayan ta zuba shinkafa akai tace “bari mugani kozata kunnu idan bata kunnu ba saina tattara kudin dake wajena kije ki sayo wata wayan dashi, kina bukatan waya kodan school, Allah kiyaye bakiji ciwo bako”? Gyadama Mama kai tayi tace “banji ciwo ba” Mama tace “to ai mun gode Allah tashi kiyo wanka kici abinci” dasauri tace “Mama girki kikayi”? Gyadamata kai

tayi tace “eh nayi shinkafa da wake da mai sa yaji” murmushi tayi tace “Mama banace ki dena girki ba” ture mata hanci Mama tayi tace “to banji maganan ki ba Anty Rashida” kwashewa da dariya tayi hakan bakaramin dadi yama Mama ba ganinta duk cikin damuwa sabida wayan tasan lissafi take ta yanda zata taba kudin saving dinsu tasai waya dashi kafin takara samin wani kudin fa, rashin lafiyan Mama fa, abinci fa, kudin wuta fa, tasan duk abinda take tunani kenan ganin tayi dariya yasa hankali ta ya kwanta, cikin shagwaba tace “kai Mama nine Anty Rashida” Mama ta kama haba tace “yooo ai hakane, Mama karki kaza, karki kaza, kullum command kike bani yarnan kinga ai kinzama Anty Rashidan” sake bushewa da dariya tayi kawai saita kwanto jikin Mama tace “Mama stoppp wlh ni ba Anty Rashida bane, Mama ina hanaki ne fa sabida karki fadi, kinga kinada yawan ganin jiri, kınada migraine kuma, Mama I have to take care of you gwara namiki komi ko ruwan dazakisha na ijiye kusa dake sabida karki wahala wajen daukowa” tabe baki Mama tayi tadagata daga jikinta tace “jeki wanka kizo kici abinci” tashi tayi ba musu ta rage kayan jikinta tadaura zani ta kwashe kayan da lab coat da kayan Mama data cire yau dasafe tafito saida ta fara wankesu tsaf ta shanya sannan tawuce bayi tai wanka tadawo Mama tabata abincin ci tayi bawani sosai ba batawani cin abinci abin yabi jikinta sannan takai kwanon waje ta kuskure baki ta dawo tahau salla kusa da Mama tana idarwa ta kwanta awajen ko 2min ba’ayiba tafara minshari Mama tai shiru tana kallonta sai kawai tasa hannu tadauki feet dinta ta daura kan cinyanta dudda uban tafiya akasa datakeyi bata da kaushi kafanta still looks very fine ga nails dinta farare kal masu kyau, ahankali take massaging kafafun ayanda ta gyara kwanciya kasan tanajin dadin tausan Mama is just looking at her babu salloli biyar dazatayi arana da zatakai goshinta kasa dabazatama Rashida addu’a ba, banda kiyamun Layli datakeyi kullum, kullum addu’an ta shine Allah yakawo ma diyarta karshen wahalan nan Rashida ita ke ciyar da ita, itace cinta shanta suturanta magungunanta da komi na rayuwan su Rashida ke nema, babu yanda zatayi ne dan batama da karfin aikin ne da itace zata fita ta nemawa diyarta abinci da komi ba diyarta tayi ba, kullum addu’an ta is Allah ya tsare yarinyar ya tsare imaninta kar wata rana tagaji da aikin wahalan nan tace zata shiga duniya tabi maza dan shine hanya mafi sauki da akebi asami kudi, addu’anta koda yaushe shine Allah yabata ikon kammala wannan karatun likitan, kowani shekara da hayya hayya take tara kudin school fees nata na last year bai musu wani wahala ba sabida tasami aikin hotel din nan ana biyan ta dubu 50k duk wata a nan ta tattara tabiya, fatanta shine Allah sa wannan shekaran na biyar kar kudin makarantan yayi yawa dubada yanda aka kakkara kudin makarantu, hawaye ta share ahankali daya zubo mata bata taba sanin dan Uwanta na jini zai iya juya mata bayaba sabida wannan cutan dudda da ranshi da lafiyanshi, bata da kowa sai Rashida, yau shekaru ashirin da uku kenan tana wannan wahalan tun Rashida na cikinta, ta haifo yarinya cikin wahala ta tashi cikin wahala sannan itama tana rayuwan wahala, batabama yarta komiba sai wahala, babu wanda ya yarda ya auri Rashida, ga yanda yar karaman yarinya ke aiki kaman namiji wata kalan uwace ita, hawaye ne suka kara zubo mata sai kawai ta jinginar da kanyon a bango takalli sama murya chan kasa that is very weak tace “Ya Allah idan mutuwata shine mafi

alkhairi agareni dakuma y’ata, idan mutuwata zai cireta daga cikin wahalan nan datake ciki Allah ka kasheni, ka aurar da Rashida gidan dazata huta, karufama Rashida asiri, ka lullubeta cikin nimarka Ya Allah.

Tadade ahaka yawanci tana boyema Rashida damuwanta da dama sabida kar yarinyar takasa karatu idan kanaso kaga Rashida ta birkice tarasa sukuni to Mama tace kaza namata ciwo tuni yarinyar zata rude, damuwa, tunani ga constant ciwon kai koda yaushe shiyafi damunta, saisa kullum tane asibiti BP ta is high, magungunan BP nema ke cinye musu kudi cus maganin HIV free ake bata a clinic dinsu.

Ganin yanda bacci ya shigeta yasa bata tadataba tabarta tai baccin anan kan dadduma.

Wuraren 5 Mama ta tadata da kyar ta tashi wanda hakan daman is daily battle nasu, gyaran gidan tayı tasa takai Mama tai wanka tai salla tazo ta dumama shinkafa da waken sannan tama Mama tuwo sunada miya daman kafin ta shirya cikin bakin abaya da stones nashi yagama fita tass but dudda haka ya mugun mata kyau abunka da fara tazo taje wajen wayanta taciro daga shinkafan tasa battery ta kunna amman still yaki kawowa Mama tace “bai kawo ba?” Gyadama Mama Kai tayi ahankali, dasauri Mama tazo karban wayan tayi tace “kodai ba chaji ne” tawuce wajen chazanta dake bango ta makala kusan 3min bai dauka ba, ahankali Mama ta tashi tace “bari nabaki dubu talatin din nan saiki sayo wata wayan kawai” dasauri tace “a’a Mama ki adana talatin din nan, bari zan kaita wajen yan waya a gyaramin zasu iya gyaramin” badan Mama taso ba dan wayan tariga tagama tsufa dukta farfashe tace “to shikenan bari na baki kudin gyaran” sip tabude taciro wani leda ta kirgo 5k tabata karba tayi sannan tayafa gyalenta tace “bye Mama” har zaure Mama tarakota tace “adawo lpy” dayake 9 ake fara clinic dinsu hakan yasa taje shagon Maman kuwa tayi aiki ta karbi 2k dinta sannan tawuce shan wajen gyara takai wayan ganin zai dauki lokaci tace “zata dawo da yamma” tashiga keke sai hospital nasu.

she’s not really doing much a consulting room take zama attached to consultant din da aka assigning nata to him yana duba yara marasa lafiya yana tambayanta me aganinta take tunanin is diagnosis din tafadi, kokuma yace wani investigation yakamata ayima yaron tafado sunayen series of test da za’ayi ganin how brilliant d girl is tsohon likitan yace “i will comfortably leave the office for you tommorow” gyadamai kai tayi dan she hardly smile outside, haka dai tagama by 1 tawuce mosque tai salla ta linke labcoat tasa a bag sannan tafito tashiga keke sai hotel.

Yau tadanyi latti sabida traffic sai around 2:30 tashigo hotel din ko kallon mutanen dake reception da lobby gabaki daya batayi ba da sauri sauri tawuce changing room nasu kofa tabude ahankali, ma’aikatan su tagani gudu uku a lobby suna chanza kaya da kallo suka bita batace musu kala ba tawuce locker dinta tasa password dinta tabude, daya daga cikinsu ne taja tsaki tace “mutum sai fadin dai, nagadai da mutum dan wani ne dabaizo hotel neman aikin shara da wanke bayi ba, tundadai duk ansan juna menene na jijji dakai kaman diyar wasu” ? Sauran biyun ne suka kwashe da dariya daya tace “dadine dake Hussy baki hadiye abu aciki” parking gashinta tashiga yi da ribbon tace “eh mana kullum fuskan mutum amurtuke ana fadin rai ana daga shoulder kaman yar shugaban kasa amman shine akazo aikin wanke bayi a hotel” wani irin buga marfin locker Rashida tayi saida yayi kara pammm!Tajuyo tai facing Hussy direct cikin zafin rai tace “dani kike maganganun nan?” Wani banzan shakiyin kallo Hussy tamata dan tadade tanajin haushin Rashida wai ace ma’aikata nawa a hotel din nan yarinya bata kula kowa, kuma kai kasauke kanka ka kulata taki kulaka back, bama wannan yafi bata mata rai ba yanda take nuna bamatasan anyi hallita irinsu a wajen ba ko ka kulata ita bazata kulakaba sai bakin taurin kai, jibidai yanzu datazo tasamesu ko Hi bazata iya gayamusu ba? Amman basu isheta kallo ba, cikeda tsana tace “naga dai ban kira suna ba, amman duk wanda ya tsargu dashi nake” wani irin kallo Rashida tamata kaman taci ubanta saikuma ta tuna nan wajen aikin tane, da kudin aikin wajen nan zata biya school fees and other things bari kawai ta barta today is her lucky day, sai kawai tajuya tasa hannu zata dauki uniform nata batare data kara magana ba, cikeda neman fada Hussy tai wani shewa tace “jakan ta tsorata” juyowa Rashida tayi da mugun zafin rai batai wata wata ba ta fizgo gaban rigan Hussy ta kifa mata mari a fuska ihu jikake tasss! Hussy tayi ihu ta chakume gaban rigan Rashida tace ni kika mara”? Sai dambe, dukanta Rashida take bana wasaba har gyalenta na fadi kasa bakin gashinta datai parking donut mai bala’in kyau ya bayyana, sauran yammatan biyu na kallo sunajin dadi ganin suna dakan juna dudda Rashida nacin uban Hussy amman kallon fada da dadi yake sukaki rabasu, ganin jini Rashida tafasa bakin Hussy yasa daya cikinsu ta tsorata tace “baruwana kar ayi kisan kai agabana” dasauri tabude kofa tafita da gudu dayan ma tabiyota hango Madam sukayi a lobby tana magana da receptionist kafin sukai wajen ma sukai ihu. “Madam ana fada” daidai lokacin Munir da Riyad na shigowa yana shaye da brown jumper yasa brown shade a idanunshi na CK dayamai kyau sosai, arude dayan tace “Ma come oo harda blood everywhere!” ganin Riyad yasa Madam tace “Sir welcome wai ana fada I don’t even know with who lemme handle it” tawuce jin yasa Munir yace “let’s intervene” Munir yayi gaba Riyad yabiyosu abaya yana tafiya one one a kasaitance, da gudu Madam ta shiga dakin tai ihu “what is this”? Ganin blood har wuyan Hussy, Rashida bama tasan an shigo bama Munir yashigo dakin daidai Riyad na isowa chak ya tsaya wajen kofan batare daya shigo ciki ba yana kallon su, jan Rashida Madam ta shigayi da karfi gaske ganin yanda take dukan Hussy, sauran yan aikin suna banbare hannunta daga jikin Hussy sunajan Hussy da bakinta yayi jina jina da jini harda hanci baya suka kwasheta da kyar daga hannun Rashida, Madam data rike Rashida

cikin tsananin bacin rai tace “fighting awajen aiki are you too Mad? Rashida wat is this why did you beat her up like this?” Itafa idan tana fushi bata gane kowa, kabar da hannun Madam tayi daga jikinta a haukace kaman ba Rashida ba cus ranta yabaci tace “dalla sakeni kekuma Malama” tajuya zata closet nata cikeda taurin kai duka ma’aikatan har Munir saida yakalli Rashida yasake kara kallonta jin abinda ta gayama Madam, Hussy dake haki an riketa tace “Ma kinga halinta ko saisa all worker ke cemata psycho, kolomental ce wlh, mahaukaciya ce very weird girl, shegiya yar shaye shaye, an gayamiki bamusan asalinki bane, uwarta nada HIV!” Chak Rashida dake tafiya ta tsaya kaman kankara, ihu Hussy tayi ganin ta tsaya chak da tafiyan datakeyi that means maganan ya shigeta tace “ai duk munsan sirrin ta Ma, harnan akazo tundaga layinsu aka gayamana we should be careful with her tanada HIV Mamanta ma nadashi, bamu gayamiki ba Madam sabida karki koreta cus munsan she needs this job for her virus drugs da Mamanta, amman shine zata kama dukana ba ban mata komiba bayan tanada wacce tafi chanchanta adaka islamically agida, diyar fasika kawai!” Wani irin juyowa da Rashida tayi zaka dauka zakanya ce ta taho da gudu tareta Madam tayi tace “where do you think you’re going” wani irin hankada Madam Rashida tayi saida Munir yatare Madan da sauri dan inda tafadi wlh saita karye, Hussy na ganin haka ta wuce da gudu tabi gefen Riyad ta gudu tafice da gudu Rashida ta taho itama tsabagen fushi ko ganin gabanta batayi ahankali Riyad yadaga kafanshi yashigo ya tare kofan yayi blocking nata, hakan yasa ta dago jajayen idanunta takalleshi adake cikin tsananin fushi da zuciya tace “ka tashin mini daga hanya” Madam da Munir ya daga kyar tace “it seems da gaske yarinyar nan is mad, call security namu and call the police” yana kallonta ta glass batare daya dauke idanunshi daga kallonta ba yace “don’t call anybody” cikin kumfan zuciya kaman zata fashe tai wani irin ihu tace “nace ka tashinmini daga hanya” strictly yace “you’re not going anywhere!” Wlh ayanda zuciya ke daukanta kaman ta dagashi ta yar takeji kawai tasan batada karfin ne, yanda hannayenta ke rawa da jikinta yasa kawai ta juya fuuuu tawuce dan bence din dake wajen ta zauna tai folding hands dinta akirji duk yan dakin kallonta suke she’s shaking, sai alokacin yakalli Munir yace “get first aid box go and attend to that girl, yakalli Madam da sauran yar aikin dake kallon Rashida da mamaki kaman yau suka fara ganinta yace “ku wuce kutafi” cikeda mamaki Madam tana kallonta tace “this is your last day here” duk wucewa sukayi suka fita yarage Riyad kadai dake tsaye awajen kofan dan kwalinta dake kasan dakin ya kalla ahankali ya shigo ya duka gently yadauka dusting nashi yayi sannan yataho inda take zaune kanta akasa tayi folding hands a kirji ahankali ya yafa gyalen akanta.

Dago kanta tayi tazubamai jajayen rinannun idanunta yanda yara masu taurin kan nan sukeyi tace “ina ruwanka dani? Wayace katabamin gyale na? Wat is your business with me? Nabar aikin naku dagayau nima, bazan kara aiki inda wata ta kira Mamana…….” Saita kasa karasa maganan sabida yanda abin ya tsayamata awuya saikawai tajuya mai baya da sauri takai hannunta ta sharce hawayen daya soma zubomata, data sharce da wani yasake zubowa sunki tsayawa yakai almost 1min

yana kallonta sannan yajuya ahankali yafice tareda maida kofan yarufe kaman jira take fashewa tayi da kuka haryafara tafiya yajuyo sautin kukanta chak ya tsaya har shesheka takeyi yakai kusan 1min ahaka sannan yabar wajen, kusan 5min tayi tana kuka sannan ta goge fuskanta tass ta tashi tawuce drawer ta ta shiga kwashe yan small small tarakacen datake dashi awajen uniform nasu tabar musu sannan ta goya jakan abaya ta tsaya takara goge fuskanta tass bazaka gane tai kuka ba unless u look into her eyes tafito sai kallonta ake a reception amman ko kallonsu batayiba ta wuce tafita ta tafiyanta gida.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 15

Da gangan Munir yabar wayanshi awajen yadauke car key yafice, tashi Riyad yayi yawuce yasaka pajamas yadawo ya kishingida tareda lumshe idanu, wayan Muneer ne yahau ringing hakan yasa yabude idanu kadan yakalli screen din ganin Mom R yasa yayi shiru yana kallo wayan na dab da katse wa yasa hannu ya dauka yakai kunnenshi yaki magana daga ta dayan bangaren Mom tace “Son” ahankali yace “Mom ina yini” ijiyan zuciya Mom ta sauke she really miss him chan tace “sabida I questioned you zakai zuciya kabar gidan? Riyad when did you grow dahar zakabar min gida sabida namaka fada? Riyad I still see you as my little baby boy da I have to guide every step of the way, your are my purpose, you are the reason I become a Mom, did you really leave house yau kwana biyu sabida na tambayeka game da abu Riyad”? Mom tai maganan muryanta na tsinkewa kaman zatai kuka, Riyad yayi shiru Mom abin ya matukar bata mata rai tace “ko kakai 100yrs of being a man I will always see you as my little child, I will always tell you do this and that, I agree raina abace yake ranan datamin maganan dan kunnen nan and I wasn’t thinking clearly, but still inada right nai fada, Babanka yayi aure aure but tell me menene fa’idan hakan yanzu? Kullum gidanshi cikin rikici makirci da fada ake, kalli Baffan ka tunda yama Amaryanshi koran kare bai sake marmarin kara aure ba sabida yaga implications din gashinan shida Jummai are living peacefully and happily, wat I’m saying is mata dayawa masifa ne, bazan taba bari ka auro wata wacce ban sani ba ko ban aminta da ita kaman Haleematu ba kafin azo arabani da d’ana that is the reason namaka fada and asked you ranan, and gashi nakosa naga Haleematu tai ciki amman shiru, dakaina nakai yarinyar taga gynecologist ance she’s fine kaine dai baka cika nemanta ba, kuma ita Haleematun tagayamin yawanci koka nemeta ba rannan ovulation dinta bane saisa har yanzu batai ciki ba, mesa kakemin haka Riyad? Kai ba dan gidan nan bane bakaga yanda matan yayyinka ke haihuwa

shekara shekara ba? Duk shirin da Babanku yakema yaranshi maza tun suna yara kaima an maka amman narasa mesa kakeda sanyi a harkan raya sunna" da sauri Riyad yacire wayan daga kunnenshi yanajin wani irin kunya da nauyi idan Mom namai irin maganganun nan, danna wayan kawai yayi a speaker ya ijiye agefense yana jinta. "Kap yaran family nan wlh basama matansu wasa kai har rama matan suke sabida yanda yaran Mai Martaba Baba Ali fire for fire ne akan matansu" wannan karan Riyad baisan sanda ya dafe kanshi yace "Mom can we change the topic please" cikeda bacin rai Mom tace "Kaci gidanku da change of topic Riyad, nabaka gobe come back home and continue kaga yanzu kayi skipping 2days babu abinda ya shiga tsakaninka da Haleema, kubani grandson nagaya maka saida safe" ta kashe wayan, ijiyan zuciya ya sauke yakoma ya kwanta tareda lumshe idanunshi.

Har Muneer yadawo a kwance yasameshi yace "ina tuki natuna wani abu daya faru dazu yanda dayar ma'aikaciyar yarinyar tace ma Masifaffiyar mamanta nada HIV" dagokai Riyad yayi yamai wani shegen kallo yace "and so"? Dan sosa kai Muneer yayi yace "bakomi kawai natuna abin ne" juyar da kansa yayi sai chan yace "HIV is just like any other ciwo, having it doesn't mean you are bad ko karshenka yazo, stop with the stigmatization" dasauri Muneer yace "haba noo bana stigmatization sai kace Baffan mu da akace ya kori matarshi mai ciki da akace tanada shi, ko tana ina oho"? Tashi Riyad yayi yace "let's eat" abinci suka shiga ci he ate alot kam yana gamawa yadauki laptop yafara aiki daman yunwa yahanashi yi.

Cikin bacci taji ana tabamata kai sabida tsabagen yanda bacci yau bai shigeta ba taba cikin tashin hankali firgigit ta farka.

Cikin dare sau biyu cikin dare Dr da Nurses sukazo duba Mama duk tana zaune bata runtsa ba harsaida Dr yace "kihau gado ki kwanta kusada ita mana ko ga babban sofa kihau" girgizamai kai tayi tana zaune kan yar kujeran dake gaban gadon, cikin sanyin murya tace "zan zauna anan" gyadamata kan Dr yayi yawuce harzai fita tace "ina bill dinmu?" Dan juyowa yayi yace "your bill has been cleared receipt duk suna cikin ledan drip dinta" yana maganan yabude kofa yafice from yanayin mutanen kawai yasan Mai Martaba taimakonsu yake.

Tashi tayi dasauri tawuce wajen ledan drip din da duk za'a sama Mama tabude taciro takardun receipt wanda na farkon na meal tagani 2 person breakfast 2person lunch dinner da snacks na 3days taga 270k, abincinta itada Mama kullum 30k for 3days 270k zaro idanu tayi takai hannunta tana dafa kirjinta, tadauki dayan receipt din single room dasuke dakeda gado sofa fridge da bayi is 25k per day kwana uku 75000, sai magungunan Mama gabaki daya da drip da allurai taga 497,250 wannan karan saida ta fada kujera ta zauna, duka kudin 842,250naira, kusan miliyan daya ta ina zata fara neman kudaded nan? No gobe zatasa a sallamesu, but ko an sallamesu sunyi kwana daya which is 25k daki, sai kudin magunguna 497,250 dole saita biya ta ina zata fara, hawaye taji sun zubomata sai kawai ta gogesu da sauri

tahada duka receipt din ta linke tasa a jakanta tadauko kudinsu ta kara kirgawa duka savings dinsu kenan 150k tadade ahaka saita maida jaka ta kama hannun Mama ta rike har aka kira asubahi idanunta biyu tashi tayi tawuce bayi tayo alwala tafito tabude jaka ta ciro dadduma anyi alamun gabas aşaman dakin hakan yasa ta kabbarta salla ta idar tai azkar tana zaune kan dadduma Dr yakara shigowa dasauri ta tashi ta linke dadduma Dr yaduba Mama yajuyo yakalli Rashida datai zuru zuru yace “Alhamdulillah BP yasoma sauka, maganin zai saketa soon zata farka bada jimawa ba” gyadamai kai tayi, murmushi Dr yayi yace “Maman ki will be fine kinji” gyadamai kai tayi ahankali tace “thank you” wucewa yayi yafita

Zama tayi har bakwai da rabi kallon Mama take sai alokacin tafara hamma sai kawai ta kifa kanta anan bakin gado ko 1min batayiba bacci yayi awon gaba da ita.

Wajajen 10 na safiya Mama ke bude idanunta ahankali bakinta dauke da kiran sunan Allah, saman dakin ta kalla sannan ta sauko da idanuwanta ta kalli drip da ake samata kafin ta sauke idanun kan Rashida dake zaune kan kujera ta kwantar da kanta bakin gadon kusada hannunta tana bacci, ijiyan zuciya ta sauke ahankali komi daya faru jiya na dawo mata, ta tuna yanda tagama magana da bawan Allah nan mai kirki tafara tafiya tafadi tabbas taga bawan Allahn hankali tashe yazo yana kiranta Mama Mama dishi dishi take gani bama ta iya magana dağa baya kuma taga shida security sun kaita mota daganan kuma bata sake sannin inda kanta yake ba, ahankali cikeda karfin hali irin nata ta cire drip din ta sauka tana tafiya da kyar tawuce kofan data gani ta bude ta shiga bayi ta dauro Alwala tafito ta sanya hijabi taje ta sauna kan dadduman data gani tai salla dağa zaunen datake tun magrib da isha’i tahada dana safiya sannan ta dawo ta lallabo ta zauna agadon jin jiri na neman yakara dibanta motsin da gadon yayi yasa firgigit Rashida ta bude idanunta ganin Mama zaune da hijab dinta yasa da sauri ta tashi tace “Mama kincire drip din” takama hannun Mama dasauri tashiga maida mata drip din tace “mesa baki tasheni ba har yanzu BP ki is high Mama, you can fall at any moment”

Yanda take maganan Mama take kallo kaman ba Rashida ba duk ta tsure harta rame idanunta sun fada ciki sosai, hannunta Mama takai ahankali ta kama habarta hakan yasa gently tadago fuskanta ta kalli Mama duk yanda taso taboye damuwanta takasa da duka zuciyanta tafashe da kuka sosai atsaye hawayen na sauka kan hannun Mama, cikin kuka tace “Mama dan Allah kiyakuri I keep causing you pain koda yaushe, Mama I know how sick you are but kullum kara miki damuwa nake Mama, akan mene bazanyi hakuri na dinga danne komi ba, komine sainayi fada akai, is because of me BP ki yatashi, Mama kiyakuri kiyafemin dan Allah” har sheshekan kuka take, zuwanshi kenan yakai hannu kenan zai knocking kofan yaji sautin kuka da maganan datake hakan yasa ya tsaya chak.

Ahankali Mama ta girgiza mata kai tace “shiiiiii don’t ever blame kanki for ciwo ba cus ba laifinki bane ko daya, stop crying to bagani nan naji sauki ba, gashi nan duk kin bata fuskanki jibi yanda idanuwanki sukai ja sabida kuka bari kiga” Mama sai kawai takama bakin hijabinta takai kan fuskanta tashiga sharemata ta shafa kumatunta tasake murmushi tace “I have the most beautiful yarinya wlh idan tai kuka sainaga idanun nata ma sunfi kyau” dan murmushi kadan tayi wasu hawayen na taruwa, Mama tace “ai kaga abin karki kukan ya isa nace, yanzu dai tafi gida ki shirya kitafi school idan zaki dawo saiki biya wajen gyaran wayanki” baki Rashida tabude zatai magana akai knocking kofar just once kallon kofan sukayi dukansu, Mama tace “jeki bude kofan muga ko likita ne natafi gida” but Dr direct yake bude kofan tai maganan aranta tasa hannu ta goge fuskanta tass sannan tawuce wajen kofan tasa hannu ta bude ido da ido tayi da Riyad dake sanye cikin wata shadda yau sky blue jumper kanshi ba hula tashin Kansa ya kwanta sidik tunda take bata tabajin kamshin turare mai dadin nashi ba, da sauri ta dauke kanta dağa kallonshi Mama hangoshi yasa tace “bismillah bawan Allah” anatse akamilance yashigo har gaban gadon yaje yaduka dasauri Mama tace “tashi tashi haba zauna ga waje” tabashi kujera ijiye ledan dake hannunshi yayına gefen gadon yace “ya karfin jiki Mama ina kwana” murmushi Mama tayi tace “jiki Alhamdulillah naji sauki, nagode da kulawa ka kawoni asibiti banda bakin maka godiya Allah maka Albarka” takalli Rashida dake tsaye wajen kofan tai folding hannu tace “baki iya gaisuwa bane ko akwai abu abakinki ne” dan juyawa tayi da kyar tace “ina kwana” baki Mama tasaki tana kallonta ganin baka yasa da kyar tace “mungode” dasauri Mama takalleshi tace “Ya sunanka ne?” Ahankali yace “Riyad sunana” daidai lokacin akai knocking tareda shigowa dakin wata ce tana sanye da uniform na ma’aikata tace “good morning Ma dazu nazo nakawo muku breakfast naga kuna bacci natafi dashi dan karyayi sanyi yanzu zanje nakawo muku” tawuce tafita daga wajen kofan akunbure Rashida tace “Mama kicemai yasa a sallamemu mutafi asibitin mu” dan juyowa yayi daga inda

Yake yazuba mata ido dauke kai tayi strictly yace “Dr yace 3days Mama zatayi anan and hakan ne zai faru” dasauri Mama tace “Riyad kaga ai dawainiyan zaiyi yawa ta ina zamu sami kudin biyanka? Dan Allah kasa asallamemu naje general dana saba zuwa kaji, Allah yamaka Albarka Allah yakara daukaka” daidai lokacin aka kawo abincin breakfast ne omlete da bread toast sausage tea dakuma bowl na fruits yarinyar ta saukar dama da Mama wajen ijiye abinci kan gado sannan takai dayan abincin kan table sannan takalli Riyad tace “Sir do you need anything”? “No thanks” yafadi atakaice, Mama ta kalli Rashida dake tsaye kikam har lokacin awajen kaman mai gadi tace “zokiyi kari kitafi school don’t even tell me bazaki ba” kaman zatai kuka tace “Mama ni banso naje wazai zauna dake natafi” “I will be here with Mama” dağa Mama har Rashida dukansu kallon Riyad sukayi, hakanan Mama kawai taji tanason natsuwan yaron, abin yana mata ma kaman tasanshi batason tai rubbing in

his face hakan yasa tai murmushi tace “to kinji Riyad zai zauna yatayani hira zoki ci abinci kitafi school kinyi katti already banson kina fashi a school kije gida ki shirya kitafi” bataso taje school ba but abinda yafima damunta is wannan mutumin dayakeyi kaman irin ya sansu din nan ko su yan uwa ne saiwani shishigi yaje musu mutumin da shekaran jiya ta sanshi, batason tai gardama sabida Mama batada lafiya hakan yasa ta taho wajen gadon gefen Riyad ta ballama jakan abubuwan dayakawo harara karaf akan idanunshi sannan tadauki jakanta dake wajen ta taso tajuyo hada ido sukayi tadauke kanta tajuya Mama tace “abincin fa” akufule tace “ni bazan ci ba” tawuce wajen wardrobe na dakin taciro kayan jakan an Mama daya kawo ta maidasu ciki kudin taboye karkashin kayan sannan tawuce tai hanyar kofa tace “natafi” tabude kofan tafice ijiyan zuciya Mama tasauke tasa cokali ta a abinci tace “I have a very stubborn yarinya Riyad” dan murmushi kadan Riyad yayi baice komiba, Mama tai shiru kaman mai tunani tace “she’s all abinda na mallaka aduniyan nan” saita dauki fruits takai bakinta tafara taunawa sai kawai tafashe da kuka as if she’s holding on to something ahankali Riyad yace “Mama stop crying she will stop being stubborn soon duk yarinta ne, zata dena nan gaba, stop crying kinji Mama is not good for you zai hanaki warkewa” ijiye spoon din tayi takai bakin hijabinta ta goge fuskanta tace “ciwo na bana warkewa bane, HIV gareni Riyad” tadanyi murmushi tace “I don’t even know why nake fadamaka nasan kariga kasani Rashida tacemin agabanku abokiyar aikinta tace inada shi” tai shiru sai kuma ta zufar da iska dağa bakinta tace “I’ve caused Rashida pain tun tana ciki na, yarinyar nan tayi girma cikin bullying din society yar fasika yar mazinaciya yar me HIV so sometimes I don’t even blame masifa da fadan da stubbornness nata society shaped her to be that way dole tai finding means na yanda zatai surviving.

Mama takara shiru saikuma tasa hannu tadauki bowl din fruit din tarike tadauki spoon tadau lemu zatakai baki is as if akwai so many things acikin zuciyanta dake damunta tace “wlh, wlh tunda nake arayuwana bantaba fasikanci ba, inada cikin 6months ina laulayi sosai aka kaini hospital akamin gwaje gwaje the next thing inada HIV, aka gwada Mijina baida shi, kishiyata ma baidashi babu wanda ya yarda da magana ta, Mijina ya koreni, yamin koran kare, nakoma garinmu dayake dagani sai yayana iyayenmu suka haifa shima ya koreni wai bazan jamai abun kunya ba yana babban mutun a kauye karnazo naraba ma kauyensu kanjamau, haka nai garari aduniya da ciki ajikina” Tasakeyin shiruuu tana kallon bowl na fruits din tace “har yau har yau bansan tayaya nakamu da HIV ba Riyad, haryau bansani ba” saikawai tafashe da kuka dayasa idanun Riyad sukai ja yasauke kanshi kasa Mama tabashi tausayi and wlh he believed her cus you can see honestly a maganan ta, her body language, maida bowl din tayi ta ijiye tace “cikin garari na haifi Rashida, komi nawa saida na saida just to sustained bata madara dan ban bata nono ba haka likitoci suka gayamin, ina zuwa clinic lokacin da karfina nafara aikace aikace ina goyata ahaka nasata school ta taso tanada ilimi har yar baiwa ake kiranta lokacin, cikin wahala sosai Rashida ta tashi, ba gatan uba ba gatan yan uwa, just ni kadai

takedashi, tun batasan menene HIV be sabida yanda jama’an unguwa ke constantly singing dinshi akanta tazo tasan menene shi, tana wajajen JSS1 karfina yasoma gasawa as small as that girl sai ita tasoma zuwa gidajen danake aikatau tanayi amadadina nina zauna agida sabida rashin lafiya tundaga lokacin kawowa yau Rashida dakake gani itace ci na, sha na, suturata, wajen zamana, magunguna na, kudin makarantan ta da komi, anywhere da zata samu aiki tayi she wants to go sabida batason taje taroki kowa yamana abu, ko an kawo mana taimako bata amsa, she’s 23 but she works like a 45yrs old man” Mama tai shiru tasa hannu ta share fuskanta chan tace “Riyad I’ve become a burden arayuwan y’ata, I’ve become a curse in her life, I believe idan na mutu she will enjoy life better….” “Mama!” Riyad yakirata da sauri, fashewa dawani irin kuka Mama tayi takalli Riyad tana bubbuga zuciyanta ta saman riga tace “I am hurt sabida I have the best daughter a duniya dabana iyama komi kawai nasata a wahala ne, I am selfish Riyad dan dana haifeta dazan iya kaita gidan marayu amman nace nizan raineta ta taso suffering, yara yammata irin ta suna gidan iyayensu akillace nawa na garari aduniya from morning to night bata airport, bata shagon abinci, bata hotel tana shara da wanke wanke da wanke bayi just to make ends meet, so I am selfish Riyad” Mama tafara sheshekan kuka da kawai kasan matan nan ta tara abu dayawa azuciyanta ne tace “na zaman ma Rashida alakakai arayuwa, na zaman mata annoba, sabida ni kullum aiki take, kowace yar budurwa na gidan iyayenta na jin dadi iya yen na nemo abinci su bata taci ni tawa ke gararin duniya ta nemo tabani naci, I’ve burden my poor daughter, I don’t deserve to be her Mother wlh I do not!!” Tashi Riyad yayi ahankali yazauna bakin gadon dan kukan da Mama take is getting too much, calmly yace “Mama don’t say that, you are wrong Mama!” Ahankali yace “kinsan yanda yarki ke sonki kuwa?” Saikuma yasa hannu a aljihunshi ya ciro handky yamika mata yace “goge fuskanki Mama nabaki labari” da kyar Mama tasa hannu ta karba ta share fuskanta tass takalli Riyad da jajayen idanunta, dan murmushi yayi just to calm her down but jiyake kaman yamata kuka shima yace “Mama all abubuwan dakike tunani akan yarki is totally wrong cus I see complete opposite of abinda kika fada” dan shiru yayi kaman mai tunani chan yace “all I see a idanun yarki is you are her motivation, her inspiration, her strength, her confident, Mama kece dalilin dayasa yarka is strong! Fearless and resilient, bold, I witness how she fought with her soul sabida ke Mama!” Dan murmushi Mama tayi ganin haka yasa Riyad yace “Mama ke kinga yanda tayi ne ai harni namiji saida na tsorata kartazo ta hada dani” daidai lokacin Mama ta kwashe da dariya yanda yayi maganan was sooo funny, ganin tai dariya yasa cikedason kwantar mata da hankali yace “Mama karki taba tunanin ke burden ce arayuwan ta ko curse all I see is kece the whole entire reason na existence nata, Mama yarki na sonki fiyeda tunaninki and duk yaran dake son iyayenshi bata taba daukansu koya kallesu a matsayin wahala kowani abu trust me Mama” murmushi Mama tayi tana kallonshi har cikin ranta taji sanyi da maganganunshi yace “idan you want her to keep being her ki warke kiji sauki sabida hankalinta ya kwanta Mama inba hakaba rashin lafiyanki will shatter her tiny little heart I’m sure ko’ina take yanzu hankalinta rabi da kwata na kanki she might not concentrate ko a school right”? Gyadamai kai Mama tayi ahankali saikuma chan tace “nagode Riyad, you

made me feel good” murmushi yamata yace “kici abincin ko zakisha yoghurt”? Gyadamai kai Mama tayi freely kaman ta sanshi da dadewa kawai saiya sauka daga gadon yabude ledan daya kawo yaciro komi yakawo ajuwa dates, ruwan Zamzam babban gora dakuma yoghurt, cup ya dauka na tea da aka kawoma Mama yaje ya zubar Mama sai binshi da kallo take ta natsu da yaron kaman tasanshi da chan, yataho da cup din ya tsiyaya mata yoghurt din aciki yabata karba tayi ahankali tace “bani dabinon” dasauri yabude daya yabata ta karba yadawo ya zauna tashiga sha tanacin dabinon wlh haka ya zauna da ita sai hira suke kaman sun san juna har Dr yashigo yadubata yadan shiga hiran shima na 5min kafin yawuce yatafi wajajen zuhur yafito yatafi masallaci ana idarwa yadawo yazauna Mama tace “bakaci komi ba” cikinshi yataba yace “kuma yunwa nakeji sosai Mama tea kawai nasha dazan fito” dasauri Mama tace “tashi kaje gida kaci abinci dan Allah” zaiyi magana aka bude kofan dakin da sallama Rashida ce tana sanye dawani material ja dogon riga ne har kasa ta yafa gyale baki kayan sun mata kyau sosai ta goya jakan school abaya da pink crocs din nan akafanta sai wayanta dake hannunta tana gumi a goshi dan da kafa tazo gashin gaban kanta duk sun kwanta, ko kadan batasan zata ganshi ba ganinshi yasa ta hade rai sai kawai ta shigo ta ijiye jakanta kan kujera tazo ta gefenshi takai hannunta da sauri ta taba goshin Mama tace “Mama ya jikin meke miki ciwo yanzu”? Dauke kanshi yayi daga kallonta Mama tace “lafiya na kalau” da idanu ta nuna mata Riyad hakan yasa ba yabo ba fallasa tace “sannu” wayanshi yaciro yashiga dannawa Mama tamata dakuwa da hannu hakan yasa ahankali tace “ina yini” shiru yayi chan yace “fyn” sai shegen jiji dakai sabida yaga yanada hotel halama na babanshine ba nashi ba tafadi aranta, maida wayan yayi a aljihu yamike tsaye yace “Mama bari naje”dasauri Mama tace “nagode nagode Riyad Allah maka Albarka nagode kaji saika dawo agida Mama” “zasuji” yayi maganan yana juyawa yawuce yafita wucewa wajen wardrobe na dakin Rashida tayi taciro kudin tarike a hannu tace “ina zuwa Mama” kafin Mama takirata harta bude kofa tafita daga dakin dagudu tabishi abaya ita bama tasan sunanshi ba hakan yasa ta kasa kiranshi gashi wayanshi na kunne har parking space yabude mota ya shiga mota yana kokarin tadawa tai knocking glass din hakan yasa yasauke glass din kasa ya zubamata mayun idanunshi haka nan taji gabanta yafadi kawai saitaji muryanta ya makale, dan gyaran murya tayi kadan duk yana kallonta sannan tadago hannunta dake dauke da kudin ta mikamai yabi kudin da kallo da aka daure da lobari sannan yajaye idanunshi dagakan kudin yazuba mata manyan idanunshi still baice komiba aranta tace “amman anyi dan wulakanci anan” saikuma ta daure ganin kallon kudin me yake mata tace “150k ne nan, sauran kudin daka kashe I will pay you back small small” dauke kanshi yayi daga kallonta ya kunna motan kaman wanda akace dole yayi magana yace “keep your money ban bukatanshi” jitayi ranta yafara tafarfasa sabida yanda yayi maganan a wulakance ta kalleshi tace “nikuma ban bukatar taimakon ka ko angayamaka i need your help to take care of my mother ne”? Da kokarin yin reverse yake but jin maganan ta yasa ya dan dakata yakalleta yace “you need all the help Rashidahhh!” Faduwa gabanta yayi yanda yakira sunanta saikuma amsan daya maida mata yadawo mata wani irin sparking taji tanayi zatai magana taga yayi reverse abinshi yana kallonta yana saka wani bakin

glass a idanu sannan yajuyar da kan motan yafice abinshi kaman ta kurma ihu takeji.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 14

Wuraren 3 Mama na zaune tsakar gida tana gyaran shinkafa ta kunna radio ta ijiye gefenta saman tabarma tana sauraro taji an turo kofa an shigo hakan yasa ta kafa ido taga wazai shigo bakuwa tayine saitaga Rashida sosai gabanta yafadi ganinta cus bata taba ganin Rashida ta shigo gida around this time ba, kallo daya ta mata tagane tai kuka dawuya ne Rashida tama wani abu tai kuka, ita kadai ke iyasa yarta kuka dasauri ta ijiye tray shinkafan tace “lafiya menene kika dawo dawuri haka?” Murmushi ta kakalo tace “Mama kaina ke ciwo sosai saisa nadawo” tai maganan tana zama kusada Mama kanta Mama ta taba tace “bari na kawo miki vitamin C kisha tashi ki cire jallabiyan kisha iska” tashi tayi tawuce ciki Mama tabi jakanta dayay strange girma da kallo sai kawai ta jawo tabude ganin karikitan ta ne ciki yasa da sauri ta tashi tabita daki tana tsugunne gaban ganamasgo tana neman kaya Mama tace “an koreki wajen aiki ne”? Dago kanta tayi ta kalli Mama zatai magana Mama tace “karki kuskura kimin karya an koreki daga wajen aiki ne?” Ahankali tace “Madam dina tace yau ne last day na aiki na a hotel dinsu” waje Mama tasamu dasauri ta zauna jin jiri zai dibeta tace “Meya faru tell me everything” Mama tariga ta ganota hakan yasa tafadima Mama komi ba karya, ba karamin baci ran Mama yayi ba tace “sau nawa zan gayamiki ki dinga hakuri arayuwa Rashida eh? Zagi na kari ne? Koko zagi na nunawa ajiki ne? Dan an zageni sai mene” dasauri Rashida ta kalli Mama, Mama tace “yes dan wata ta zageni and so wat dazaki hau fada awajen aikin ki kina hankade Madam dinki har sau biyu mai hotel din gabaki dayama shima kinmai rashin kunya” ahankali takai hannu ta goge hawaye tace “Mama bazan iya daurewa azageki agabana ba ko ace wani abu mara kyau wlh” saikuma tarushe da kuka tace “narasa me nayima yan layin nan duk inda nake aiki sai sunsan yanda sukayi sukaje suka batani su fallasani, wlh kowaye meyi ban yafemai ba” tabama Mama tausayi amman kawai saita wuce tabude drawer tadauko hijabinta har kasa ta saka da sauri Rashida ta mike tace “Mama ina zaki?” Cikin dan masifa tace “ina zani? Ina kuwa zani inba wajen aikin naki ba naje nabada hakuri itama yarinyar a nunamin gidansu naje nabada hakuri, idan babu aikin nan tayaya zaki gama makarantan ki eh? Me zamuci? Dame zaki sami kudin siyan tufafi? Ga wayanki ta lalace baki dawo da itabama that means bata gyaruba duk ina zamu samu kudin nan kafin kisami aikin nan kin manta kalan wahalan dakikayi eh? To zuwa zanyi nabada hakuri” dasauri ta taho takama bakin hijabinta tace “Mama dan Allah dan Allah karkije kinji Mama” fizge hijabinta Mama tayi tace “inda bakiso kisani naje nabada hakuri ai da bakiyi abinda zai tursasani inje ba, yau ko basu

karbeki ba dolena naje na bada hakurin abinda kikayi kinma mutanen dake gaba dake reni sannan kin fasama yar mutane hanci da baki” baki Rashida tabude zatai magana Mama ta nunata da hannu tace “kimin shiru anan” ta fiziğe hijabinta tajuya tafita fuu Rashida nada zuciya so tasan yarinyar didn’t even realize how important this work is to them most especially towards karatun ta she will do everything ta tabbatar Rashida tagama karatun ta lafiya.

Kafa Mama tasa ahanya tana tafiya ahankali kanta na sarawa amman ta daure cus she knows what school din Rasheeda means to her, she will not allow her to sabotage mean na school fees payment nata ba, she just hopes darajanta zaisa sumata afuwa.

Tanakai junction ta tare keke da taso taje da kafa ne, amman taji jiri na dibanta bazata iyaba, har hotel din aka kaita ta sauko tabiya kudin tajuya ta kalli tamkeken hotel din almost duka inda Rashida take aiki ta sani musamman take binta dan tasan inda diyarta ke aiki incase wani abu yafaru she knows inda zataje neman diyarta amman bata taba shiga wajajen aikinta ba, ijiyan zuciya ta sauke jin yanda heart nata ke beating saita dan natsu kafin ta shiga building din motoci cike anyi parking, hotel din yahadu bana wasaba, karasawa tayi zuwa entrance door din zata shiga from yanda take looking security guard dake gadon kofan shiga reception din yace “Hajiya wakike nema? Idan zancen taimakone Oga yace jibi ranan juma’a za’ayi rabon abincin azumi you can come by 10AM” ahankali Mama tanuna kanta tace “nine Maman Rashida sannunku da aiki, Rashida na aiki anan maybe kasanta, to tayi laifi ne shine nace bari nazo nabawa Oganta hakuri dan Allah akomar da ita sannan nabama yarinyar hakuri” kallon Mama sukayi sannan suka kalli juna kafin daya ya nuna mata kujera dake chan gefe wani plastic chair yace “guest da ma’aikata kadai ke shiga ciki jeki zauna achan Oga nada baki amman zai fito anjima kadan sai a gayamai” Mama batai musu ba tace “toh” wucewa tayi zuwa kujeran dasuka nuna mata ta zauna tabuga tagumi tai shiru burinta kawai karsu kori Rashida addu’anta kenan, gabanta sai faduwa yake cikeda fargaba.

Tunda yaje office nashi yayi shiru bakin dasukayi ma yawanci Munir ke kulasu, agogon hannunshi kiran Rolex ya kalla 5 tayi na yamma kaman an tsikaresh ya mike duk kallonshi sukayi “excuse me” yafadi tareda wucewa wajen kofa yafice Munir yabishi da kallo kafin yacigaba da abinda yake samin kanshi yayida shiga elevator ya sauka kasa, he doesn’t even know why he’s doing this but samun kanshi yayi da zuwa hanyar changing room din ganin kofan wangale abude yasa yadan

leka ciki babu kowa wajen fuzar da iska yayi yajuyo yafito daidai Madam zata shigo hanyar chak ta tsaya ganinshi surprisingly tace “Yallabai wani abu kake bukata”? Kaman bazaiyi magana ba saikuma yace “where is she”? Kallon hanyan Madam tayi tace “wa she? Oh mahaukaciyan nan”? Dan lumshe idanu kadan yayi hakanan yaji kalman azuciyanshi yadai daure bai nuna wani abuba ya kalleta, dasauri tace “ta tatare kayanta ta kwashe komi na locker ta tatafi tabar aikin da kanta kafin mu mata official kora” yanda taga yahade fuska yasa dasauri tace “sorr….” Ahankali yace “sack the other gurl Hus….” Cikeda Mamaki Madam tace “Hussyn Yallabai”? Babu wasa akan fuskarshi yace “I don’t want her working for my company, just compensate for the injury, give the other gurl a call tadawo aiki” yana maganan yawuce baki Madam yakasa kulluwa tana kallonshi, yarinyar data barar da ita yake cewa akirata back, wacce aka jibga yayi sacking, dan ijiyan zuciya tasauke aranta tace “his company his rule!” Tawuce ta tafi office nata.

Wucewa kawai yayi yabar wajen yafito, security daya budema wani guest kofa dazai shigo ne ya hango yallabai hakan yasa yashigo ciki da gudu daidai zai shiga elevator yace “Yallabai barka da hutawa dama wata mata ke nemanka awaje” wani kallo Riyad yamai irin wata wa? Shi kuwa? Dasauri security yace “tace wai itace Maman yarinyar da aka kora tazo tabada hakuri tana waje, she’s Rashida’s Mom Sir” hakanan Riyad kawai yaji gabanshi yafadi but yadaure yace “why is she sitting outside?” Dan sauke kanshi kasa Security yayi yace “uhmm Yallabai cewa akayi cutan kanj……” fuuu Riyad yawuce zuwa entrance door din kafinma abudemai kofan dayake glass door ne yana iya hangota yanda tazauna kan kujera tayi tagumi tana kallon waje daya cikeda tsananin damuwa and kana kallon matan kasan she’s really sick she looks so skinny and pale jiyayi zuciyanshi yamai ba dadi sosai yanda security sukai trashing nata awaje haka, dasauri yafice bayan an budemai kofan yayi wajenta direct yana zuwa kawai saiya duka cus bemasan mezaiyi ba, she’s the mother of the girl that save his life kome yayi bai biyataba, cikeda girmamawa yace “Mama” firgigit Mama tadawo daga dogon tunani datake tajuyo ta kalleshi, dasauri tace “Naam Bawan Allah kaina mai wajen nan nazo nabada hak…..” kafin takarasa maganan dasauri yace “Mama” hakanan Mama taji yanda yakirata yataba zuciyanta, yanda yakira sunnan just touched so many things a zuciyanta kawai sai hawaye, life and sickness nata have made her so emotional, muryanta na rawa tace “dan Allah dan Allah kuya kuri nasan Rashida da zafin zuciya ga fada ga taurin kai, kome akace tama yarnyar nan nasan tayi dan Allah kuyakuri kurufamin asiri kada ku koreta daga aikin nan dan Allah ku taimakeni” tai maganan tana jan kujeran baya zata duka dasauri Riyad yakama knees nata ahankali yace “Mama dan Allah karki rokeni, ban koreta ba zata iya cigaba da zuwa aiki” da sauri Mama ta kalli fuskanshi tace “da gaske?” Gyadamata kai yayi yace “eh” ijiyan zuciya Mama ta sauke tace “to inane gidansu yarinyar naje na bada hakuri” ahankali yana sakin knees nata yace “basai kin bada ba lafiyanta kalau Mama, is just normal misunderstanding da kananun maganan yara yajawo fadan kada ki damu kinji” gyadamai kai tayi tace “Allah maka albarka” murmushi yamata kadan baice komiba, Mama tace “bari natafi gida to Alhamdulillah nagode nagode nagode kaji”

daga yanda take maganan kasan hankalinta ya kwanta gyadamata kai yayi, Mama tace “to sai an jima” “saida safe Mama” yafadi ahankali, Mama ta wuce cike da farin ciki tafara tafiya kadan kadan sabida yanda kanta ke sarawa, tayi tafiya daya biyu uku ana hudu kawai ta yanke jiki tafadi, Riyad na tsaye yanama security magana sukaji karan fadin abu juyowa sukayi ganin Mama yasa dawani irin gudu Riyad yayi wajenta suma security din haka dago kanta yayi yana tapping hannunta yana kiranta. “Mama Mama Mama” amman shiru dasauri yace “help me” daukanta sukayi yabude bayan motanshi yasata yakoma yashiga gaba yatada motar sai wani babban private hospital dayake zuwa anytime yake Kano yana zuwa aka karbi Mama sai emergency yawuce office na Dr dinshi ya shiga Dr ya sallami patient dayake tareda shi yace “Ranka shi dade mai Martaba” dan yatsine fuska yayi yace “don’t call me that I have a patient tana Emergency I want you to be on her case fast” tashi Dr yayi suka fito tare ya shiga emergency din, shi ya tsaya agaban wajen yarasa yanda zaiyi sai kuma yakoma office na Dr ya zauna, yana nan zaune yana jiranshi har aka kira magrib saiya tashi yafito yawuce mosque yana gani Munir na kiranshi yaki dauka salla yayi yafito yawuce ciki yakoma office na Dr yazauna sai gashi Dr yashigo dasauri Riyad yatashi yace “how is she ta farfado?” Gyadamai kai Dr yayi yace “da kyar muka samu ta farfado amman tana bacci” saikuma ya zauna ya kalli Riyad yace “kasan wacce ka kawo? Who is she to you?” Batare daya amsashi ba yace “does that matter? Meke damunta? How can I help?” Gyara zama Dr yayi yace “she’s HIV patient!” Yayi maganan yana kallon fuskan Riyad dayaga bai chanza ba saima yace “me da me take bukata yanzu”? Ahankali Dr yace “is like she’s on medication so bahsine abinda ke damunta ba bashine kuma dalilin yankewan jikinta tafadi ba, abinda yafi komi damunta is BP, BP ta yayi raising sama sosai I don’t think zan sallameta yau ko gobe ko jibi ma sef, sai ya sauko sannan zan sallameta, just get wanda zai zauna da ita and then drugs” yashiga rubuce rubuce duk Riyad na kallonshi saida yagama komi sannan yanunamai takardan, tashi Riyad yayi yazaro wallet dinshi ya ijiye akan table din cikeda izza yace “take any amount kake bukata for drugs, bills, pin is 6648” yana maganan yawuce yafita akasaitance yasauka kasa dakin dayaga an shiga da ita yawuce shiga yayi ahankali ya tsaya bakin gadon an cire hijabinta daga ita sai riga da zani da hulan dake kanta an samata drip, shiru yayi yana kallonta sannan yajuya yafice daga dakin yawuce yaje motanshi yashiga yadau wayanshi yana shirin kiran Munir wayanshi yashiga ringing Munir dinne yana dagawa kafin yayi magana yace “Munir open file na employees dina a desktop get info na Rashida I need address nata ASAP” kafin yayi magana ya katse wayan yayi shiru chan saiga Munir din yakira yace “suna Ranji, wajen tudun Murtala” baimasan inane wajen ba but haka ya katse wayan ya kunna google map yashiga driving….

Tunda tai magrib ta zauna tai shiru tana mamakin ina mama taje harta dau hijabi kota bita hotel dinne ko wani case dinne akeyi achan but karta kara bata ran Mama taje wajen hakan yasa ta daure ta hakura, kuma zai iya yuwa tadawo takai karanta wajen Baba liman ne dantana haka wani zubin hakan yasa ta zauna adaki zugum

kaman wata marainiya idan aka kira isha’i bata dawo ba zatasa Hijabi taje ta nemeta….

Shigowa layin yayi ga majalissar maza gaban shaguna ana zance rage wutan motan yayi karya haskosu yana karasowa yakashe motan kawai ya bude ya sauko yazo wajen yamika musu hannu yace “Assalamu Alaykum” atare duk suka amsashi suna karban hannunshi ganin arniyan motan dayake ja, yace “dan Allah tambaya nake” dasauri sukace “Allah sa mun sani” anatse yace “gidansu Rashida nake nema” tsit wajen sukayi kaman ba su ba saikuma daya daga cikin samarin yatashi yace “bismillah yallabai zomu kebe mana” binshi Riyad yayi sujkaje wajen mota kaman mutumin arziki yace “nasan ba laifinka bane Rashida kam nada kyau Masha Allah yarinya kaman Balarabiya amma dai kyan dan maciji ne, yanda muke gayamaka dinnan haka muke gayama duk wani saurayi dazaice zaizo nemanta hakkinmu ne na yan unguwa, hakkin makotaka tunda su basu fadin gaskiya” tunda yafara magana Riyad yaji ranshi na baci amman ya daure dan he wants the address, mutumin yace “kagadai uwar yarinyar nan fasika ce garin kwashe kasheta ta kwaso kanjamau Rashidan ma muna kyautata zato tanada shi tun acikinta tasam….” “Zaka fadamin adreshin ko bazaka fadi ba”? Riyad tafadi sounding bitter and angry baki mutumin yabude zaiyi magana Adamu mai chemist da tun zuwan Riyad ya hangoshi daga chemist yace “kaje chan kasan layi zakaga gida mai jan kofa nan ne gidansu Rashida” kallonshi Riyad yayi yace “thank you” yawuce yakoma mota yatada mota yabar wajen, gaban gida mai red door yayi parking ya sauka ya tsaya gaban kofan yakai hannu yayi knocking, Rashida na zaune kan dadduma taji ana knocking hakan yasa ta tashi dasauri batare data cire pink hijab dinta ba tafito silipas ta zura gabanta sai faduwa yake ta taho zaure tana mamaki Mama ta kulle kofan ne dazu dan idan aka rufe yana shiga jam, ganin kofan abude ga wani arnen black car parked agaban gidansu wani mutumi a tsaye yajuyama kofan baya so bata ganin fuskanshi yasa ta fito kai tsaye cikin muryanta mai bala’in dadi tace tace “kaine kai knocking wa kake nema?” Har cikin zuciyanshi yaji sanyin muryanta hakanan, cikeda wani irin kwarjini yajuyo yana zuba hannun cikin aljihun rigan dake jikinshi, hada ido sukayi ta kalleshi ido cikin ido dan akwai wuta a kofar gidansu mamaki da tunani yacika kanta, ba mutumin nan bane mai hotel dinda take aiki ba? Ko idanunta gizo yake mata? How is he agidan su? Ganin ya tsaya yana kallonta bayako kyafta ido yasa tadan dauke kai tattare bakin hijabinta tashigayi tana tabawa saikuma takai hijabin bakinta, saichan tacire, saikuma chan ciki ciki kaman an sata dole ahankali tace “ina yini” he’s looking at her mostly sabida baisan mezai fada mata ba, chan yace “Mama wants to see you” hakanan gabanta yayi bala’in fadi dasauri ta kalleshi baki tabude zatai magana saita kasa sabida yanda kirjinta ke bugawa da gudu da sauri sai kawai ta tsugunna, wani irin tausayi yaji tabashi yakasa cemata komi, da kyar kusan 30sec sannna ta mike jin tadawo daidai cikeda karfin hali tace “ina Mama wat happened to her? Nace mata kartazo tabada hakuri but taki jina, normal Mama da tuni tadawo, tana ina yanzu? Just tell me wat happened to my mother mekuka mata? Me kuka gaya mata? My Mom is very sick,

tell me tana ina yanzu?” Tai maganan hawaye na cika idanunta harwani kyalli suke adake still kallonta yake yace “she’s fine now but tana hospital” hannuwanta biyu ta daura a fuska saikuma ta juya takai hijabinta ta goge fuskanta tass tajuyo ta kalleshi da jajayen idanun hijabinta daya jike da kuka ya kalla sannan yakalleta, cikeda dauriya da karfin hali tace “inane asibitin bani address din natafi” batare dayay magana ba yajuya yace “get few things da Mama zata bukata lock the house I will take you there is late bazakije da kanki ba” yayi maganan authoritatively yawuce yabude motan ya shiga gaba, kallonshi tayi sai hawaye sai kawai tajuya takoma cikin gida, drawer tabude takwaso simple t-shirt tasa ajaka tadaga kayansu ta dauko ledan duka kudin dasuke ijiya 139k, tadauki dadduma da zanin gado wankakke tasa ajakan bayanta takashe wuta tafito sai goge hawayenta take tarufo kofan waje tasa key sannan tajuyo ta kalli motan, bata taba shiga mota babba haka ba, ahankali yakawo hannunshi yabude kofan ganin yanda take kallon motan kaman matsoraciya, daurewa tayi ta matso ta shigo ta zauna agaban ta maida kofan tarufe wani sanyi da kamshi na dukanta ta rungume jakan a hannunta gam.

Tada motan yayi ahankali sannan yafara tafiya bini bini tajuyar da kanta takalli gefen window tana goge fuska, sunyi tafiya na kusan 30min sannan sukakai asibitin da saida ta firgita ganin kyanshi dan tasan zaiyi tsada tayaya zata biya kudin? Parking motan yayi yafito, kokarin bude kofanta tashigayi tafito takasa, cus ba irin normal kofan mota data saba dashi bane, abinma yana nema yakarasata kuka ta daure ganinshi ya zagayo ta inda take yana kallonta ta glass dan wannan motan ba tinted bane, bude mata kofan tayi da sauri ta sauko batare data kalleshi ba ta tsaya gefenshi dan nesa dashi maida kofan yayi yarufe sannan yafara tafiya tabiyoshi abaya da saurinta suka shigo cikin hospital din har zuwa dakin da Mama take kwance kafinma yasa hannu yabude kofan da sauri tasha gabanshi ta rigashi tura kofan tashiga ta tsaya chak tana kallon Mama dake bacci an samata ruwa an makala mata wasu abubuwa a hannu yarda jakan dake hannunta tayi awajen tawuce dakin da gudu taje inda Mama take kawai ta kwanta jikin Mama ta manna fuskanta akan wuyanta tana kuka sosai wanda babu kara idanba ka kalli kakkarwan da jikinta keyiba bazaka gane kuka takeyiba, ahankali yaduka yadauki jakanta yashigo dakin yakawo gefen gadon ya ijiye saikuma ya zuba hannayenshi a aljihu yana kallonsu, takai 3min ahaka sannan ta taso da sauri ta dauki Dr note dake saman table na gadon ta shiga karance karance magungunan da alluran dake wajen ta shiga duddubawa tana karantawa har drip din da aka samata sannan ta sauke ijiyan zuciya tasake zama bakin gadon takama hannun Mama tarike gam tana kallonta, kawai kana ganin Rashida kasan yanda takeson Mamanta, ta dade ahaka tana kankame da hannun Mama sannan tasaki hannun takai hannayenta ta share fuskanta tajuyo tareda tashi tsaye ta kalleshi hada ido sukayi da sauri ta dauke kai cikin muryanta dahar ya chanza sauti sabida kuka tace “nawa ka kashe nabiyaka inaso akira Dr ya sallameta na nemo keke napep nakaita chan asibitin datake amfani dashi” yana kallonta right in the eye yace “which hospital”? Ahankali tace “teaching hospital” kai tsaye cikeda izza da iko kaman Mamarsa yace “kibarta

anan” da sauri ta kalleshi sake hada ido sukayi cikin konewan idanu Rashida tace “wannan kuma nice next of kin nata i decide and make decision for my Mom not you, nawa nidai ka kashe” yadade yana kallonta baitaba ganin feisty mara kunyan yarinya irin this girl ba, yana kallonta yace “idan Dr yazo ki tambayeshi” yajuya zai wuce tace “eh zan tambaya and i will pay you back cus banson any favor ko taimako from anybody zan kawoma kudinka” dan jimm yayi sai kawai yabude kofan yafita, mota yawuce yashiga yatada yayi dialing number Dr yana dagawa yace “Dr on no condition zakai releasing that patient without letting me know, don’t let the Daughter take her to another hospital, sign them up for abinci” cikeda girmamawa yace “to Ranka shi dade” dan yatsine fuska yayi ahankali yace “and about that!” Yadanyi shiru chan yace “don’t disclose my identity to anyone nor address me ahaka in front of anybody” Dr yace “shikenan Riy….” Harya katse wayan ya bala’in gaji hotel yakoma ya kashe mota ya sauke ya shiga ciki ana gaidashi ko amsasu baiyiba yawuce office nashi straight yana budewa ya shige ganin desktop a kunne yasan Munir na ciki, hakan yasa yawuce ciki Munir na kwance yana buga game a tv dagashi sai singlet da 3quater ganinshi yasa ya ijiye remote yataso yace “ance Maman yarinyar tazo and she fainted kasata a mota hospital ka kaita” yana cire riga yace “eh” tsayawa Munir yayi yana kallonshi yace “I know the girl itace wacce saved you but are you sure zaka barta tacigaba da aiki kai the girl have quiet a temper” batare daya amsashi ba kawai yawuce yafada bayi wanka yayo yafito daure da towel a waist turaruka ya tsaya ya fesa sannan yazo yazauna, Munir tace “Mom takirani yafi sau goma nace mata we are not together tace she will call back in the next 5mins idan ban hadata dakai ba zata kai karana wajen Ammi” Shiru yasakeyi hakan yasa Munir yadafa kafadanshi yace “common mana fushin ya isa haka before kasa karyan vakada lafiya da Mami tayi azo asani please go back home” yatsine fuska yayi yace “I’m hungry Muneer, please kaje gida ka kawomin abincin Ammi” tashi Muneer yayi yace “okay”.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 16

Rashida tadade awajen tsaye ranta na kunan wulakancin daya mata sannan takoma ciki Mama tace “ina kikaje”? Kudinsu ta nunama Mama tace “naje rage kudin daya kashe mana ne amman yaki kulani” yanda take maganan kasan ranta abace yake Mama bata cemata komiba idan sabone tasaba da halin Rashidan nan na batason ataimakesu, itafa kawai bataso ne sabida gori da wani abu dazaije yadawo.

Har dare duba Mama ake akai akai ana zuwa auna BP da sai sauka yake ahankali ahankali, kawai Mama is at stage da batason damuwa da wani abu dazai tsoratata ko tadamata da hankali ko kadan, tare suka sauko sukai isha’i suna idarwa tazare hijabinta ta ijiye nan kan dadduman yanda kanta kemata nauyi sabida jiya batai

bacci ba jiya batasan lokacin data wuce tahau kan gadon ta shige cikin chan bango danta barma Mama dake azkar space nata, taja bargo ta rufa ko 1min bata karaba sai bacci tafara jan munshari juyowa Mama tayi dagakan dadduma ta kalleta sai kawai ta cigaba da jan charbinta tana zikiri, knocking akayi tareda budo kofan Mama tace “bismillah” ahankali ya shigo rikeda basket na kayan abinci wannan karan yana sanye da jean da riga dasukamai kyau, dasauri Mama tace “Riyad kaine sannu da zuwa” zata yunkura dasauri yace “No Mama karki tashi” yataho inda take ya duka basket din ya ijiye yace “abinci nakawo miki Mama na gida, nasan abincin asibiti ba dadi” murmushi Mama tayi tace “sannu da dawainiya Riyad, sannu Allah saka da alkhairi, ni bandama bakin maka godiya again” dan satan kallon Rashida yayi daya hango a gado tarufa da bargon gadon sabida AC amman kana ganin fuskanta karaf a kan idon Mama dauke kai yayi dasauri daga kallonta yamike tsaye yace “Mama bari naje” dasauri Mama tace “nagode Riyad saida safe ayi tuki ahankali” “Toh Mama” yafadi yajuya hakanan yasami kanshi da sake kallonta yana tafiya harsaida ya bude kofa sannan yajuyar da kanshi ya kalli kofan yafice Mama tadanyi murmushi kadan tareda bude kulan, she just feel wani irin strong trust for Riyad connection that she feels towards the boy yawuce misali, bude kulan tayi taga tuwo da miyan kuka ga man shanu da yaji a gefe da namomi sai kuma 3rd kulan pepper soup ne, shiru tayi tana kallon abincin tana tuna rayuwan datayi abaya ire iren abincin nan sune cimarta dan abincin da Baban Rashida yafici kenan, he always complements abincinta especially pepper soup yace baitabacin pepper soup mai dadin nataba, spoon tadauka ta debo naman takai baki wato duk kalan dadin rayuwa da mulkin dakake ciki idan Allah yaso kwacewa it takes seconds yayi hakan, alokacin bata taba sanin zatai rayuwan da abinci zai gagaresu ba! Ijiyan zuciya ta sauke sai kawai ta ture tunanin kafin kanta yafara ciwo.

Mota Riyad yawuce da Munir keciki yana jiranshi yabude gaba yashiga Munir yatada mota yace “hope she’s feeling better tunda you don’t want me to go with you” yatsine fuska yayi yace “thanks for the food daka karbomin daga wajen Ammi”baicemai komiba suka wuce gida, ta side nashi suka shiga as usual, parking Munir yayi yawuce yafita dan yaje side nasu shikuma yawuce flat dinshi, zaune yaga Mom afalo tana ganinshi ta taso da saurinta tazo wajen kawai ta rungumeshi saikuma ta dago tahau taba fuskanshi tace “you have not been eating Son, look at you, duk ka rame” ahankali yace “I’m fine Mom” waje yasamu ya zauna Mom ma tazauna tace “kayakuri kayafema Haleematu is not her fault banson kayi fushi da ita over petty mistake, she’s just 25 yanzu so kagani she’s still a small girl, kishi take batason ka kula mata which nayi supporting hakan” kaman bazaiyi magana ha saikuma yace “Mom she needs to learn to respect my privacy, tadena bincikamin kaya and tadena…..” yadanyi shiru Mom tace “tadena me?” Baki yabude saikuma yayi shiru sai chan kuma yace “tadena sharing my private affairs with my Mom” dakuwa Mom tamai tace “she shared private affairs naka dani da duniya tai sharing? Zanje nagayama duniya baka iya kwanciya da matanka kullum ne”?

Lumshe idanu yayi sai kawai ya kalli gefe duk Mom na kallonshi sai kawai ta mike tsaye tace “if you don’t want that then kaima do the needful, kama yarinyar nan ciki kagani, I just need heir to the king, gabaki dayan masarautan nan jira ake aga matarka ta haihu so kake ace ita juya ce? Yanzu gashi kayi fushi kabar gida 2 nema ko 3days yanzu bakuyiba, I will tell her to come now kuma wlh kamata maganan fadan nan saina sabamaka umarni na baka, tarayya nace kuyi kui bacci good night” tai maganan tawuce tana fita daga daki yabita da kallo wondering wat happened? Mom bata damunshi ada tana duk abinda yaga dama yanzu ko she dictate everything. Tashi yayi ahankali kawai yafada bayi yashiga wanka fitowa yayi ya shirya cikin pajamas yadan gaji so he just wanna sleep kwanciya yayi yana kashe wuta yana ji akai iso Sarauniya zata shigo ta telecom ana neman izininshi dan barinta danna boturin yayi alamun a barta, da saurinta Haleematu ta shigo taci gayu tasaka gold alkyabba wucewa ciki tayi da sallama ta shiga bedroom nashi dayayi sanyi sosai ga duhu hannu tamika zata kunna wutan strictly yace “karki kunnamin wuta” da sauri ta tsaya saikuma ahankali tashiga cire Alkyabban wasu arnan kayan bacci tasaka tataho ahankali ta hayo gadon kawai ta rungumeshi tana manna boobs dinta awuyanshi tace “I’m sorry Ranka shi dadi bazan kara maimaita kallan laifin dana maka ba dan Allah ka gafarce ni kaji”.

Kasa magana yayi yay shiru dago kanta tayi takai hannunta kan gefen fuskanshi ta shafa tace “amin afuwa akulani” tashiga shafa fuskanshi ahankali zuwa kirjinshi zuwa kasa daidai zata kai hannun wandonshi kawai ya jefata gadon yabita yanajan wandonshi kasa he don’t know so many things na zuciyanshi harda mara kunyan yarinyar nan he just needs natsuwa kawai ya shigeta tareda sakin ijiyan zuciya sannan yafara ita kanta takasa gane yanason sex ne bayaso ne oho shifa yafi karfin ya nemeki saidai ke kizo, kuma kikazo ya rikeki kaman mayunwaci wani zubin, saida tafara kabar da hannayenshi akan boobs dinta sabida yanda suke mata shegen zafi yau dan he’s handling her very rough but yaki yau yabata wahala saida tafara tureshi amman cinta yake chan ya kankameta yafara numfashi da karfin gaske ahhhh! Uhmmmmm! Assshhhh! Ya feso ciki sannan yasaketa dasauri yatashi yawuce yafada bayi wanka yayo kawai yafito feeling calm ya kwanta sai bacci.

Wuraren 7 Mama ta tursasata dole taje gida ta shirya ta sanar da Baba Liman batada lafiya sannan ta tafi school karta kara latti bataso tabar Mama ita kadaiba amman tawuce ta tafi, yau in patient pediatric ward tayi aiki the kids loves her, she’s so gently and sweet with them har sauran yan group dinta ma were jealous hakadai tai aiki har 1 tai salla ta tafi tadawo hospital har dare Riyad baizo ba suna zaune kan dadduma Mama tace “yau Riyad shiru” tabe baki Rashida tayi tace “sai kace daman kin sanshi daga wani waje ne ni wlh bakiga yanda nakejin haushin sa ba na tsanes……” wani kallo da Mama tamata yasa ta hadiye maganan kawai ta tashi tawuce ta zauna akan kujera tahau duba log book nata tana yan karance karance, tadauki book tana karatun everything datayi takuma koya tunda bata samu taje library ba sabida Mama, anan kan kujeran tai bacci.

Yau dadi takeji za’a sallamesu Mama tace “wai bazaki school bane” dasauri tace “Mama Dr yazo ya sallame mu zan kaiki gida saina tafi ai nadauki permission a hospital” Shiru Mama tamata wajajen 9 Dr yazo yakalli Mama dayaga har hijabi da kaya ta chanza sun gama arranging komi yace “Mama yanzu kin gaji damu zaki tafi ki barni”? Dan dariya Mama tayi tace “ai asibiti ba abun so bane likita dan haka zan tafi in barka fa” dariya yayi sosai yaduduba Mama duk Rashida na kallon abinda yake da manyan idanunta kaman za’a Mamanta wani mugunta yace “Alhamdulillah Mama BP ki yasauko Mama, dan Allah ki rage tunani kinji” yajuyo ya kalli Rashida yace “makesure baki barin Maman ki na yawan tunani, da shiga damuwa da stress da tashin hankali none of abinda na lissafo is good for her, she needs to be happy all the time, Mama take your drugs akai akai kinji Mama” gyadamai kai tayi sannan yabama Rashida takardan sallama yaced “you can go now, mun sallameta everything has been cleared by Riyad, ga magungunan ta nan bari namiki bayanin yanda zatasha” yashiga yima Rashida bayani gyadamai kai tayi tace “thank you” murmushi yayi yace “Mama yarki kaman Balarabiya akwai wani akasa ne idan babu kowa ina kam…..” kasa karasa maganan yayi sabida turo kofan da akayi babu ko knocking duk suka juyo Riyad ne, yasaka wani ash color shadda mai haske yana wani irin kamshi mai dadi dake banbanta shi da mutane da dama, dasauri Rashida tadauke kai daga kallonshi mugun haushinsa takeji, takalli Mama tace “Mama tunda na hada komi bari naje na nemo mana keke napep” kafin Mama tabata amsa ma tajuya ko kallon Riyad batayiba tabi ta gefenshi tafice, Dr yace “ahh Riyad kaine barka da zuwa” adikile yace “yauwa” dan kallonshi Mama tayi bata tabajin irin muryan nan tattare dashi ba, kin kallon Dr yayi yawuce wajen Mama yace “Mama ina kwana nazo nakaiki gida” yakalli kayan dasuka hahhada yaduka ya kwasa duka da kulolin yafice Dr yabishi da kallon Mamaki, aranshi yace “who are this people to Riyad cus this is just more than help akwai wani abu akasa, look at the way he’s serving them” saikuma yakalli Mama yace “Mama Allah kiyaye hanya” yawuce yafita shima, shiru Mama tayi kaman mai tunanin wani abu sai chan tai murmusa kawai, shigowa yayi yazo har wajen gadon yace “Mama can you walk? Ko in dauko kujera”? Dan murmushi tayi tace “haba zan iya tafiya Riyad” saukowa tayi daga gadon ahankali tafara tafiya yana kaffa kaffa da ita dudda bawai riketa yayi ba Mama ta rame sosai kaman iska zai kadata tafadi sunyi tafiya sun fito cikeda kulawa yace “zaki huta Mama?” Wlh har cikin zuciyanta tajejin Riyad yanzu, he’s caring and just too protective da sauri tace “a’a bangajiba da karfina fa muje kagani” murmushi yayi suka fito har wajen mota baya yabude mata dayake jeep ne sai alokacin ya taimaka mata ta shiga ta hanyar dan dukawa ya nuna mata shoulder shi yace “dafani ki shiga” kallon shaddan jikinshi kalkal Mama tayi saikuma ta kalli hannunta dudda bawai datti bane a hannunta amman saitace “kai haba karna bata maka kaya” ahankali yakai hannunshi yakama nata yadaura akan shouldershi yana rage tsayi yace “Mama kibata duk albarkanki ne” ahankali Mama tai murmushi kafin ta dafashi da kyau ta daga kafanta ta taka step din ta shiga motar yana kallonta yace “are you comfortable Mama” gyadamai kai tayi tace “yes Riyad thank you”

daidai lokacin Rashida na shigowa hospital din tana cikin wani empty keke napep ta hangosu, azuciye ta sauko ta taho wajen daidai yajuyo, chak ya tsaya yayi folding hannunshi a kirji tundaga kan kafafunta yake kallo dake cikin wani bakin flat shoe daya gama mutuwa but dudda haka kafanta ya haska flat shoe din, zuwa skirt dake jikinta na atampa da pink hijabin data saka mai hula ya tasya mata a guiwa, tana zuwa ta tsaya agabanshi cikeda masifa tace “bakai zaka kaimu gida ba nariga na kira keke” wani banzan kallon raini yamata yace “then saikije ki sallameshi” yanda yamata maganan kaman ta kurma ihu mutumin nan dan bala’in rainin wayo ne sabida yaga yanada kudi da hotel shine zai dinga ma mutane magana yanda yaga dama, wai ina ruwanshi dasu? Cikin fushi tace “nace maka kafito mini da Mamana daga motan ka, wayasani ma ko dan yankan kaine kai tunda sai shegemana kake” wani kallo yamata sai kawai yawuce yabude mazaunin direba ya shiga ya zauna itakuma ta shiga kiciniyan bude kofan back sit, da hannu Riyad yakira mai keken da sauri ya sauko yazo wajen yace “gani yallabai” kudi dayawa yazaro daga aljihu ya mikamai yace “gashi kaje” karba yayi yahau godiya Mama tai murmushi ciki ciki dan duk tana kallon draman tai kaman batasan sunayi ba making sick and tired face, danna glass na window tayi takalli Rashida dake tsaye tana kallon Riyad kaman zata iya fada dashi akace tayi, Mama tace “shigo muje kina batama Riyad lokaci zaije aiki fa Rashida” kallon Mama tayi har idanunta sunyi ja akufule tace “kuje ni bazan shiga motan ba” Mama na kallonta tace “zan saba miki fa wlh, zoki shiga mota muwuce” kallon Mama tayi bataso ta batama Mama rai yasa ta danne zuciyanta da kyar ta zagayo harta bude kofan baya Mama tace “tunda ga direba kin samu ko dole ki shigo baya” wani sweet smile Riyad yasaki ya gyara fuskanshi da sauri yana kallon waje kaman baisan anayi ba, kaman tayi ihu Rashida ta maida kofan tarufe takoma gaba tabude kofan ahankali tadan kalleshi ganin waje yake kallo abinshi yasa da kyar tashiga ta zauna ta jawo kofan tarufe tana harare harare, murmushi yayi yatada yajuyo yadan kallo Mama da tausassan murya yace “Mama are you comfortable? Natada motan” wani irin murmushin dadi Mama tasaki tace “I’m comfortable d’ana muje” wani irin zafi Rashida taji aranta yanda Mama takira Riyad danta kawai saita ciro wayanta ta manna earpiece tasa a kunne, tada motan Riyad yayi suka tafi baya wani gudu sosai, Mama sai hira takemai kaman tasanshi hakan yakara tunzura Rashida dudda batajin mesuke fadi but tana ganin bakin Mama na motsi, har anguwansu hira suke sai kallon motan ake a kofar gidansu yayi parking ya bude kofa ya sauko yabude baya Mama ta sauko ahankali yabude booth ya kwaso bags nasu Mama tace “key na bakin jakan” takai hannu tasa blavk jakan aljihun taciromai tabashi yana sane yasan bata iya bude kofan motanshi ba ya shareta shiga da Mama ciki yayi sai kallon gidansu yake koina a gyare tsaf zaunawa Mama tayi yace “bari naje Mama Allah kara sauki” Mama tace “nagode nagode Allah maka Albarka, wai ina Rashida ne hala ta wuce wani waje” baice komiba yawuce Mama tabishi dagodiya dayake motan tinted ne baya iya ganota but yaga yanda motan ke motsin ana bubbugata yayi kaman bai saniba yawuce yabude kofa yashiga ya zauna batare daya kalleta ba yace “wat are you still doing in my car”? Akufule tace “inba dole ba mema zai kawoni cikin your so called car”? Still yaki kallonta yace “get out!” Kaman yana magana dawata dabba kirjinta tafarfasa yake

tace “ka budemin kaga idan nakara wani numfashi a motan naka” dan kallonta yayi strictly yace “who are you to make Riyad work for you”? Mamaki ne yakashe Rashida irin what exactly guy din nan thinks of himself ne, tadai daure ta danne zuciyanta da kyar tace “to ai ban iya bude kofan bane ni” dan juyowa yayi yayi facing nata yace “then learn to soften muryanki and ask for help politely miss” ido cikin ido take kallonshi ya zubamata mayun idanunshi dayasa kawai taji jikinta namata wani iri, duk yanda taso ta daure tacigaba da kallonshi itama saita kasa tadauke idanunta dan kasa jure kwayar idanunshi tayi, ta hadiye wani abu da kyar dataji yaa tsayamata a wuya tadan runtse idanu kai kasan she’s about to say komene zatace ne out of compulsion tace “kadan budemin kofan motan nafita” sosai yake kallonta sabida yanda kawai yaji muryanta pierce his heart, this is the first time tunda ya santa takemai magana softly but da gangan dan ya kureta yakaita bango yace “soften your voice more and add please cus no one command Riyad!” Da sauri ta kalleshi wani kallo yamata na idan baki fadi ba zanja motata nayi gaba abuna, kaman tayi ihu takeji shine namiji na farko so far so good tunda ta girman nan ya iya tankwarata yakuma juyata haka, batasan mesa ba batakaimai duka ko kokawa ba the normal ita datuni takaimai duka suyi dambe but shi takasa, agogon hannunshi yakala kirar TAG Heuer yace “you have 5secs left ko i will go wherever zani u will be here is none of my business” yayi maganan yana kunna motan ma abinshi, wani ijiyan zuciya ta sauke ta sauke muryanta kasa kaman ba ita ba sounding like a Baby tace “kadan budemin kofan motan” dan juyo da kanshi yayi ya kalleta muryanta is the best muryan mace daya tabaji in his entire life, yanda yake mata wani irin kallon yasa ahankali kaman ba itaba lips nata na rawa rawa tace “p……..p….lease…..please!” sannan ta dauke kai da sauri kaman tai abin kunya din nan, sabida son yakaita bango gabaki daya shikuma annoyingly and authoritatively yace “good gurl!” kaman wata damusa ta kalleshi for the first time Riyad yasakin mata wani kalan murmushi dayasa taji zuciyabta yabuga rasss! Yana beating dum! Dum! Dum!! Da sauri ta dauke kai trying to control yanda zuciyanta ke beating takasa, dan tasowa yayi daga sit din dayake ta gefen ido taga ya nufota da sauri ta juyo da kanta ta kalleshi dan kaman zai hugging nata, hada ido sukayi gashi yaki daina kallonta kaman akwai wani abu dayake son gani game da ita sai kawai lips dinta yahau rawa tawani koma baya da sauri ta manne jikin kujeran kaman zata nitse ciki har hannunta rawa yake barin yanda kamshin turarenshi ke shiga hancinta jinshi dab da ita infact yadin kayan jikinshi ke tabata ta she was scared, lost, shaking, it was just a freaking reaction jikinta keyi dabatasan na me ba, he could feel heartbeat dinta, he could clearly see kwayan idanunta, this whole fadan nata is just an act! A mask! Hannunshi yakai ahankali kaman baiso yabude kofan still looking at her ya bude kofan tareda komawa seat nashi ya zauna bude idanunta tayi da sauri he was expecting tamai rashin kunya but saiyaga duk ta dimauce ta sauka da sauri kawai ta maida kofan tawuce ta shiga gidansu da sauri sai kawai ya girgiza kai yatada motan yawuce yabar anguwan.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 17

Tana shiga gıda Mamag tace “ke kuma an ina kika tsaya?” Ahankali tace “waje” kawai tashiga ciki zata kwaso kayan abinci dan daura girki Mama tace “kibar girki inada abincin da Riyad yakawomin har yanzu da zafinsu a kula shi zanci, kizo kije school daganan ki wuce aiki, Riyad yace kidawo” dasauri tafito daga dakin ta kalli Mama tace “Mama nifa yau na dauki permission bazanje school ba” saikuma ta taho ta zauna wajen Mama tace “Mama wai kinsan mutumin chan ne”? Mama na kallon kwayar idanunta tace “wani mutumin”? Cikeda mugun hali tace “shi wannan mutumin daya kawomu naga kunatayi kaman daman kunsan juna ne tun chan” dan murmushi kadan Mama tayi tace “a’a amman kawai zuciyata ya natsu dashi kaman na sanshi daga wani wuri, kema kinsan dawuya nake natsuwa da mutane amman shi kawai yayi fuce araina, mutumin arziki ne mutunci da dattaku, yanada halaye da dama nagari, bantaba gani a idanunshi yamin kallon mai wata cuta ba, gakuma yanda yabiya kudin asibiti akamin komi, wanda yamaka Akhairi kasoshi” ranta adan bace tace “Mama ni na tsaneshi” baki Mama tasaki tana kallonta ganin da gaske take, yunkurawa tayi tace “kuma konawa ya kashe miki a asibiti saina biyashi alkawari ne ko zanyi shekara dari ina neman kudin” dan dariya Mama tayi tace “zo ki juye abinciccikan ki wanke kulolin nidai fitina’u” wucewa tayi ta kwasa batai musu ba haka dai tai aikin komi Baba Liman ma yashigo gaida Mama wuraren 1 ta shirya ta tafi aikin sabida yanda Mama tace “saitaje” ga mamakinta ko kallon banza Madam bata mata ba hakama sauran ma’aikatan dudda bataga Hussy ba, kin zuwa office na Riyad tayi tadaiyi duka ayyukanta idan tana gaban desk aka kira ana neman cleaner a so so room ta taje, harta tashi by 6 bata ganshi ba bakaramin dadi tajiba ta tafi gida.

Washegari da sassafe ta tafi hospital nasu yau pediatric surgery departmant zasu to watch not to do itada team dinta zasu, direct tawuce inda suke ijiye bags nasu ta ijiye aka dan musu lectures kadan sannan tawuce tashiga shirye shiryen shiga surgery tsayawa tayi tana wanke hannunta wata tazo itama ta tsaya kusada ita tai murmushi tace “Hi” saikuma ta kalli Labcoat nata tace “Rashida I’m Maimuna but Maimoon ake cemin, tun ranan monday nake noticing naki, can we be friends pls”? Dan tsayawa Rashida tayi tana kallonta like a weirdo dasauri Maimoon tace “please” dan lumshe ido Rashida tayi yarinyar seems very cool and calm ahankali tace “I don’t know yanda ake friendship gaskiya” murmushi sosai Maimoon tamata tace “I know and I will teach you, let’s go” shiga cikin operation room din sukayi duk hannayensu a sama aka sassaka musu handglove ga yaron da za’ama operation din da baifi shekara biyar ba anyi sedating nashi shigowa surgeon din yayi wanda Babba ne bawai yaro ba aka samai nashi handglove din yawuce surgical table din student Doctors din dasuke su bakwai duk suka tsaya a gefe, Dr yace “yaron nan dake kan table din nan nada hydrocele wazai gayamin procedure da zanbi in this

surgery, and ya sunan surgery din”? Maimoon ce tafara daga hannu tabata amsa yace “wrong” almost dukansu saida suka bada amsa yace “wrong” yakalli Rashida dabatai magana ba dan ita bata show off ko a aji, yace “make attempt miss” dan ijiyan zuciya ta sauke Rashida confidently cikin turencinta that is good muryanta kuma makes it sweet a kunne tace “zamuyi Hydrocelectomy surgery to remove the hydrocele daga scrotum din, zamuyi making incision anan…..” tafara bayanin procedure din da sai kawai Dr ya tsaya yana kallonta exactly abinda zaiyi tafadi kaman ta tabayi, hannu yamikama head nurse yace “scalpel” samai wuka akayi a hannu yarike yadauki marker yamikama Rashida yace “come close” ahankali ta matso kusada surgeon din gabanta nadan faduwa yabata marker yace “draw the line” karba tayi ahankali taja, to her biggest shock yace “make the cut” dasauri ta kalleshi, confidently yace “I’m here you won’t make a mistake so go ahead” dan tsayawa tayi Dr yace “we all start ahaka, go for it, I’m right here ina kallonki” bismillah tayi ahankali ta karba tana kokarin kallon fuskan yaron yace “don’t look at his face” ijiyan zuciya ta sauke tareda rufe ido what is her biggest motivation da inspiration na son zama likita? Ahankali tace “Mama! I want to become the best Doctor for Mama! I want to make research nagano yanda ake curing HIV for Mama! I want to make Mama better, I want to be the best Dr in Nigeria da kewaye da al umma zasuyi alfahari dasun samu” daidainan tabude idanunta kawai tashiga cutting Dr na tsaye kusa da ita yace “suction” aka kwashe jinin, wasa wasa da shi da Rashida sukai surgery din nan tass yasake barinta tai stitching yaron up, her stitching style kadai saida ya kalleta almost 10yrs yana aiki in this surgery student Doctors daban daban interns but baitaba ganin skilled yar baiwan Dr like this girl ba ita kanta for now bama tasan wacece itaba imagine abinda take iyayi in year5, sallaman su yayi yakalli Rashida yace “makesure you become a surgeon Doctor R” dan sunnar da kanta tayi batare datai murnushi ba cus she hardly smile outside tawuce tafita Maimoon tabiyota tace “wowwww you are amazing Rash kai! I can never do that” ahankali tace “thanks” dasauri Maimoon tace “let’s go grab some drinks” wayanta Rash taciro daga jaka taga 2:30 tace “ohh no I have to go to work” taciro log book dinta da sauri tawuce taje aka mata signing tajuyo takalli Maimoon tace “gobe” bata jira amsanta ba tajuya dasauri Maimoon ta tsaya awajen tai shiru tana kallonta, tace “she’s unique, Bilal you loose a rare gem”. Wajajen 3 takai hotel din dan saida ta tsaya tai salla tana shiga tawuce changing room tafito kenan saiga Madam tace “yanzu ne lokacin zuwa aiki i will deduct 5k from salary naki” sauke kanta tayi kasa tawuce tashiga aiki thank God yau Friday gobe ba aikin, tass tagama aikace aikacen ta wuraren 5 Madam ta kirasu hall duk suka wuce, abinci tagani an kakkasa buhun shinkafa, jarkan mai, indomie, madara da milo sugar sai gero da taliya tace “kowa ya tafi da abincin azuminshi gida courtesy of Oga” sai murna ake, tunda tafara aiki dasu da Ramadan ana basu abinci last year an bata is not new thing amman saitakeji yanzu kaman karta dauka sabida Riyad but kuma idan bata dauka ba za’ayita surutu daman ance tanada girman kai, Madam tace “zansa security su taya kowa fita da nashi sai kuje ku kira keke, Happy Ramadan to everyone” ihu duk sukayi ana shouting thank you Ma sannan ta sallamesu wucewa

tayi ta chanza kaya ta goya jakanta tafito taje ta taho da keke tana zuwa security suka tayata lodawa abayan keken ta tafi.

Yau sunday tana so taje kasuwa tadan yo musu yan kananun cefenen azumi tunda batada aiki yau, atampa tasaka green shima ya kwana biyu tadau wani black hijabi ta daura asama mai hula ya tsaya mata a knee aiko yamata kyau tafito falo inda Mama ke zaune tana kirga kudinsu, zuwa tayi kusada Mama ta zauna Mama tace “yauwa kin shirya”? Gyadama Mama kai tayi, kudin da Mama takasa agabanta kashi biyu ta dauki me yawan tabata tace “ga wannan kudin dubu talatin ne nakine kisai dan atampa da takalmi da yan kayan kwalliya da turare kema kiyi kyau da salla kuka dawo sai akai dinki ko” dasauri ta maidama Mama kudin tace “Mama bana bukatan kayan salla, kayan danake dasu zan iya sawa da salla, Mama we have important things to do, drugs dinki, abinci, school fees dina dakuma kudin da mutumin chan ya kashe na asibiti ni sai na biyashi” kallonta Mama take tace “shiyace miki kibiyashi “? Girgizama Mama kai tayi tace “Mama you’re my responsibility ni kadai don’t others, banson wani ya taimakeni wajen kula da mahaifiyata, inda bekaiki asibitin masu kudin nan nasu ba dana iya biya amman yakama kaman an sashi ya kaiki asibitin kudi” tai maganan tana batarai tsayawa kawai Mama tayi tana kallonta tun Rashida na yarinya tanada wani irin kishi dasai ka san halinta ne zakasan kishine itafa batason kowa na raban Maman ta, yana daga cikin abinda yasa takejin haushin Riyad dakuma so tabiyashi kudinshi sabida yanda taga yana nan nan da ita bataso taga Mama na kula wasu with a smile, maida kudin kawai Mama tayi hannunta ta danne tace “listen to me umarni nabaki kisai kayan salla inaso nima naga yarinyana tayi kyau takuma fito da salla kinji” shiru tayi tana kallon Mama taki magana hade fuska Mama tayi tace “bazaki amsaba?” Ahankali tace “naji toh” dan murmushi tayi tabata 20k tace “wannan sai kiyo su cefene su maggi da nama da kayan miya tunda mun sami kayan abinci” gyadama Mama kai tayi ahankali ta tashi Mama tace “adawo lpy ki duba titi kafin ki tsallaka kinji” toh ta amsa tawuce tasa takalminta tafita abinta Mama tai murmushi.

Kusan 3hrs tabata a kasuwa, tasayo atampa mai kyau da gyale da takalmi tadansai bra da pant guda biyu sai pad dan tanaji cikinta na ciwo sannan tayo cefene tashigo keke tabar kasuwan.

Abakin titi aka saukesu hakan yasa ta dandaro cikin anguwansu da kafa, tun kafin takai gidansu ta hango wata arniyan karaman mota baka pake a kofar gidansu motan waye wannan? Hakan yasa ta kara sauri tana zuwa tabude kofar gidansu da sauri ta shiga saura kadan tayi karo da Riyad azaure yadan koma baya kadan tsayawa itama tayi gabanta kawai yafadi ta zubamai ido, yana sanye da wani milk soft yard dake kyalli yabi jikinshi kaman magic, kafanshi kafanshi sanye da Jordaan leather loafers brown, hannunshi daure da agogon Audemars Piguet, dayan

hannunshi rike da waya samsung galaxy fold, ba hula gashin kanshi ya kwanta yana sheki sai kamshi yake zubawa, dauke kai tayi da sauri daga kallonshi dan he’s so clean wlh ko datti ko stain ko tabo guda daya babu ajikin kayanshi, haka kayan a goge babu squeezing ko daya, shima tundaga kan kafafunta dake sanye dawani black takalmi flat da duk an dinke ya kalla dudda fararen kafanta are shinning ga long fararen nails na kafanta da babu lalli ko daya akai zuwa ataman dake jikinta da hijabin da ledoji biyun dake hannunta bakake data rike sannan yazubama fuskanta idanu she looks tired, she’s even sweating a goshi dan duk gashi ya kwanta a goshin nata, ga lips dinta sun bushe kaman she’s a bit sick. “Kallon fa”? Tai maganan cikeda rashin kunya dayasa ya daidaita kwayar idanunshi cikin nata dasauri ta janye idanunta hakanan taji takasa kallonshi but tsabagen karfin hali tace “kadena zuwa gidanmu banso” cikeda isa kaman anyi forcing nashi yayi maganan awulakance yace “are you angry ba wajenki nake zuwa ba”? Wani dum! Taji saukan maganan da sauri ta kalleshi tsaf shima yake kallonta mene mutumin nan yace? Mema ya dauketa? Taji haushi dan ba wajenta yake zuwa ba on wat ground? Kokarin hado martanin dazata bashi take dan she was a bit speechless but yarigata wani kallon raini yamata calmly yace “bakida matsayin dazan zo nemanki” yana maganan yabi ta gefenta yafice wlh takai 1 good minute fassara maganan shi take akanta taji ranta na kumfa dasauri tajuyo tafito kofar gida daidai yaja motanshi tabishi da kallo yana wani saka bakin glass a idanunshi ko inda take bai kallo ba yawuce abinshi kaman zata hadiye zuciya tamutu tace “nima ka isa kazo wajena ne aka gayamaka? Sai ji dakai kaman wani dan shugaban kasa sabida yana takama da dan hotel din dayake dashi I will leave your company soon zan nemi wani hotel din wlh kuwa” tana maganan tajuya tana saisaita bacin ranta takoma cikin gidan kaya tagani cikin gidansu harda su indomie da kwalin kwai kudan 5 crete gasu manta manyan roban madara Milo oat, wlh shopping data gani zube a compound yakai na 300k ga bandir na kudi kuma ijiye kasa na yan 1k guda biyu dasauri ta shiga ta tsaya gaban kayan ranta abace tace “Mama waya kawo mana abubuwan nan”?

Ahankali Mama tace “Riyad yakawo” kaman zata fashe sabida bacin rai tace “Mama shine zaki karba?” Kallonta Mama tayi tace “babu yanda banyi dashi ba amman yaki yarda wai ni mahaifiyar sa ce kodan darajan azumi na amsa, kinga uban kudin daya ijiye dane naki amsa da kyar na zari yasake daura daya, haka ya ijiye komi anan dan ni naki karba” cikeda bakin ciki harda abinda yamata a zaure tace “Mama shine baki kira yara kinsa sun maidamai da kayan mota ba”? Kaman wacce aka daka kawai saita fashe da kuka sosai ta ijiye kayan data shigo dasu daga kasuwa nan kasa ta tsallaka tashiga daki kawai tahau kuka idanunta sunyi jajir tashi Mama tayi tabiyota ciki cikeda damuwa tace “Rashida mekuma haka da kuka? Duk mai imani yadaga ido yaga rayuwanmu dole yaji tausayinmu, na karba badan komi ba saidai naga yaron kirki ne hakanan zuciyana ya natsu dashi kuma bawai saurayi bane ya gayamin yanada mata so mutum ne mai hankali ba yaro ba, saikuma dalili nabiyu shine karbansu zai saukaka miki kema at least daganan zuwa 2month zamu

manta da siyan Kayan abinci albashin dazaki samu saimu hada da wayan nan kudin ki biya kudin school fees ragowan mu rike na asibiti, you think I’m happy da rayuwan wahalan dakikeyi? Understand me it’s Ramadan kyaututuka haka is normal ko na yan anguwan man sabida baki karba ne da yanzu an kawo mana, it’s okay ya isa stop crying” Mama tajawota cikeda lallashi rabon datai kuka haka tun ranan da aka kwantar da ita a asibiti cikin kuka tace “Mama stop collecting abu daga hannun kowa, I’m enough for you, Mama bazan taba bari ki kwana da yunwa ba, I will never” hawaye taji yaciko idanunta saikuma tai murmushi ta danne takai hannunta ta share mata fuska tace “I know y’ata will never allow me to go hungry, natuba to bazan kara karban komi daga hannun kowa ba, Rashida na is enough for me, the best daughter aduk duniyan nan, come here” Mama kawai ta rungumeta tana murmushi she’s lucky Allah ya azurtata da y’a dake sonta haka, sun dade ahaka sannan Mama ta dagota takai hannu ta yaye hijabin jikinta ta tana taba wuyanta tace “jikinki da zafi baki da lafiya ne”? Ahankali tace “cikina ke ciwo kadan gobe naje asibiti zan karbi magani” cikeda so Mama tace “sannu kinji, zauna kihuta ni zan miki girki” dasauri tace “zanyi Mama” tashi zatayi Mama takama hannunta bawasa kan fuskanta tace “zauna kihuta” zama tayi Mama ta tashi atampanta tafara dubawa ta yaba sannan tashiga daura musu abinci itakuma anan bacci yayi awon gaba da ita.

Da kyar Mama ta tadata around 4 na asuba sabida suyi sahur, tariga tasan bata azumi wucewa tayi tama Mama abincin sahur sannan tawuce bayi yau da hot water tai wanka dan zazzabi takeji da ciwon mara but she feels she can manage dan is not that serious tana dawowa takaima Mama itama nata ruwan zafin tashigo daki tace “muje Mama” idanunta Mama ta kalla tace “dan Allah kina zuwa clinic kisha magana kar zazzabin nan yarufeki da kyau kinji” gyadamata kai tayi Mama tace “barshi zan iya zuwa bayin da kaina jeki kimtsa” batai musu ba ciki tawuce tashiga kimtsawa tasa black abaya tahada jakanta na baya saikuma ta kara kwanciya yawanci a rashin karfi ne kafi gane Rashida is sick dan baka ganewa a baki da fuska sabida masifa da fada, shigowa Mama tayi ganinta a kwance yasa Mama tace “namiki shayi”? Girgizama Mama kai tace “idan naje school zanci abinci Mama karki damu” da dan damuwa Mama tadauko mai tana shafawa hartai salla tana kwance wajen saima lumshe ido data farayi sai kawai Mama ta barta zuwa 7 ta tabata tace “tashi kitafi school” tashi tayi ganin Mama tafara damuwa yasa tace “laaaa Mama kinga najini garau maybe dama baccin danake ji yakara karamin zazzabi” 200k na jiya Mama takawo da 100k nasu tasa asama tabata tace “gashi ki biya kudin makaranta kisai yan littafan da baza’a rasa ba” kallon kudin tayi zatai magana Mama tace “ni Maman ki aka bama kudin nan, nikuma nabaki, kaman yanda Hajiyan nan taraba mana 20k a clinic naje na siyamiki crocs consider wannan kudin haka, go and pay school fees naki and buy textbooks dakike bukata” ayanda fuskanta kadai yayi kasan bataso ba but ganin yanda Mama tayi yasa tasa hannu ta karba kawai tasa kudin ajaka ta goya, taja black gyale tashiga rolling tai kyau

kaman balarabiya dudda bakomi akan fuskanta sannan tace “Mama natafi” 5k takara cirowa cikin kudinsu dabaifi 50k ba Mama tabata tace “dan Allah kihau keke yau, kici abinci mai kyau a school kinji” gyadama Mama kai tayi tace “natafi Mama thank you” “adawo lpy Allah bada sa’a” fita tayi tana kaiwa junction ta shiga cafe tai printing ramita, sannan tafito tashiga keke sai bank taje tafara biyan school fees nata sannan tafito tashiga keke again sai asibitin su, sauka tayi wuraren 9:30 taga student nasu Maimoon na hangota ta taho wajenta dagudu tace “anyi releasing namu yau, kaman za’ayi manyan baki ne dai ance mu student mutafi wlh” ahankali tace “really, bari na karbi magani to natafi” dasauri Maimoon tace “meke damunki”? Dan yatsine fuska tayi tana tafiya tace “I think I’m coming down with Maleria saikuma cramps” Maimoon tace “oh no sorry” office nasu tashiga tabude locker ana ijiye musu magani haka tadauki na Maleria da cramps suka fito yawance Maimoon ke hiran, ahankali tace “I want to buy food da water dazansha magani dashi” dasauri Maimoon tace “muje cafeteria” Jellof rice tasaya da beef 800, tasai ruwa daya ganin tana bude jaka yasa Maimoon tace “mu zauna anan kici mana” girgiza kai tayi tace “kema kawai na gayamiki ne only Mama na ke sani idan bana azumi I don’t want people knowing kunya yake sani” dan murmushi Maimoon tayi tana kallonta yanda take arranging abincin ajaka tana maganan she looks so cute and adorable maida jakan bayanta tayi ta goya tace “bari naje to sai gobe” Gyadamata Kai Maimoon tayi suka fito tana kaiwa titi tashiga keke, is just around 10 yanzu gwara ta tafi hotel tamusu aiki saita sami free evening har gaban hotel din aka kaita ta sauka tabiya kudi tashiga ciki, direct changing room nasu taje, saida tafara chanza kaya sannan tadan fito ganin kowa na aikinshi yan morning sun riga sunzo tun dazu so kafin wani yadawo dakin nan cikinsu kuma probably sai idan yan afternoon sunzo kuma, hakan yasa tadawo ta maida kofan tarufe batare data saka sakata ba takoma ta zauna taciro rice daga bag da water dakuma maganinta ta ijiye kan long bench dake wajen itama ta sauna ahankali sannan ta dauki abincin tabude tasa spoon tafara ci ahankali bayamata dadi ma abincin sabida zazzabi.

Ahankali yake tafiya da shi da Munir dawasu ma’aikata guda biyu dake biyedashi abaya, akwai some changes dayakeso ayi abinda ma yakawo shi hotel din kenan this morning, duk ya gama nuna musu saura changing room na ma’aikatan shi corridor suka shigo suna biyeda shi yasa hannu yabude kofan yasakai ciki yana magana yace “the lockers nakes…….” Shiru yayi ganin yanda Rashida tawani yarda takeaway jellof rice din da ruwan yashiga tittila akasa ta tashi tsaye da sauri daidai su Munir zasu biyoshi su shigo ciki yace “wait!” Duk kallonshi sukayi suna tsaye bakin kofan batare da sun shigo ba strictly yace “kuje lobby” yanayinshi kawai yasa Munir yace “okay” yajuya ma’aikatan ma suka bishi yajuyo yazuba mata ido tana kallonshi cikeda fada baki tabude zatai magana dan akwai abinci abakinta sai kawai tai wani wawan kwarewa sai tari, maida kofan yayi yarufe ya kalleta ganin yanda take tari kaman zata mutu yasa gently yaduka yadauki bottle water nata daya fadi yadan zube yamike tsaye yasake kallonta tsabagen tarin datakeyi tama kasa

tsayuwa ta tsugunna idanunta sunyi jajir ga rice guda daya fito daga hancinta alamun ba karamin kwarewa tayi ba, dasauri yataka zuwa inda take ahankali ya tsugunna yamika mata bottle water batare dayayi magana ba yana kallon fuskanta, tsabagen azaba sabida ga yaji a abinci ga kearewa mai kyau batasan lokacin data daura duka hannayenta biyu saman kan nashi ba takama both hannunshi da goran takai bakinta hakanan jiyayi jinin jikinshi ya tsaya chak jin saukan hannayenta biyu kan nashi, ahankali yadaura idanunshi kan hannunta dake saman nashi sannan yakai idanunshi kan fuskanta da yanda takeshan ruwan kaman yaki, tass ta shanye ruwan sannan tacire bakinta daga goran har lokacin tana rikeda hannunshi dabatasan tayiba tana sauke ijiyan zuciya kaman wacce tagudo daga hanyan mutuwa idanunta sunyi jaa, kusan 1min tayi tana sauke ijiyan zuciya sannan ahankali kaman mara gaskiya tadan dago kanta tadaura idanunta akan nashi yanda yake duke dab da ita kamshin turarenshi ya bade wajen da sauri ta maida idanunta kasa still bata sakeshi ba, yana kallon fuskanta baya ko kyafta ido yace “can you let go off my hand now”? Dawani irin sauri ta kalleshi saikuma ta kalli goran ruwan data rike ganin yanda ta kama hannunshi da duka hannuwanta biyu saida taji kaman ta kurma ihu sabida kunya dawani irin sauri tasakeshi hakan yasa ya mike tsaye ya kalli magungunan ta dake kan bench na wajen sannan yawuce kofa haryasa hannu yabude kofan ya tsaya batare daya juyoba yace “kifito amaidaki gida, kafin ki mutu in my building” dasauri ta kalleshi kaman wata damusa dan juyo da kanshi yayi but bai kalleta ba yace “take days off when you feel better you can resume” yasa kafa yafita saikuma ya tsaya yace “someone will clean the place you don’t have to, kifito akaiki gida!” Yana maganan yawuce yafita takai almost 2min aduke a inda yabarta saikuma ta daga hannuwanta ta kalla yanda tarikeshi saikawai taji kunya da haushin kanta sai abin yasa taji mugun zazzabi ya rufeta tanama jin sanyi, ahankali ta lallaba ta mike tadauki jakanta ta goya abaya batare data chanza uniform nata ta maida abayanta ba kafin wani ya sake shigowa yaganta tana chanza kaya she will not take the risk, tadauki magungunanta tarike a hannu tafito tana tafiya ahankali hakanan kawai sanyi taji tanaji barinma a hannuwanta dasuke abude dan uniform nasu short hands ne, gashi small farin baby hijab ne jikinta that covers her chest only, ahankali take tafiya is as if every step datai taking yana kara mata zazzabi harta fito lobby kadan kadan take tafita tana jin sanyi kaman akwai kankara awajen, hakan yasa bakinta yahau kakkarwa irin na me jin sanyi din nan kaman an sata a cold room, idanunta na rawa rawa suna kukkullewa kadan kadan take bude idanunta tasan ta hango mutane zazzaune da suit a lobby daganan kuma batasan meya sake faruwa ba dipp kaman an dauke wuta ta zube awajen.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 18

Ahankali take bude idanunta dataji sun mata nauyi sosai kafin tagama budesu da kyar tazubasu asaman dakin sake lumshe idanun tayi tabudesu taga drip na ruwa hakan yasa tabi dakin da kallo da kyau, idanunta ne suka sauka kan Riyad dake zaune kan wata kujera mai kyau one seater, wannan karan babu jacket na suit ajikinshi just white shirt da trouser hannunshi rike da wani file yabude yana karantawa ga pen a hannunshi, faduwa gabanta yafarayi kadan kadan hannunta daya ta daga taga anyi fixing drip hakan yasa ta daga dayan hannun takai saman fuskanta sabida iska dataji yana shiganta da kyau jitayi babu hijabinta kan fusnanta babu dan kwali asaman kanta, hannunta takai saman wuyanta zuwa saman riganta taji an bude boturan saman riganta har zuwa wajen bra Allah yasa tasaka singlet sauke hannun tayi kasa tacikin bargo taji an daga riganta da vex din sama cikinta abude ga hook na wandonta an bude ahaukace ta tashi zaune tawani fincike drip din da aka samata taja bargon sama tana kare kirjinta tai wani irin ihuuu tace “mekamini”? Sauke file din dayake rikedashi yana karantawa yayi kan coffee table dake gabanshi yakalleta tareda sauke soft boyayyen ijiyan zuciya, yazuba mata mayun idanunshi daidai lokacin tufkin gashinta ya warware black silky hair nata yawani irin zubo half ta face nata ragowan ta baya abun just grip his attention dayasa yawani zuba mata idanu kaman tsohon maye kaman akwai wani abu dayake kallo ajikinta, ihu Rashida tayi sosai taja bargon tarufe har wuyanta tace “you pervert Allah ya isa ban yafemaka ba wlh mugu azzalumi kaci amanata ta, wat have you done to me? Dame kai drugging dina? Wani substance kasa aruwan daka bani, sabida kaga kanada kudi idan kasaba yima yan mata haka ana kyaleka wlh akaina you’ve messed with the wrong person bazan taba kyale wanda ya batamin rayuwana ba” gashi takasa tashi sabida yanda aka kwance hook na wandonta daidai lokacin taji an bude kofa dasauri tajuyo idanunta sunyi jazur wata mata tagani very elderly zatakai 45 tafito daga bathroom na dakin rikeda bowl a hannunta tace “young Lady calm down” ta taho wajen da sauri tana ijiye bowl din da Rashida tabi da kallo taga ruwa ne da karamin towel aciki tace “calm down no one did anything you’re sick, your fainted and Mr Riyad called, my name is Dr Amara Kennedy, I’m this hotel’s Doctor, incase of any emergency or anything ni ake kira” tadan sauke ijiyan zuciya tazauna bakin gadon tace “calm down, I came in immediately an kirani, you were running serious temperature dayasa kikai passing out kina convulsing this is the result of your blood test” tai maganan tana mika hannu ta dauki wata paper dake saman drawer gadon hakan yasa itama Rashida da gabanta ke faduwa sosai ta kalli wajen, taga allurai da magunguna daukan takardan tayi tamika mata tace “take a look” matse bargon tayi da wuyanta tasa hannunta dake rawa har lokacin ta karbi takardan tashiga dubawa Dr tace “kinada high typhoid da Maleria, namiki allurai so I got water ina shafa miki ajiki just to get temperature nata to cool down and for Mr Riyad dakika gani he just came in not less than a minute ago yadubaki saina tashi nima after I cover you up naje bathroom dan na zubar da ruwan and get another one” ji tayi hankalinta ya wani irin kwanta saikuma taji kunyan abubuwan data gama fadi, gashi ta gama zage zage kasa kallon wajen dayake tayi ta kalli Dr ahankali tace “I want to go home” Dr tace “I think Mr Riyad arrange driver that will take you home, but I think you need to

change sabida” tanuna mata kafanta da idanu tashi Riyad yayi yajuya yafita daga dakin yace “ku sameni awaje” lumshe idanu tayi jin muryanshi tana kara mugun jin kunyan wat she just did.

Da taimakon Dr ta tashi bayi ta kaita bayan ta dauki gown nata dake jaka she change, kayan kuma ta kulla a Leda tasa ajaka takai gida ta wanke she is feeling better yanzu tareda Dr suka fito waje yana tsaye jikin mota shida Munir suna magana yayi shiru hangosu dayayi har saida Munir yajuyo dan ganin meyake kallo kin karasawa wajen motan tayi tace “I will take keke” kafin Dr tayi magana tayi gate da saurinta tafice duk yana tsaye awajen yana kallonta ta tare keke ta shiga sai kawai yabude bayan motan ya shiga ya zauna Munir kuma yadanyi magana da Dr ya sallameta sannan yadawo ya shiga yaja motan sundanyi nisa kadan Munir yace “in tambayeka mana Riyad?” Dago kanshi Riyad yayi ya kalleshi batare daya bashi amsaba alamun yana jinshi, Munir yace “why do you give that girl special attention?” Shiru yayi yadauke kanshi ya maida kofa yana kallo sai chan yace “do i?” Munir yace “yes on different occasion” wayanshi yaciro daga aljihun gaban riganshi ya shiga dannawa yace “I had no idea” shiru Munir yayi yace “before you hardly come to the hotel cus I always handle it, office kafi zuwa but tun randa ka ganta anan hotel yazama shine latest head office namu, look at dazu when she fainted you took off jacket naka ka rufamata and just picked her up ka kaita sama kahau kiran Dr without assigning me to do that, not to mention dat day datama yarinya duka normal you dakayi sacking nata but bakayiba, saikai sacking wacce akama duka, are you perhaps interested in her? Cus this is beyond she saved my life” Chak ya tsayan da danna wayan dayakeyi ya tsare screen din da ido kawai that moment na dazu na gashinta na zubowa nadawo mishi rabon dayaga breath taking view haka harya manta sai yau, dan fuzar da iska yayi yasa hannu yasauke glass na motan kasa ahankali yace “I’m not interested in her I just find the girl fascinating! She’s a topic!” dan murmushi kadan Munir yasaki yace “okay oo, but wat do you mean by she’s a topic”? Wannan karan shiru Riyad yayi yafi nada chan yace “she’s a topic in my heart that I just feel obligated to study” Riyad ma dan rainin wayone Munir yafadi a zuciya jin yanda yake using english yana sugarcoating the word affection dayake developing for the girl but woo idan tai tsami za’aji ai hakan yasa yace “uhmm topic indeed!”.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 19

Har kofar gidansu me keke yasauketa tasauka tabiya kudi ta shiga gida, anriga anyi magrib Mama na ganinta tabar kunun datakesha ta taso dasauri tace “yaya jikin

ne?” Kin fadama Mama ta suma tayi sabida karta tsorata tace “Mama naji sauki wlh har allura an mini, kinsha ruwa lpy” zaunar da ita Mama tayi tasamata kunu karba tayi tashiga sha still bata da karfi Mama bata wani bari tai aiki ba wanka kawai tabarta tayi tana shiga daki ta kwanta ko kaya bata saka ba sai bacci washe garin ranan ma ko school bata iya taje ba, bini bini taita tuna abinda tayi tanajin kunya.

Sai jibi ta tashi garau taje school tadawo dayake tagayama Mama a bata off a aiki bataje ba.

Azumi biyar tasha arana na 6 ranan day 7 taje hotel din sai addu’a take karsu hadu cikin ikon Allah bata ganshi ba har azumi yayi nisa basu kara haduwa ba taji sosai dataji wasu ma’aikatansu na cewa Oga umara yaje saisa tunda aka fara azumi baya zuwa itadai ko ajikinta.

Yau saturday morning taje aiki around 2 ta tashi ta shirya ta goya jakanta abaya yau daman hijabi tasaka tunda aka fara ramadan hijabi take sawa hakanan kawai taji kirjinta nata bugawa tana tuna Mama hakan yasa tana shiga keke taciro yar vivo nata ajaka tai dailing number Mama amman harta katse bata dagaba that is so unlike Mama, sake kira tayi shima shiru hakan yasa ta shiga damuwa ko zazzabin Mama yatashi ne?

Abakin junction ta sauka tashigo layin su da kafa tun kafin takai gida ta hango manya manyan motoci guda biyu agaban gidan saikuma taga yaran layi an taru a kofar gidansu some nata fitowa da biscuit da taliya guda guda a hannunsu yanda taji zuciyanta na tafarfasa har sarkakewa numfashinta yake da sauri ta kutsa cikin yaran ta shiga cikin gidan wata babban mace ce tsaye tsakar gidan taci uban lace da duwatsun lace din har kashe ido suke tarike wani arnen jaka a hannunta akalla zatai 45-48yrs gawasu mata haka wanda kana gani ma’aikatan ta ne sun rike kwalin taliya a hannu datake rabama yara ga wani buhun local rice akasan tsakar gidan an yatsar da karamin man gyada a jarka, Mama takalla dake zaune kan tabarma sanye da hijabi abinta duk yanayinta yayi wani irin alamun she’s not happy ganin Rashida yasa tai maza ta gyara fuskanta tace “kin dawo yarinya na”? Daidai lokacin matan ta dago kanta ta zubama Rashida wani kallo, da sauri Rashida tai wajen Mamanta cikeda tsananin so takai hannunta ta taba fuskan Mama tace “Mama did you cry? Sun miki wani abune? Mesa baki kirani ba”? Tai maganan tana daga hijabin Mama tana duba jikinta da hannayenta cikeda so.

Matar dake tsaye tana kallonsu, tawani bushe da dariya tace “akanme zan daki me kanjamau banda yarinta irin naki”? Dasauri Rashida tajuyo da kanta ta kalli matar zatai magana Mama tajuyo da ita yace “tashi mushiga ciki tunda kindawo abincin zakka takawo mana nace mata karta damu mun gode, muje ciki idan tagama rabo saita tafi” Rashida zatai magana matan tace “ke har kinyi darajan korana daga gidanki wulakantacciya irinki me bin maza da aurenta nasunna” zabura Rashida tayi ta tashi Mama ta taso dasauri takama hannunta tace “ke zonan muje daki” wani irin

dariya matan tayi tace “naga alama baki bata tarbiya ba saki hannunta dan Allah zan bata tarbiya ni” kama Rashida Mama tayi takomar da ita bayanta tahade hannayenta tace “Hajiya Jummai na rokeki da girman Allah kifitan mini daga gidana stop provoking my daughter, banson hayaniya dan girman Allah kitafi” kallon idanun Rashida tayi yanda take kallonta kaman zata kasheta da idanu to be honest sabida Rashida tazo, Mama batada karfin bala’i kuma banda haka tasan babu abinda Zainab keso aduniya irin yarta Rashida saiso yanzu burinta shine ta nakasa diyar tata itama ta lalata mata rayuwa, da gangan matan ta kalli yaran dasuka cika gidan tace “ku nuna matar nan kuce ke tsohuwar banza me HIV” aiko yaran suka kalli Mama sukace “ke tsohuwar ban…….” Wani fincike kanta da Rashida tayi daga hannun Mama ta taho wlh watsewa yaran nan sukayi dan ansan halinta suka fice daga gidan dagudu, kaman zakanya tawani tsaya agaban matan tanuna mata hanyar zaure tace “ke Jummai fita daga gidan nan tunda bana mijinki bane before I loose my temper” dasauri Mama tazo takama hannun Rashida tace “ke muje” cikeda masifa Rashida tace “Mama ki banni lemme put this useless woman in her place babban banza kawai yar wahala” fizgota ama tayi cikin fushi tace “stop insulting elders” itama Rashida cikin fushi tace “Mama she’s not an elder, waye ita dazata shigo gidanmu ta zageki enough! Yanzu ba da bane, I will protect you Mama, Madam ki fita daga gidan nan and take this trash dakika kawo away we have morethan enough” tafarfasa zuciyan Jummai yake kaman ta chakamata wuka takeji ta nuna kanta tace “ni kika zaga”? Rashida tace “akwai wata kalanki anan ne?” Kallon yan matan dake tare da ita tayi tace “kuma ita da uwarta duka” kambu! Rashida jitayi jikinta yakama da wuta rike ta Mama tayi tasan halinta tace “muje ciki mu rufe kofa Rashida don’t fight them” ganin yan matan biyu sunyo kansu yasa tawani kama Mama ta maida bayanda daidai sunzo suka kakkawo mata duka dunkule hannu tayi ta zubamusu nushi aciki duk sukai ihu kafin tafara dambe dasu sai kawai Mama ta shiga kuka ganin yanda su biyu suka tarunma yarta dudda Rashida nacin ubansu cikin kuka Mama tai gaban Hajiya Jummai tahada hannunta tace “Hajiya Jummai na rokeki da Allah kiyakuri kifita daga rayuwan mu shekaru ashrin da uku munyi zaman kishiyoyi narabu da mijinki tun kafin na haiho Rashida, narabu ashi ko amafarki kinsan bazai kara aurena ba takuran nan ne menene eh?” Daidai lokacin jikake kum kum kum Rashida ta barar dasu duk sun daki bango sun zuzxube kasa a sume goshinsu na jini daga Mama har Hajiya Jumai ihu sukayi Mama tace “Innalillahi wa innailaihi raji’un Rashida me kikeyi”?Mama tai wajen da gudu hankalinta atashe tana tattabasu itakuma Haj Jumai tashiga ciro waya daga jaka tace “shikenan ta kashemin bayi, yarki is a killer she’s a murderer wayyooo jama’a ku taimakeni sun kashemi yan aiki daga mun kawo musu abincin taimako” Jumai tafice waje da gudu tana ihu tana making call before you know it yara da manya an shigo gidansu maza sukai kan matan ana dagosu amman ko motsi basuyi Jumai tashiga nuna Rashida dake tsaye a gefe tace “wlh yau idan Police basu rabamu ba sai nasa kema an kasheki kokuma nakashe uwarki” takama Mama zata kai mari wani irin damke hannunta da Rashida tayi ta murda saida tahau ihuuu bana wasaba mazan duk sun kasa tabata sabida tsoron Rashida itakuma tana ihu Mama najan Rashida amman bataji zuciya yakaimata wuya idanunta sunyi jaaa tace “you keep

hurting my Mom tun kafin a haifeni I’m ready to kill you today to die Mama na tahuta” kawai takai hannunta dayan takama wuyanta ta matse gam daidai lokacin saita yar sanda macen dake tare da yan sandan tawani rapkama Rashida kulki a baya hakan yasa tasaketa Mama tafashe da kuka ganin yanda aka rafkama yarta kulku itakuma Jumai da gangan tazube tana haki tace “officer she’s a murderer daga zuwa basu abinci munga mabukata ne shikenan, macen police din tashiga sama hannun Rashidan ankwa tace “you’re under arrest for attempt murder na Hajiya Jummai” sauran yan sandan suka shiga duba sauran sukace sunada rai but they need hospital, kutafi da me laifin” fashewa da kuka sosai Mama tayi tai kneeling tace “dan Allah kuyakuri laifinane niku tafi dani not my daughter she’s a small girl ko aure batayiba dan Allah karku kullemini diya dan Allah” cikin zuciya Rashida tace “Mama stop begging kowa babu Allah cikinsu kitashi Mama, babu wanda ya isa yamin wani abu anan Mama kitashi” macen police din tace “au haka kikace? Kinyi laifi still kina rashin kunya kina taurin kai”? Cikeda dakewa Rashida tace “laifin me nayi kin tambayeni mesukayi min su? Ko nima bakiga jikina da ciwo ba ne it was self defense, kuma garau suke sabida Ogan su tace karsu farfado ne sukai kaman suma I’m a doctor I know idan mutum is unconscious, dukanku are corrupt officers working for this evil woman!” Tassss!! Yar sandan ta dauke Rashida da mari da saida tai tangal tangal zata fadi Mama ta tashi da gudu tai ihuuuu tana tare Rashida, Jumai tai wani murmushi kaman an mata busharan aljanna, tarota da Mama tayi yasa bata fadi ba ta kalli yar sandan da idanunta dasukai jazur kaman zata daketa babu ko alamun hawaye, yar sandan tace “ke me taurin kaiko? Zan gyaramiki zama muje police station wlh saikinyi dana sanin abinda kikayi dahar yasa na kaiki police station” kallon Rank dinta Rashida tayi tace “yar wahala saisa har yau bakikai any matakiba, corrupt evil woman” zata kara kaimata mari dayan dan sandan yace “stop let’s go to police station tarubuta statement, let’s go” wani irin finciketa yar sandan tayi daga hannun Mama sukai gaba da ita Mama tabisu da gudu, yanda suka wurgata bayan motan kaman wacce aka kama da bomb suka ja motan Mama na gudu tana binsu harsaida ta fadi akasa duk Rashida na kallo idanunta sunyi kamar jini ganin yanda mahaifiyarta ke wahala all because of this family gidan Sarautan nan, she hates that house da kowa naciki, duk randa tazama wani abu she will ruin them, they will pay for abinda sukama mahaifiyarta, this woman tazo har gidansu ta wulakanta mata mahaifiya duk all because of kishin jakin mijinta Alhaji Mujitapa Baba Ali! Give Rashida few years! I will come for dukanku! I will ruin all of you and gabaki dayan gidan sarautan saina tarwatsashi!!!.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 20

Mama na duke a tsakiyan anguwa tana kuka sosai ana kallonta an taru Hajiya Jummai tazo inda take tsugunnawa tayi takai bakinta saitin kunnen Mama tace “mission accomplished! Now watch how I will ruin rayuwar yarki this is just the 1st step, watch and see how zanyi feeding yarki to those hungry police officers, I will make sure sunyi kacha kacha da duk wani abu daya maidata diya mace, barima kiji Amarya na aikamusu yau akwai biki” tawani kwashe da dariya, juyo da kanta Mama tayi ta kalleta irin kallon nan na bakomi akwai Allah sannan tace “nabaki raina ki dauka Jummai, yau kidauki wuka ki sakamin aciki na mutu na yarda, kome kikeso kiyi dani kiyi amman spare yarinya na, she’s a small girl, meta miki? Mijinki dama tun tana ciki yace ba tasa bace haryau ko fuskanta baitaba ganiba to meta miki? She’s not a threat, she’s a small child kulleta a police station will ruin her life, Hajiya Jummai banda kowa sai ita, kiyafema Rashida ni kisa a kulleni” murmushi tayi tace “kinga I hate you with every blood na jikina saisa I want to end you using abinda kikafi komi so, wlh wlh ko kudina zasu kare yau saina tabbatar an yaga yarki a cell, wlh sainasa sun maidata nama, saina tabbatar sun halakar da rayuwanta tass, maybe then na hakura nasa afito da ita kokuma na aikata prison she need to be taught a lesson, ke I will cook her up bazata fito daga cell anytime soon ba, this is for auren Mijina dakikayi!” Tana maganan ta tashi tawuce wajen mota ahankali Mama tajuyo da rinannun idanunta ta kalleta ga mamakin Mama saitaga yan matan sun taso fess da kafansu sun fito sun shiga mota direba sun yatada motan sun tafi, Ahankali Mama ta tashi wani kalan bubbugawa zuciyanta keyi dabai taba mata arayuwanta ba, yan layin sai kallonta suke mata an lalleko daga gida tanaji ana kananun magana ana dama maraji makomarsa kenan anzo baku abinci mu makota mun shaida but yarki tazo tana dukan mutanen arziki ai gashinan tahadu da daidai da ita, gida Mama ta shiga ta tattaro duka kudin dasuke dashi tasan belin mutum da kudi akeyi sunada 80k agida a account din Rashida kuma akwai 100k da aka mata salary na hotel just jiya 50k ake biyanta but sallan nan sai aka basu 100k, sakawa tayi a lalita tasa takalmi tafito ta kulle gidan ta shiga tafiya bama tasan wani police station aka kaita ba, tafiya take a anguwa wasu nacemata Allah kiyaye gaba wasu na Binta da kallo Adamu me chemist ne yafito hangota dayayi dan shi yana mutunci dasu yace “Mama Allah kiyaye gaba ina zaki yanzu”? Bama ta iya magana sai hawaye bakin hijabinta tasa tace “bansani ba duk police station dana gani zan shiga” dasauri yace “ina ganin kije head quarter dan naga babban police car suka zo dashi sabida local street police post ba’a ijiye musu manyan motoci haka, Allah kiyaye gaba” gyadamai kai tayi ta wuce ta tare keke ta shiga 500 aka kaita headquarters.

Sauka tayi tashiga ciki ta tafi chan gaban kanta yan sanda dake wajen sukace “lafiya Hajiya” baki Mama tabude zatai magana sai kuka matar tace “Hajiya dan Allah kifita ki gama kukan saiki dawo” dasauri dayan dan sandan yace “mehaka Grace? Mama lafiya calm down meya faru fadamana”? Da kyar ta tsagaita kukan tace “y’ata wasu yan sanda suka kama kusan minti talatin kenan bansan inda aka kaitaba yan anguwan mu since nazo nan headquarter” mutumin yace “ya sunan diyar taki”? Ahankali tace “Rashida Almustapha” log book dake gabansu yaduba

yaga sunanta kafin yayi magana Grace tace “banan aka kawota ba kije wani police station din” kallon Matan Mama tayi saikuma ta kalli wanda ke attending to her ahankali yace “Mama je waje ki zauna ina zuwa” fita waje Mama tayi tasami waje ta zauna, kirjinta bugawa yake like never before ga azumi abakinta wlh kusan 2hrs tai spending awajen dan har 5 tayi sannan yafito yazo wajenta yace “zo gefe Mama” Dasauri Mama tabishi ahankali yace “Mama bansanki ba amman kin bani tausayi wlh tuntuni sai bin office daban daban nake ama barki kiga diyarki sunki, wai yaran data daka suna ICU, sannan she attacked officer mu wata and abuse her” cikeda tashin hankali Mama tace “wlh wlh karyane sherine agabana yaran suna shiga mota da kafansu basa ICU, kuma wlh Rashida bata taba police dinba” ahankali yace “to yanzu dai bani dubu goma zan taimakeki da kyau koda yarki zata kwana zansa ido akanta kar acutar da ita” fashewa da kuka Mama tayi tana tura hannu alalita ta kirgo 10k tabashi ya karba yace “bari kiji Mama the truth is powerful mutane sukasa aka kulle miki yarinya dan haka yanzu dai idan kinada wani babba haka kije kitaho dashi ko za’a miki alfarma abaki belinta inba hakaba wlh bazama kisan yarki na nan ba ninedai nafada miki” yanda Mama ke kuka sai yataba zuciyanka tace “wanake dashi? Banda kowa sai Allah ni” dan sandan yace “nidai nayi miki iya nawa kije ko waye kisamo, suna ganin kalan kudi ajikinsa zasu badata, bari nakoma ciki kada anemeni” wucewa yayi yakoma ciki yabar Mama wajen tsaye shiru Mama tayi saikuma ta daga idanunta takalli sama irin kallon Ya Allah kana ganin komeke faruwa sannan tasa bakin hijabinta tashiga tafiya tawuce gate kafanta yayi butu butu da hijabinta ma sabida zaman kasa datayi sai tunani take ina zata shagon Mama miwa tane tunda tanada kudi but tace baruwanta da police station bata zuwa, Rashida tafada mata tace taji ance Riyad na Umara saisa batai tunaninsa ba.

Bari taje ta gwada yima manager magana kozata taimaketa gashi Baba Liman yaje kauyensu shima duba gona, adaidaita tasake shiga ta tafi hotel din hanyar shiga taje yauma wasu security daban ne dana ranan suna ganinta sukace “ina zaki”? Arude Mama tace “manager zan gani” wani kallo suka mata daga sama har kasa sannan sukace jira anan daya yashiga ciki yama manager magana tafito daga office nata hango Mama tayi daga glass door tace “I don’t know her, please send her away yau banda lokacin all this beggars I’m very busy” takoma office security yafita yaje inda Mama take tsaye yace “batanan” tsayawa Mama tayi tana kallonshi yanda taji kaman jiri na neman dibanta batasan sanda ta duka ba saitahau kiran sunan Allah. “Allahumma ajirni fi musibati……Innalillahi wa innailaihi raji’un, Ya Allah kadubi yarinyana dake cikin cell kar awani abu yasameta please karsu cimma burinsu” tashi tayi tana taba bango kawai kaman kanta ya kwance takeji cus batada hope kuma yanzu sai magana take ita kadai. “Rashida na is scared, yarinyana bata taba zuwa police station bama, yanzu tanachan locked up a cell an ciremata slippers, an karbe komi nata, hala ana azabtar da itama, idan suka batama mata rayuwa fa, wat if they rape her? My poor baby must be so scared yanzu, yarinyana batada kowa aduniya sai ni, wat are they doing to my child right now…….”

Diiiiiiiiiiiii! Taji karan ana daddanna mata car horn dayasa kawai ta birkice hannunuwanta tadaura saman kunne ta kulle idanunta kawai tahau juwajuwa akan titi go slow kawai yahadu bama tasan meke faruwa ba, “Mamaa!” Taji an kira sunanta da karfi dasauri tabude idanunta dasukai jazur, Riyad tagani tsaye agabanta yana sanye da farin shadda datasha aiki kanshi da kula ganinshi kawai saita fashe da kuka sosai ahankali yasa hannunshi yasauke hannayenta daga saman kunne ganin she’s not herself yakama hannuwanta duka biyun sukabar tsakiyan titi zuwa motanshi yabude baya yasata shima yashiga bayan wani bodyguard dake tukanshi yaja motan suka gangara gefen hanya yayi parking, Riyad dake kallonta yace “Mama menene? Why are you in the middle of road”? Bakinta rawa yake ta birkice kawai tace “Riyad…….Riyad…….Riyad” hannunta yakama ahankali yace “get me water” fita direban yayi anatse Riyad yace “Mama calm down I’m here now, calm down everything will be fine, calm down Mama kinji” bakinta is still calling name nashi, ahankali yace kice “Innalillahi Wa Innailaihi Raji’un” ahankali Mama tace “Innalillahi wa innailaihi raji’un” dan natsuwa tasamu kadan daidai lokacin an kawo ruwan budewa yayi yabata tasha kadan sannan yace “wat happen Mama”? Fashewa da kuka tayi tace “tasa an kamamin yarinya an kulle a police station” anatse yace “wace”? “Kishiyata wacce mukai zaman aure tare kafin mijinmu ya koreni”? “Wat happened Mama”? Labari Mama tabashi tundaga time datazo gidan da time da Rashida ta shigo, da all abinda yafaru da duka abinda tagayama Mama na zatai feeding Rashida to yan sanda” jiyayi ranshi yayi tsananin baci, “drive” yafadi ahankali yama Munir text dan daga gidansu zuwa head quarter is even closer than daga nan hotel zuwa wajen.

Wajajen magrib sukakai police headquarter ya kalli Mama yace “Mama ki zauna anan zan fito da ita kinji” gyadamai kai Mama tayi ya kalli security yace “make sure she stays in the car she’s not feeling well” “yes sir” ya amsa yana fita yaga Munir yafito daga tashi motar ga sauran bodyguard nashi yayi gaba kawai Munir da guards nashi na binshi abaya, all eyes yadawo on them ko kallon yan sandan wajen baiyiba yawuce sama direct zuwa office na inspector cus yasanshi sosai yana kawo gaisuwa fada dudda bai sanshi babu rawani ba, kai tsaye yabude kofan ba knocking babu komi Inspector na zaune yana dube duba, da zafi sosai an anger kan muryan Riyad yace “I will sue you and I will sue the entire police headquarters for rashin adalci for tauye hakkin talaka, for rashin yin investigation, I will make sure anyi sacking all of you anyi replacing naku with better and eloquent officers dasuka shirya yin aikinsu yanda yakamata” from yanda yake magana kadai yasa gaban Inspector yashiga faduwa yama kasa magana, Munir yace “you must be confuse kana magana da Mai Martaba SARKI RIYAD! Sarki mai adalci, sarkin talakawa” wani kalan tashi inspector yace “an gaida Mai Martaba Allah huci zuciya ka, tub……” hannu Riyad yadagamai yace “release Miss Rashida Almustapha, and nabaka 24hrs kuyi realeasing evidence cewa yaran data daka suna ICU with Doctors report and everything, and again inaso kuyi proving cewa she’s really a killer, banda haka I

want to know wat right that officer takedashi to slap and hit Miss Rashida, and again wanda aka bishi har gida shine akaje neman tsokana, prove all this ba set up bane inba hakaba" Munir yace "zaku hadu da bacin ran Mai Martaba" baki Inspector yabude zaiyi magana Riyad yadagamai hannu for the second time yadakamai tsawa sabida yanda ranshi yake abace yace "release her now!!!!" Shi kanshi Munir saida ya kalli Riyad rabon dayaga dan uwanshi yayi fushi haka harya manta, da wuya Riyad yayi fushi, jikinshi har rawa Inspector yake yafita dasauri shi baimasan case din ba duk suka bishi yawuce kasa Riyad na biyedashi yadauki key na kofan da ake budewa a shiga bangaren cell nasu yabude kofan da sauri ya shiga saikuma ya juyo yace "Allah taimaki ranka shi dade ban santa ba ita yarinyar" wuceshi Riyad yayi kawai yashiga ciki mutumin ya bishi abaya cell cell ne daban daban, na mata daban na maza daban but duka ajere suke, ga mutane kukkule amman baiga Rashida ba in any of cell na mata dasuka wuce ba, zagawa dashi Inspector yayi zuwa cell masu kama dana kaji ana kiran dakunan NO SS CELL wato no sitting no standing cell, wanda shi na punishment ne bazaka iya tsayuwa ba bazaka iya zama ba kana duke kawai idan anaso a azabtar dakai ake kaika wajen, hangota Riyad yayi ita kadai an rufeta a cell dayakenan kaman cell din dan buri alalo alalo gwanin ban tausayi she looks very very miserable and terrible ko kadan bata kallo inda suke ba danta dauka matarce tadawo, ahankali Inspector da gabanshi ke faduwa ganin ita kadai ce abarayin NO SS yace "itace naga kana kallonta"? Juyo da kanta Rasheeda tayi jin datayi anyi magana tunda ta shigo wajen sai yanzu taga haske hasken Riyad dake tsaye yana kallonta idanunshi sun chanza launi kallo yake mata dabazaka iya tantance na menene ba, ahankali yake kallonta even though she's not crying but kasan she's very very scared, she's terrified, she's lonely, she's afraid, dauke kanta tayi daga kallonshi da sauri tashiga wasa da fingers nata, bude kofan Inspector yayi yace "fito" kokarin motsi tayi da kafa amman takasa sabida yanda kafafunta suka sankare suka rike sai kawai Riyad yaji zuciyanshi ta tsinke awani irin hankali yafara tafiya dudda bata kallonshi but every step nashi tana jinshi har a bangon zuciyanta, ahankali azo gaban cell din ya tsaya chak still taki dago da kanta, yakai wajen 10secs yana kallonta kafin awani irin hankali yaciro hannunshi daga aljihu yamika mata cikin wani irin murya mai masifan taushi yace "Rasheedah!" Har kasan zuciyanta taji yanda yakirata hakan yasa tadago kanta takalleshi sannan takalli hannunshi dayake mika mata batare data karbi hannunba, ahankali yace "come Mama is waiting" dasauri ta kalli fuskanshi kafin awani irin hankali takai hannunta tadaura gently kaman mai tsoro cikin nashi, atare dukansu sukaji shock amman yadaure yakamata sannan ya fizgota tashi daya tafado kirjinshi making deep sound mara kara sosai dazai nuna how hurt she's, kafafun na mata ciwo sosai amman sabida dauriya da taurin rai taki nunawa but takasa motsi tana kirjinshi, dan sauke kai Inspector yayi aranshi yace "budurwan mai martaba muka kulle dama? Suwaye keson sani a bala'i" takai one minute a kirjinshi batare daya taba bayanta ba banda hannunta daya rike but ita takasa motsa kafan tafita daga kirjinshi, in a very caring tone dabama tasan yanada shi ba yace "can you walk now"? Duk yanda taso karta kalleshi kasawa tayi tana kirjinshi tadaga fuskanta takalleshi hada idanu sukayi cikeda tsananin kulawa yace "can you walk yanzu?" Very soft itama ta gyadamai

kai tana yunkurin fita daga kirjinshi, saitai baya zata fadi dasauri yakai hannunshi daya yakama waist nata sai kawai adake yakama hannunta daya yakai ta bayan kanshi ya ijiye yayi supporting nata dakyau kafin yace “let’s go” she’s scared internally, she’s shaking bamata da karfin wani abu so she just followed him tana dan dingishi suka fito ahaka.

Hannu yasa yabude kofa mutanen data gani awajan da yawa gasu police gawasu kaman bodyguard ga Munir datake gani a hotel nasu ga yan sanda maza biyu na dazu bataga macen ba yasa tadan yunkura cikeda karfin hali zata fita daga jikinshi kaman daga sama taji saukan hannunshi akan waist nata yamaidata side nashi da kyau dawani irin sauri tadan juyo da kanta ta kalleshi but fuskanshi is looking straight bayako kallonta yacigaba da tafiya da ita hakan yasa ahankali ta maida kanta kasa daidai sunzo kofan fita saiga yar sandan dazu tana shigowa itama suka hada ido wani abu Rashida taji yazo mata wuya ya tsaya duk kalan ciwon da kafanta ke mata amman saida taji tasami karfin daga kafan kawai takai ta kwasheta within a blink of an eye jikake tippptipp! Officer tai wani mummunan faduwa danko ita bata lura da kafan da Rashida tasamata ba dan fuskan Rashidan take kallo dana Riyad datagani tareda ita, da all the people dake wajen, yan sandan sukai kanta ganin kalan faduwan datayi ana “lafiya kika fadi haka sannu me kike kallo haka” dan babu wanda ya lura da abinda Rashida tayi dagowa officer tayi hancinta na jini ta kallo kofan hada ido tayi da Rashida dake mata kallon munyi settling score dake, tsayawa shima Riyad yayi yana kallon Rashidan cus he saw wat she did saikuma kawai yacigaba da tafiya da ita suka fice har wajen motan shi su Munir suka biyosu baya yabude baya Mama idanunta harsun kumbura na zaune taganshi da Rashida dataga har yar rama tayi, sai kawai Mama tafashe da kuka jikin Rashida yayi mugun sanyi da taimakonshi ta shiga bayan motan sai kawai ta rungume Mama dan jim yayi yana kallonsu kafin ya maida kofan bayan yarufe yajuyo yadan taka zuwa wajensu Munir dake kallonshi kallon what is going on, anatse yace “I will see you at home bari na kaisu gida” bai jira amsan Munir ba yajuya yawuce saiya shiga gaba direban yatada motan yaja har lokacin Mama kuka take wlh takasa magana ma, hakuri take ta bama Mama amman yana shigowa tayi shiru kawai dai ta rungumeta agaban wani pharmacy yasa aka tsaya yafita yashiga yakai kusan 10min aciki yafito rikeda leda yadawo ciki ya zauna aka tada motan har zuwa anguwan su parking yayi yabude gaban motan yafito yabude bangaren Mama ahankali Rashida tasaketa goge fuskanta tayi ta sauko sannan ta mikama Rashidan hannu tace “taho muje” cike da karfin hali ganin yana wajen yasa tace “ni zan iya fita dakaina” tsayawa Mama tayi tana kallonta irin kallon wani irin taurin kai da karfin hali Rashida kedashi ne, shima Riyad folding hannunshi yayi a kirji ya tsaya kawai suna kallonta jan jiki tayi har tazo bakin kofan ahankali ta daga kafa daya tafito hakama dayan sannan ta yunkura ta tashi dudda she’s not showing the pain a fuskanta but wlh kasan da kyar take komi takawa tashigayi ahankali sai kawai tawuce tai zaure da dafa bango ta shige cikin gida, Mama tabiyota abaya tana shiga rabin buhun shinkafar taci karo

dashi a tsakar gidan nasu jitayi zuciyanta kawai yarikice ranta yabaci tama manta tanada ciwo kawai tai wajen shinkafan azuciye ta daga shinkafan zata mike kafanta yayi wani irin kara da duk dauriyanta saida tai ihu daidai lokacin Riyad ya shigo gidan azuciye yayi wajen yasa hannu ya fizge buhun shinkafan yayi ihu yace “what is your problem?” Kallonshi tayi ido cikin ido tace “mezamuyi da shinkafarsu? Zubarwa zany…….” “Quiet!” Riyad ya daka mata tsawa da saida taji jikinta yayi rawa, cikin tsananin fushi ya nuna Mama datake rabe a bangon zaure kawai ta tsaya chak tana kallon yarinyar tata gwanin ban tausayi, irin kallon yaya zanyi da wannan yarinyar ya Allah, yace “can you give your Mom just a minute of peace?” Kallon Mama tayi saikuma ta kalleshi zata bude baki authoritatively Riyad yace “I said quiet!” Cikin kwayar idanunshi ta kalla the anger datake gani da fushi kawai saitaji takasa magana wani bai taba shutting nata up in her life ba sai yau, cikeda tsananin bacin rai yace “kina tunanin komi arayuwan nan you settle it da fada da duka you think is by fighting?” Yasake shiru saikuma ya lumshe idanu tareda fuzar da iska yasake kallonta yace “every action have consequences do you for once sit down kiyi tunanin waye ke suffering consequences na action naki?” Yadan mata ihu kadan still kallonshi take da manyan idanun nan nata, saiya sake nuna Mama dake tsaye looking at them tana goge hawaye da bayan hijabi yace “do you have slight idea of abinda Mamanki went through today? Did you even know an ina naganta?” Yasakeyin shiru saikuma a sanyaye yet da tsaurin harshe yace “do you even love your mother?” Wani kallo datamai har saida idanunta sukahau sparking sabida anger kaman zata rufeshi da duka, cikin fushi tace “kai waye dazaka tambayeni ko inason mahaifiyata, waye kai”? Cikin tsatsauran murya Mama tace “tamaka rashin kunya ka yanka mata mari Riyad!”.

RASHIDA IS STUBBORN CUS WATT

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 21

Kallon Mama Rashida tayi zuciyanta yafara tsinkewa ganin shi Mama take supporting tabude baki zatai magana saitaji kuka na son subuce mata hakan yasa tarike maganan da kyar ta danne kukan tace “to sai in tsaya ina kallo ana zagin Mamana”? Rai abace Riyad yasa hannu a lips nashi yace “shush” abu taji yazo mata wuya wayeshi dahar zai dinga mata fada agidansu kuma Mama na supporting nashi sai kace wani Yayanta, dauke kai tayi daga kallonshi tana huci kaman damusa yace “zagi baya kari, zagi baya chanza fatan mutum, you are a very selfish girl that care

about feelings nata not her mother” wannan karan juyo da kanta tayi ta kalleshi idanunta sun ciko da hawaye amman tahanasu zubowa shima yana kallonta kyar yace “duk yaron daya gwammace yabi zuciyanshi dayabi maganan Mamanshi is selfish! Your mother is sick! Anything daya shafeki affects her greatly, akanme bazakiyi hakuri ba just for her safety and wellbeing huhh? And kince kinason Maman ki? Your are just a terrible selfish daughter wacce ta damu da ego nata not her mother” shima yayi maganan idanunsa na ja Mama kawai kallonsu take bata tabajin tanason Riyad kaman yanda taji tana sonshi ba yau, cikin fushi yace “your Mom nada BP very high BP, kwanciyan hankali takeso but kullum cikin tashin hankali take sabida ke! Kullum fitinan ta kike da fitinu daban daban do you want to kill her?” Daidainan hawaye ya zubo sharr daga idanunta da sauri ta dauke kanta tasa bayan hannu ta share, cikeda fada yace “I saw your Mom at the middle of titi bamatasan metakeyi ba she was panicking calling your name, yarinyana! Y’ata, da kinfito daga police station kinga ta mutu fa?” Takawa yayi zuwa inda take facing ya tsaya chak agabanta adake hakan yasa ta kalleshi da rinannun idanunta ya nuna mata yatsu cikeda wulakanci □□ yace “take this as your last and final warning, idan kika kara troubling Mama zanzo I will take her away from you na kaita inda za’ayi cherishing nata forever, sannan abata peace of mind data rasa daga wajenki, I dare you ki kara trying wani nonsense hali dazai tadama Maman ki hankali saina sabamiki you selfish egotistic girl!!” Yana maganan yajuya zuwa inda Mama take a zaure cikeda so yace “muje Mama” juyo da kanta tayi ta kallesu abunda taji tuntuni yana wuyanta kawai taji yazo mata baki da sauri tajuya tashiga daki tawuce uwardaka sai kuka taji kawai ta tsani Riyad, kishi yakamata yanda Mama kaman tafisonshi sama da ita, he’s making her look like a bad daughter.

Zaunar da Mama yayi akan tabarma sai ya zauna a gefenta yace “Mama kidena damuwa kinji she’s fine babu abinda yasameta, itakuma Matan zansa anemota she will pay for abinda ta muku” dasauri Mama ta girgizamai kai tace “Riyad tunda ka karbomin Rashida kabar mutanen nan da halinsu duk inda kake tunani sun wuce haka I don’t want to involve you a matsalanmu this people are terrible and very powerful banso sumaka wani abu, kamin alkawari bazakasa anemota ba, kabarta da halinta, karma ka koma police station din, bawai koda yaushe take damunmu ba, rabonta da gidan nan kusan 5yrs ago sai yau datazo maybe sai nan da another 5yrs kuma zata kara zuwa, banson wani tashin hankalin banson damuwa, banda ma karfin zuwa police station bada statement, haka kuma banso Rashida taje police station wazai aureta? It will ruin her life? Cell din nan kadai yanzu ma yayi ruining life nata yan anguwan nan babu inda bazasukai labarin ba, I’m tired of all this, I keep causing pain arayuwanta, nice darkness na rayuwanta, nasan Rashida bataji she’s stubborn but she became like this sabida ni, no body wants to be friends da ita, no body wants to marry her, koyaya wani yazo nemanta Sheri da gaskiya sai yan layin nan sun tara sun fada akanta yanzu kuma dataje cell we are ruin gabaki daya” Mama ta share kwallan daya zubomata saikuma tadaga kai ta kalli Riyad da

fuskanshi yayi kaman zaiyi kuka tace “Riyad kamin komi arayuwan nan wanda har dan uwana na jini bemin ba, thank you for everything, thank you for saving my daughter’s life, nagode Riyad kaji, but don’t involve kanka in our personal family issues is not worth it, babu amfanin shiga 23yrs of matsala kana shiga zata dawo sabuwa I hope you understand”? Shiru yayi sai chan ya gyadama Mama kai yace “I understand Mama nabar case din but duk randa tasake zuwa I won’t spare her” murmushi Mama tamai tace “tashi kaje gida kaima ka huta gobe salla, kasha ruwa Allah maka Albarka” wlh har cikin ranshi he’s feeling very attached to Mama kaman karya barta ahaka amman yadaure ledan Pharmacy dake aljihunshi yaciro yabata yace “gashi Mama na kafanta ne” yayi maganan yana tashi yace “saida safe Mama” kallonshi kawai Mama take cikeda kauna tace “saida safe Riyad ayi salla lafiya” sannan takalli ledan pharmacy din tana tuna yanda yama Rashida fada yanzun nan saikuma tai murmushi.

Gyara zama Mama tayi tai shiru ita kadai awajen Allah kadai yasan tunani tunanin metake bini bini tasa hannu ta share hawayenta dayake zubomata, ruwan dabatasha kenan ba, har wajen 12 na dare ita kadai, sannan ta tashi da kyar tawuce tayo alwala kanta kaman zai cire tashiga daki tadauki pure water tasha sannan tahau dadduma azaune tai sallan tana idarwa tashiga uwardaka akasa taga Rashida na bacci ko hijabi bata cireba tsabagen fitina, zama tayi wajen ta yaye skirt na jikinta tadauki ledan ta ciro man shafawan daya siyo Mama tai shiru tana kallo saikuma ta kalli fuskan Rashidan ahankali tace “stop this madness and see Riyad Rashida, is because you’re hurt abin yakara batamai rai yake miki fada not just sabida ni kadai” dan murmushi kadan Mama tayi tace “he’s romantic” saikuma takai hannunta saman bakinta kaman mainin kunya tace “ke Zainabu” budewa tayi ta lakato ta shafa mata maganin a kafafunta sannan ta ijiye maganin saikuma tai tagumi tana kallonta addu’a kawai take Allah yarage mata zafin zuciya da yawan fushi din nan kar watarana fushi yasa tai kisan kai yanda ta watsar da matan nan biyu dazu ga jini a goshinsu Mama ta girgiza ainun batasan Rashida tayi nisa hakaba.

Har asuba tayi Mama bata kulle idanu da sunan bacci ba.

Ahankali tabude idanunta jin an tabata ganin Mama sanye da hijabi tai alwala yasa ta tashi zaune da sauri ahankali tace “Mama” kallonta Mama tayi saitai shiru bata amsaba kaman irin da abin ta kwana hakan yasa tafashe da kuka mai karfi tace “Mama dan Allah kiyakuri ki yafemin bazan kara miki rashin ji ba, kome kikace nayi zanyi, Mama everything is my fault, danaji maganan ki dakikace nabari nabarsu

munshiga dakin da duk haka bai faru ba, Mama da mota ya kadeki dame zan gayama Allah”? Yanda take kuka wlh saita baka tausayi Mama taso yau ta shareta Amman saitaji bazata iyaba saita zauna tace “kimin shiru” tsagaita kukan tayi tana kallon Mama da rinannun idanunta, ahankali Mama tace “yawan fushi nasa kai abu da dama dazakai nadama Doctor” cikin raunin murya tace “Mama u hate that woman, I hate mijinta, I hate entire family nasu, those people made you suffer all your life har yanzu kuma basu barkıba” Mama na kallonta tace “idan zaki bimin hakki na ne then kiyi focusing a school, ki gama school ki zama wani abu, ki nuna musu cewa Mamanki dasuka wulakanta ta haifoki diya me albarka me goshi, ki zama Dr tukunna and cure me kinji kidena fada da mutane akaina focus on goal naki nan gaba na warke no body can troll me right”? Gyadama Mama kai tayi Mama tace “bansan ko zamuyi rayuwa tare har karshe ba babu wanda yasan gobe ke babu wanda yasan anjima ma, idan bana raye kikai wani abu who will protect you and stand by you? Ayau dudda banda wani abu but at least I use strength dina na shiga gari ina neman wanda zai taimakeni ya tsayama diyata but randa bananan fa? Who will fight for you and stand by you? Lokaci yayi dazaki bar halin nan, ke kadai gareni kene komi nawa if something happens to you I die, jiya I was so scared…..” saikuma tafashe da kuka dayasa Rashida ta rungume Mamanta da gudu tace “Mama it’s okay bazan kara ba kinji, I’m here now I’m fine kinga kafan ma naji ya warke tass” ta shilla kafan sama Mama tace “maganin da Riyad ya siyamiki ne” haderai tayi da sauri tace “Mama wlh na tsaneshi baida kirki niyake gayama zai rabaki dani yana kirana selfish daughter” ahankali Mama tace “he did the right thing, kuma kika dameni zan bishi dagaske, Allah yamai albarka daya miki fada, naji dadi da akwai wanda zai iya miki fada haka kiyi shiru dan gani kike kaman kinfi karfin kowa” tashi tayi sabida bataso tace wani abu tasake batama Mama rai kawai tawuce tafita.

Alwala tayo sai yanzu ma ta Tuna ki ruwa batasha ba jiya to waka yasha? Har Mama ma batasha ba Tana salla tafita tea tahada musu sukasha sannan takaima Mama ruwan wanka tadawo tadawo ta gyara gidan ciki da waje tsaf Mama tace “zoki wanka karmu rasa sallan idi idan muka dawo mayi girki”.

Wanka awuce tayo tadawo atampanta na salla data karbo fara wajen dinki ta warware skirt da riga ne blue pink atampa ne tasaka da sabon bra da pant tayi kyau sosai dudda batai lalle ba daman jiya sukace zasuyi but Allah bai nufa ba, ta daura dan kwali Mama tace “zauna kisa kwalli ki shafa jan baki kodan darajan yau salla” batai musu ba tazauna tajawo basket na kayan kwalliya tadauki kwalli tasaka tadau wani pink tsohon jan bakinta ta shafa ta gyara gashinta wanda shi ta wanke abayi yanzu da safen nan ta shafa mai ta taje tai parking sannan ta daura dan kwali ta fesa turare ta tashi sai Mama dake kokarin sa hijabi tabita da kallo batasan lokacin datace “tubarkallah Allah ubangiji ya nunamin aurenki haka kici gayu kısa kayan amare” turo baki tayi taki amsawa tadauki pink hijabin data dinko na salla tasaka ta dauki dadduman su da yar wayanta suka fito rufe gidan sukayi da kafa sukaje

masallacin ana salla ana kaiwa sujud Mama tashiga rokon Allah yabama Rashida mijin dazai sota ya tsaya mata yakuma kula da ita, sallamewa akayi suka wuce kasuwa kaji guda biyu suka sayo da kayan Miya da fulawa dasu butter sannan suka shigo keke suka tafi gida suna dawowa ta shiga kiciniyar hada gawayi dan daura abinci ganin gawayinsu saura kadan gashi tasa abinci a wuta yasa tarike kudi a hannu tawuce zaure dan neman yaro ta aika makotansu yakawo mata gawayi, tana sakai awaje karaf suka hada ido da Riyad daya bude kofa yafito daga cikin mota yana sanye da manyan kaya da babban riga da hula bugawa kirjinta yayi sabida yanda yayi kyau na bala'i, sai kawai ta tsaya chak ita takasa komawa ciki ita takasa motsi ita takasa daina kallonshi, har saida shi yadauke kanshi daga kallonta akufule yace "kifito yan duniya suga kwalliyan sallan da kyau!" Runtse idanu yayi dan baisan ya akayi maganan tafito daga bakinshi ba, saikuma yahade giran sama da kasa yajuyo yamata wani irin kallon da kawai taji tajuya da sauri takoma cikin gida kirjinta na bugawa dim dim dim chan sai ga sallaman yaro yashigo da kwalin kaji yace "gashi wai inji Riyad aba Mama" afadace Rashida tace "Kai maidamai kace batanan" yaron yace "ai yashiga mota yatafi" ranta taji yabaci daga daki Mama tace "ijiye zo ga tukuici" dasauri yaron ya nuna new 1k note dake hannunshi yace "ai yabani dubu daya" yajuya yafita abinshi, hijabi Rashida ta dauka tasaka tafita ganin bayanan yasa ta shiga makota tasayo gawayi tana dawowa taga Mama tacire just 3 acikin kajin da an gyara but ba'a yayyanka ba tace "dauka sauran kikai gidan Baba Liman kice kawo mana akayi karsuki karba" batai musu ba ta dauka tawuce takai a zaure tahadu da Liman yace "jiya naje kauye saida nadawo naji abinda yafaru Allah kiyaye gaba ki gayama Mamanki zan shigo anjima da yamma" gyadamai kai tayi tawuce ta koma gida lafiyayyen girki tayi tai dambun naman kaza ta soya some tai pepper chicken da some, tai jellof rice tai cincin around 4 tagama komi ta shiga daki ganin Mama duk bata wani cicciba yasa tace "Mama baki ciba" ahankali Mama tace "kaina kedan ciwo anjima ya sauka zan sha" kallon Mama tayi saikuma ta zauna kusada ita tace "Mama kedai sabida ina chan ina aiki ne yasa bakiciba, bude bakinki kiga" ta deba rice din takai bakinta dan murmushi Mama tayi tabude ta karba just to make her smile ta yarda taci amman ko taste bataji na abincin ba.

Har isha'i hira sukeyi around 9 tai bacci awajen Mama tabita da kallo sannan ta lallaba ta mike tana dafa bango kujera ta dauka da buta tawuce chan bakin makwarara amai ta kwara sai ijiyan zuciya takeyi ta wanke fuska tadawo daki kafafunta ta kalla da tun dazu da rana sai zugi suke mata gashi ta lura sunata kumbura, yanzu ma sun karu sai kawai ta zauna tai tagumi tana kallon Rashida damuwa da fargabanta data shigane yasa kawai taji jikinta yanaso ya rikice haryakai ga abinci ma bataso, tunani take, takasa manta maganan Jummai, dudda tahana Riyad karyay involving kansa a case din tasan yanda aka ciro Rasheedan nan that woman will find a way ta cutar da Rashida Alkawari ne wannan! She's just scared for yarta, idan tafita school aka dauketa fa? Idan aka halakata fa? Idan tasa akama Rashida wani abu fa? Wat if she set Rashida up yanzu ta yanda zata tura mata yarinya prison inda ko Riyad bazai iya cirota ba, abinda ke kara firgitata is

zuciyan Rashida just like yanda tazo jiya ta takali Rashida and she fell for it still haka zata karayi Rashida kuma ba hakuri taje tai wani abu shikenan akamata akai prison with concrete evidence. Yaya zatai protecting Rashida? Kodai su saida gidan su koma kauyensu dudda Kawu ya koreta ada dasuka je? But makarantan Rashida fa, itafa asibiti fa, auren Rashida fa? Riyad fa? Batama Rashida kwadayi tai auren kauye, tanaso diyarta tazama wata babba aduniya, but idan matan nan ta turo maza suka dauke Rashida sukai amfani da itafa suka lalata mata rayuwa tunda dai burinta na police station bai yuwuba, tayaya zata kare yarta? Dudda Rashida akwai karfi akwai zuciya but maza maza ne! Idan akai kidanapping Rashida yanzu yaya zatayi? Tunani daban daban take sai kawai jikinta yasake rikicewa har aka kira asuba yau takasa tashi tana wajen zaune tana kallon yarta,har Rashida ta farka da kanta tabude ido taga Mama murmushi tayi tai mika ta tashi tace “Mama baki tadani ba sabida ba aiki ko” gari yawaye Mama banyi salla ba”.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 22

Dasauri ta tashi tafice alwala tayo tashigo agurguje tasa hijabi ta tada salla tana sallamewa daganan kan daduman ta hango kafan Mama yanda suka kumbura suntum dawani irin sauri ta taso tazo wajen tace “innalillahi” dan yatsa tasa ya nitse akafan yanda jikin Rashida yahau rawa saida ta tsorata tace “Ma…..m” tama kasa magana tsabagen yanda zuciyanta ke bugawa saikuma ta juya a haukace zata fita daga dakin hijabin dake jikinta Mama takama hakan yasa da sauri tajuyo saikuma ta duka, ahankali Mama da bakinta baya motsi sosai tace “kaini nai fitsari nai alwala nai salla” gyadamata kai Rashida tayi da sauri tace “to Mama” tawuce tafita takai ruwa bayinsu sannan tadawo daukan Mama tayi ta dagata Mama ta tashi kafan natama nitsewa yake dasauri Rashida ta zaunar da ita tace “Mama tsaya nakawo po kiyi fitsarin adaki namiki alwala” ta zaunar da ita tacire hijabin ta ijiye tafice taje chan hanyan bayi ta dauko po ta wanke tadawo dakin da taimakonta Mama tayi tai tsarki tadauko tafito tadawo ta goge wajen tass sannan tamata alwala ta daura ta kan dadduma dantai salla hannunta Mama takama tamata murmushi tace “relax babu abinda zai sameni daga hannunki inajin yanda zuciyanki ke bugawa” kallonta Rashida tayi idanunta sun cika da hawaye baki tabude zatai magana saita kasa tafashe da kuka tace “Mama wlh ina sonki Mama, Mama kene rayuwana gabaki daya Mama kiyakuri kiji sauki I know damuwana yasa BP ki yatashi bare naje nakira Musa yaron Baba Liman ya kaimu asibiti, Mama kiyafemin wlh wlh wlh bazan kara saki magana ba, Mama kina cewa nabari nabari kinji Mama wlh na rantse da Allah” dayan hannunta Mama takai saman fuskanta ta goge hawayen dasuka zubo ahankali Mama tace “come” matso da fuskanta tayi kiss Mama tamata a goshi

muryanta chan kasa tace “I love you Rashida remember this always konai fushi dake bahar zuciyata bane kinji, stop crying I will be fine muje asibitin jeki kira Musa” tai maganan tana kara goge mata fuskan tass tashi Rashida tayi tadauki hijabinta tafice daga gidan, gidan Baba Liman tawuce a kofar gidama taganshi ganinta yasa kafin tamayi magana yace “lafiya?” Ahankali tace “Musa nazo kira yakaimu asibiti jikin Mama yatashi” ahankali Baba Liman yace “Subhanallahi Allah yabata lpy jeki kimtsa zan biyoshi muzo” juyawa tayi takoma gidan Mama nakan dadduma kallonta tayi da kafafun dasuke amike kaman kara kumbura suke every minute, wata yar jakarsu ta dauka ta shiga debama Mama su t-shirt da zani she’s a student doctor she know case din Mama is not something daza’a sallamesu gobe, tadau zanin gado wankakke da hijabi itama tasa yan kayanta dan daga wajen zata dinga zuwa department dinsu ta kwaso duka kudin dasuke dashi tashiga kirgawa gashi sun kashe kudi akasuwa ranan salla, Mama sai kallonta take yanda jikinta ke rawa kaman tamata kuka tadai daure bataso ma tanuna mata kalan azaban datakeji saisa take daurewa sunayen Allah akwai take kira abakinta, 85k sukedashi tadauki wayanta tanada about 51k a account, jakan makarantan da da komi keciki tagoya ta gungura jakan takawo tsakar gida daidai lokacin an buga gate dasauri ta gungura box din waje su kasa a keke ahankali tace “Musa zoka tayani mu dauketa bazata iya tafiya ba” daga Musa har Baba Liman biyota sukai ciki, Baba yakalli Mama da idanunta ke a kulle sabida tsananin ciwo yace “sannu da jikin Maman Rashida sannu” gyadamai kai tayi batare data bude idanubta ba, Baba Liman yace “kawomin ruwa Rashida namata addu’a” dan yana ganin Mama yasan ita kadai tasan metakeji, kawomai ruwa tayi da sauri karba yayi yayi addu’o’i ciki yabata yace “bata tasha ki shafa mata sauran akafa” karba tayi cike da tsantsan so tace “Mama sha Baba Liman yamiki addu’a” ahankali Mama tabude idanunta dasukai jazur tadaurasu kan Rashida tadan bude bakinta kadan samata ruwan Rashida tayi tasha kadan sannan ta tsiyaya a hannunta ta shafa mata a kafafun sannan ta ijiye a gefe tace “Musa zoka tayani” zuwa yayi atare suka daga Mama tsaye sannan suka dauketa chak suka fita da ita a keke suka sata dawowa ciki tayi tadan gyara ko’ina agurguje sannan tadauko key tafito ta kulle gidan da kofansu tazo tashiga keke tazauna Musa yatada keken Baba Liman yace “duk yanda ake ciki kinkirani, Allah baki lpy Maman Rashida” Ameen Rashida ta amsa Musa yaja keken itakuma tashiga kiran HOD nata wacce suke kira da Mrs Bugaje wacce take Doctor Mama, kusan a kira nabiyu ta daga sabida girkin salla yau yawon salla, tana dagawa tace “Rashida how are you sorry ina kitchen ne I missed call naki is everything fine”? Ahankali tace “Ma jikin Mama ne kafafunta sun kumbura sosai she’s in pain muna hanyan tafiya hospital” Dasauri Dr Bugaje tace “take her to A & E, she must be treated as emergency, bari I will call Dr Usama yau ina off but I will come once na gama girki for my family, don’t worry okay Maman ki will be fine” gyadamata kai Rashida tayi tana sharce hawayen dakeson zubomata daga idanu sannan ta katse wayan, suna kaiwa asibiti A & E tawuce ba’asa sun jira anything ba sabida Rashida is a Dr aka sa Mama agado akai ciki da ita Dr Usaman yazo Rashida takasa komi, all ciwon Mama tadamata da hankali yake but hakanan she’s getting a special vibe daga wannan kaman zaifi kowannne worst duba da kafafunta tana tsaye inda yagama dubata,

sannan yajuyo yakalli Rashida Dr Usama yazo yace “follow me” binshi tayi ahankali har zuwa office nashi saikuma yajuyo ya kalleta dan murmushi kadan yamata cikeda hikima na manya yace “calm down Dr Rashida sit” tana tsaye tace “tell me meke damun Mamana Dr” Dr Bugaje warned him about telling her anything yabari saitazo hakan yasa yace “is just blood pressure ta yatashi” tana kallon kwayan idanunshi tace “tell me I can handle anything I know People living with HIV (PLHIV) dakuma HBP (High blood pressure) Hypertension sunada significantly high risk of cardiovascular events abubuwan daya danganci matsalan ciwon zuciya da mutuwa, which is thought to be due to a complex interplay of various factors including immune dysfunction, endothelial dysfunction, and inflammatory changes, nasan Mama na is at risk of coming down da stroke, heart attack, heart failure, kumburin jijiyoyin daukan jini na jikinta, taushewan vessels dake daukan jini daga zuciya zuwa jiki, kidney issues, high cholesterol, dakuma matsalolin iya numfashi” hijabinta takama tadaura daura kan fuskanta tana matse idanunta sosai dakeson suyi kuka tace “just tell me wanne daga ciki ke damun Mamana?” Wlh ayanda yaga Rashida shi kanshi saiyaji bazai iya gayamata ba gwara Mrs Bugaje tazo tagaya mata, dan murmushi yace “I actually called you nagaya miki yanayinki din nan zai saka Maman ki cikin tashin hankali, calm down Mrs Bugaje is coming wuce kitafi” wani irin kallo tama Dr saikuma ta tashi tawuce takoma A&E din tazauna kan kujeran dake gaban gadanso takalli Mama da idanunta ke kulle sai bakinta daketa motsi na la’ilaha illallah tanashan azaba takai hannunta takama tarike gam, kawai she’s just looking at Mamanta feeling pains she wish itane akan gadon kwance ta dauke ciwon instead of Mamanta, tana zaune awajen wayan jakanta yashiga kara na Mama cirowa tayi taga Liman dauka tayi takai kunne yace “Yaya jikin nata me akace Rashida?” Ahankali tace “Dr Bugaje nake jira tazo gatanan a hanya” anatse yace “kome ake ciki ki kirani Allah bata lpy” ahankali tace “Ameen ta katse wayan” ta ijiye.

Around 12 Mrs Bugaje tashigo office nata tafara zuwa ta ijiye bag nata da komi ta sanya lab coat tafito Babban mace ce dazata kai 50yrs haka office na Dr Usama taje tadan jima kafin sutaho ward din tare Rashida na zaune rikeda hannun Mama taji muryan Mrs Bugaje cikeda wasa irin na professional Doctors din nan tace “Mama yaya mukayi ni da ke?

Wat was our agreement? Dasauri Rashida ta juyo ta kalleta, handglove tashiga sawa tana murmushi tana kallon Mama kaman irin nothing serious din nan sannan tataho gaban gadon tace “open your eyes for me Mama kar Rashida tafashemin da kuka anan dukta damu” ahankali Mama tashiga bude idanunta da kyar tabude kadan sunyi jazur takalli Rashida dake tsaye gefen Mrs Bugaje tai zuru zuru bakaramin dadin hakan Mrs Bugaje tajiba tace “good job Mama, tell me meke damunki? Meya tadamiki da hankali haka dahar kika bata agreement namu na

bazaki dinga tunani be?” Mrs Bugaje tai maganan tana duba kafafun Mama tana dubawa kumhurin yanzu ya wuce guiwowinta ma, cikin wani irin murya da baya fita Mama tace “Jummai, Jummai zata halakamin rayuwan yarinyana, Jummai nason halakamin yarinya” dasauri Rashida tai wajen takama hannunta da sauri tace “Mama dama abinda kiketa tunani kenan babu wacce zata iyamin komi I can defend myself kinji kidena tunanin” girgizakai Mama tayi hankalinta nawani irin tashi takalli Dr tace “Mrs Bugaje hide…….hide my daughter…..banson ta cutarmini da yarinya, nasan Jummai nasan bazata kyaleta ba, Jummai Jummai, yarinyana, Rashi…… Rashi….Rash….” Kawai sai Mama tafara yunkurowa tana wani irin nishi kaman zata mutu numfashi kaman yana gagaranta ma, Mrs Bugaje tai maza takama kafadarta tana maidata gado tace “Mama calm down calm down Mama I will hide Rashida babu abinda za’a ma yarinyarki” inaaa kaman ma Mama batasan inda kanta yakeba wani irin gasping breath Mama keyi dayasa Rashida kawai tadaura hannunwanta kan baki tana wani irin kuka tana kallon Mama dataga Mrs Bugaje da Dr Usama are trying to save at all cost Mama tasha ciwo but not irin wannan bata tabajinta this scared arayuwanta ba Mama is her biggest strength for the first time arayuwanta taji karfinta jarumtarta ma gaxawa she don’t even know ina kanta yake tadaiji an jijigata ance “Rashida!” Firgigit tadawo daidai Mrs Bugaje ne tace “come with me” dasauri takalli Mama dataga an sama oxygen a hanci wasu ma’aikata na gungurata zuwa wani wajen dabama tasani ba har office na Mrs Bugaje taje zaunar da ita Mrs Bugaje tayi akan kujera itama tazauna ganin yanda take kuma saita kara tashi tabude fridge na office din taciro cold water tamika mata tace “sha” ahankali Rashida tabude tadan kurbi kadan daidai lokacin Dr Usama na shigowa dawasu papers kusan guda 5, Mrs Bugaje ta karba tace “thank you Dr” gyadamata kai yayi yace “bari nakoma” yajuya yafice papers din Mrs Bugaje tasaka glass tana dubawa kusan 20min sannan ta ijiye tareda sauke glasses din takalli Rashida daketa kallonta she doesn’t even know what this small girl will do, ahankali tace “Rashida tun kina 100 level nasan how strong you are, bantaba ganin strong resilient student arayuwana like you ba wacce at a very young age shoulder responsibilities Mamanta da school da komi na rayuwansu, I supported you all through pull some strings na tabbatar kina gamawa da clinic dinki by 1PM wanda ba’a taba dagama student kafa haka ba, but I made it happen sabida I see you I see rayuwan dakikeyi a daughter like you deserve standing ovation, dan haka banson ki karaya this time fight this also kaman yanda you fought komi na baya kuka cigaba da rayuwa kinji Rashida” gyadamata kai Rashida tayi tana kallonta tana rike duka abubuwan datakeji azuciyanta, Dr Bugaje tace “BP Mama yakai level din da ko makiyina bazanmai fatan yakaiba, legs nata are starting to have stroke sabida blood vassel nata na zuwa wato Artherties nata are blocked jini baya fita da kyau, now dole mu mata procedure call……” ahankali Rashida tace “arherectomy!” Ijiyan zuciya Mrs Bugaje tasauke tace “yes, minimal invasive procedure ne dazamuyi dan muyi flushing buildup din daya cika vessel din sabida jini yasamu yawuce wajen freely, that is one” tadan sauke ijiyan zuciya tadauki paper gabanta tamika mata tace “ga result na express ECG da Dr Usama yasa aka mata can you read ECG da kyau?” Gyadamata kai Rashida tayi da sauri takarba tana karanta rhythm din, cikin wata

kalan sassanyar murya Mrs Bugaje tace “I think zuciyan Mamanki is failing!” Wannan karan ijiye paper Rashida tayi agabanta tadaura hannunta saman idanunta ta matse hawaye still yana diddiga from side, wlh kawai dan ita Dr ne but she wants to cry for the girl, ahankali tace “matsalan HIV is yanacin kwayoyin garkuwan jiki, dazaran cuta tashigeka HIV yana cinye wayan nan garkuwan na jikinka da naturally suke fighting cuta kowace iri, it’s a long shot but banso kiyi loosing hope we can still save your Mom” har lokacin Rashida batasaki idanunta ba hancinta kawai yake motsi tip na hancin yayi jazur wani tsinkakkiyar majina na lekowa daga hancin, ahankali Mrs Bugaje tace “Rashida” dago kanta tayi tana sakin idanunta cikin muryanta dahar yakoma kaman na me mura tace “naam” wani paper again Mrs Bugaje tabata tace “idan kinaso muyi treatment nata ayi procedure sannan ai connecting Mama da machine dazai taimaki heart dinta dake failing sannan ayi tackling BP da stroke din, to this is just a rough estimate na kudin dakike bugata rough estimate dan zaifi haka anything heart magungunan shi da treatment nashi is expensive, plus oxygen da yanzu muka sata akai dazai dinga tayata breathing you need about 2.5M!” Kallon list din take kawai, ta ina zata sami kalan kudin nan? Wani aiki zatayi tasami kudin nan just today sabida afarama Mama treatment sai alokacin kawai taji kuka yazomata kawai tafashe da kuka da karfin gaske tawani zube kasa daga jikin kujera ta dunkule paper a hannunta tana kuka sosai tashi Mrs Bugaje tayi ta zagayo ta duka ahankali agabanta idanunta sunyi jaaa tadafata tace “I know bakida this kind of money bakida hanyan samunsu Rashida it’s okay ya isa kukan we will not let Mama die” wani irin kallon Mrs Bugaje take tana kuka, Mrs Bugaje tace “Rashida I’m a family woman kwanan nan nama yarana dake UK registration na school wlh banda kudi but I will give you 200k sauran kudin kuma akwai this student loan da student ke iya applying idan kafara internship duk albashinka za’a dinga karba as payment for the loan, but matsalan shine CMD kadai ke signing and approving but baya gari dole mujira yadawo which bamuda lokacin the next option is student doctors and other people’s help seek for donation for Maman ki yawanci an sanki ansan situation na Mamanki they will help you hopefully zamu iya tashi da something, in the meantime kudin nan dazan baki dayan chanjin dake hannunki jeki sayi necessary magani dasu drip da ake bukata sabida afara ma Mama treatment kinji and pay for oxygen also dan na this hour kawai zasu bata idan baku biyaba bazasu bata again ba, Stop crying, remember na gayamiki you have to be strong ke kadai Mamanki keda shi, kene kadai zaki iya kula da ita, stand up dagata Mrs Bugaje tayi tace “Allah baya hada bawa da abinda yafi karfinshi kinji” gyadamata kai Rashida tayi takama hijabinta ta goge fuskanta tass, jakanta Mrs Bugaje tadauka ta bude taciro bandır na 100k guda biyu wanda sabida ita ta taho dashi tabata tasan basu dashi cus tun awaya Dr Usama yagaya mata komi tace “take” tsayawa tayi tana kallon kudin Allahu Akbar tunda tafara girma tafara aiki bata taba accepting wani kudi daza’a bata sabida Mama ba saidai Mama ta amsa yau gashi ita ake bama kudin taimako zata karba hannunta tamika dahar rawa suke ta amsa tama kasa godiya sabida shock Mrs Bugaje ta dauki precribtion sheet dawasu papers tabata tace “jeki sayo magungunan sannan kibiya kudin ECG da aka mata ki kowamin a ICU” gyadama Mrs Bugaje kai tayi tafito tafiya kawai take taje ta bibbiya

kudin ECG tasayo magunguna dasu drip tabiya kudin oxygen na kwana uku dan per hour ake biya shi, da kudin da Mrs bugaje taba tada kudin account dinta da na hannunta duka sun kare sai naira dari biyar daya rage mata this is duka kudinta gaba da baya, dawowa tayi ta tsaya gaban ICU mrs bugaje tafito ta amsa tace “now go round ask for help from this Doctors kinji” gyadamata kai tayi tajuya batamasan taya zata faraba stufent Dr dinsu duk sunje hutun salla public holiday wayanta ta dauka tasami waje ta zauna tai shiru yau ne rana na farko datai realizing good human relation ma wani abu ne arayuwa mu’amala me kyau yanada ranan sa, duk yanda kakaiga you don’t need anybody las las you still need everybody saidai in Allah bai jarabceka dawani abu ba, yanzu kotai magana a group ma yan class dinsu zasu taimaketa? Yawanci tayi fada dasu, yawanci bata kulasu kosun kulata, daurewa tayi tashiga typing komi na neman taimako Mamanta na critical condition tana neman 2.5M ta tura group din da acct details nata bini bini tana duba info kusun gani taga duk sun gani Layla ma fitowa tayi tafara hira a group din babu ko Allah sawake few friends nata suka shigo suka biyemata suna hira suna turo emojis na dariya.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 23

Kawai saita fito daga watsapp din da sauri tama kashe data ta ijiye wayan tasakeyin shiruu batada kowa Baffa yakori Mama takirashi? Yadena daukan number Mama banda haka ta tsani duk wanda ya wulakanta mahaifiyarta tashi tayi tana numfashi ahankali tashigo A&E ward din ta tsaya tana kallon yanda Doctors ke aiki trying to save lives duka duka nawane salary su babu wanda baida matsala tayaya zata fara binsu one by one tana neman taimako? Da kyar taja kafanta tawuce wajen wata Macen Dr datake tsaye gaban nursing station tana magana dasu ahankali Rashida tace “sannu” dasauri likitan tajuyo ta kalleta tace “yauwa sannu” kasa magana Rashida tayi batasan ta yanda zata fara rokon ba Dr tace “lafiya?” Ahankali Rashida tace “taimako nake nema, uhmmm” tahadiye abu awuyanta tace “Mama na needs 2.5M” kallonta Dr tayi saikuma chan tace “sorry about your Mom but kinsan this is the 2nd month da government basu biyamu ba? Metron fadamata” Dasauri katuwar Metron na wajen tace “wlh da na iya roko nima I’m bold enough like you danabi kowa na nema tsabagen rashin kudi this Tinubu Tenure no good for us kawai, ba’a biyamuba everyone is broke” gyadamusu kai Rashida tayi tawuce kawai taje wani lungu ta duka tana maida numfashi tana ahaka wayanta yahau ringing fitoda wayan tayi ganin Mrs Bugaje yasa ta tashi tama kasa daga wayan ta taho da gudu danta

dauka wani abu yasami Mama agaban ICU taga Mrs Bugaje, tana kallon Dr Usama dake kokarin helping Mama machine din da aka samata sai kuka yake arude tace “Dr what is happening to Mama”? Dasauri Dr tace “she needs atherectomy now vessels dinta sun kara blocking, you need to pay I think 800k ne or so kudin amata before we loose your Mom go” Mrs Bugaje na maganan ta juya takoma ciki Rashida tajuya itama bamatasan mezatayi ba Baba Liman tashiga kira tana tafiya kaman mahaukaciya ahanya tace “Baba Liman wazaisai gidanmu Mama na bukatan 2.5M yanzu kuma ana neman 800k ayi flushing zuciyanta” Baba Liman yace “Subhanallahi ta ina zamu samo wanda zaisai gidanku yanzu yanzu Rashida ai kusan is impossible amman bari natara jama’a naji” ya katse wayan batasan ma ina xatasa kanta ba Riyad! Kawai taji zuciyanta ya ambato, Riyad ne yafado mata arai, he helped them before, and yana shiri da Mama taje ta nemi rance ne kafin a saida gidansu? Tunanin yasa tashiga keke tawuce hotel last 500 naira tabiya keke dashi, ta sauka saikuma ta tsaya tai shiru tayaya zatai facing nashi? Mutumin dabata tabamai godiyan abubuwan dayama Mama ba saima rashin kunya datakemai accusing him of lalata mata? Yau Allah yana nunamata abubuwa da dama datayi abaya that were wrong gashi yanzu she needs his help desperately dudda tagama mai rashin kunya da kurin cewa she alone can take care of Mamanta bata taba sanin a day like this will come ba, takai kusan 5min tsaye take awaje cikin rana tana lissafin yanda zatai confronting Riyad kafin tadai daure tadaga kafa tashigo building din tawuce ciki direct elevator ta tafi tana addu’a Allah yasa yana nan, har office nashi taje ta tsaya gaban kofan tana kallo kafin ahankali tadaga hannunta tai knocking, jin shiru yasa takara knocking, harta fara tunanin kobezo bane dan yau ranan yawon salla ne nabiyu sai chan taji daga ciki ance “come in” cikeda isa, ahankali ta murza kofan ta shige yana zaune gaban desk nashi yana sanye dawani milk yadi shidai yanason kaya masu haske, rubuce rubuce yake da pen da sauri he seems busy batare daya dagokai ba yace “yes” ijiyan zuciya tadan sauke saikuma maganan ya makale a wuyanta batasan ta yanda zata fara maganan ba, chan dai tadaure cikin muryanta me rauni tace “aron kudi nake nema 2.5million kafin asaida gidanmu nadawo maka da kudin” tunda tafara maganan chak ya dena rubutun dayake batare daya dago kanshi ba saida takai karshen maganan sannan yadago kanshi ya kalleta tundaga kafafunta dayaga slippers tasaka dawani maroon hijabi har kasa da ko’ina dabbare dabbaren ruwan hawaye, kanta akasa takasa dago idanunta ta kalleshi but tip din dogon nose dinta dayagani that looks reddish and runny nose yagane she cried, ahankali yataso yazagayo ya tsaya agabanta yana kallonta but taki dago kanta awani irin hankali akuma taushashe yace “wat happened to Mama?” Kaman yatabo mata wani gyambon ciwo a kirji dago fuskanta tayi tazubamai jajayen idanunta shima kallonta yake baki tabude zatai magana sai kawai tafashe da kuka jikinta and everything is just shaking, tunda ya santa today is the first day yake ganin hawayen ta eye to eye, today is the first time yake ganinta this weak, wani irin sheshekan kuka kawai take agabanshi dayasa yakai hannunshi cikin aljihu yazaro handky yabata cikin wani irin soft tone yace “nothing will happen to Mama kinji” gyadamai kai tayi kaman baby tasa hannu ta karbi handkerchief din takai fuskanta tana gogewa still wasu hawayen na zubowa shikuma yajuya yadauke

car key nashi da wayanshi yakalleta yace “stop crying let’s go”tsayar da kukan tayi da kyar sannan tabishi yayi gaba fitowa sukayi atare suka shiga elevator tana gefenshi suka sauka kasa yan reception dake lobby sai kallonsu suka dasuka fito but ko’ajikinshi hanyar mota yayi da kanshi yaje wajen yabude mata kofa yana kallonta ahankali tazo ta shiga ta zauna ya maida kofan yarufe yazaga ya shiga dayan yatada motan suna tafiya sai kiranshi ake yaki dauka daga Mama takira sai Munir yakira yau hawa ana bukatanshi da sassafe yafito because of wani important work nashi da US sunce yatura musu wani abu abun yake tashigo yabarshi yanzu ma.

Dayake yasan kwanaki sunce general hospital suke using hakan yasa hanyar ya dauka motan yayi tsit sai ijiyan zuciyan datake saukewa na wayanda sukasha kuka, suna shiga asibitin yace “ina zamu” cikin muryanta da baya fita sosai tace “A&E” nan sukayi yasami waje yayi parking yafito praying babu wanda zaiyi recognizing nashi yadauki black glass nashi yasaka yafito yazagayo yabude mata, ahankali tasauko suka jera ciki har zuwa ICU daidai lokacin Dr Bugaje natahowa wajen ganin Rashida tareda wani hadadden guy yasa glass yasa takarasa shima ya zare glass nashi, yana zuwa yabama Dr Usama hannu yace “sannunku” yakalli ciki ICU dayaga Mama da oxygen unconscious yace “me ake bukata yanzu”? Anatse Dr bugaje da dudda batasan wayeshi ba but he looks responsible tace “follow me” office dinta suka bishi Dr Bugaje da Usama explained everything to him yana fahimtan komi with so much care and affection yace “idan akayi Atherectomy din zaiyi aiki bazai koma ya taushe ba or do you think nafita da ita UK within the week”? Ahankali Rashida tadago kanta takalli Riyad dayayi maganan da hankalinshi nakan su Dr sunamai bayanai, Dr Bugaje tace “kozaka kaita UK dole muyi flushing na pipe din nan inba hakaba she won’t make it” gyadamusu kai yayi yace “okay a ina zan biya kudin komi”? Dr Usama yace “account building yana nan opposite MOPD idan kafita daga this building” gyadamusu kai yayi yace “thank you” yatashi rikeda takardun biyan kudin itama Rashida ta tashi tabiyoshi ahankali yajuyo yakalleta hada ido sukayi saikuma yadauke kai yacigaba da tafiya tana biyeda shi har saida sukazo wajen ICU din da kujeru ke gaban wajen, da hannu yanuna mata kujeran gently yace “sit” kallonshi tayi da rinannun idanunta saikuma ta gyadamai kai like an obedient girl ta zauna ahankali shikuma yawuce yatafi, almost 20minutes shiru hakan yasa ta tashi tun kafin takai account building din taganshi tsaye a layin biyan kudi jitayi zuciyanta yamata wani iri game dashi, no one tunda ta taso has ever done something like this for them, saikuma tajuyo tadawo tazauna wajen tana kallon Mama ta glass almost 15minutes sai gashi yadawo ga papers a hannunshi gawata yar leda a hannunshi, yana zuwa daidai inda take zaune saiya tsaya agabanta ya bude ledan yaciro wani iced coffee yakalleta yana mikamata yace “have this” ahankali take kallonshi yanda yazuba mata ido yasa gently tasa hannu ta karba hawaye na kara cikowa a idanunta, sai kawai taji she’s feeling bad sai kuma taji tabama kanta tausayi sai kawai tafashe da kuka kaman an daketa tarike cup din gam a hannunta gwanin ban tausayi, softly yace “it’s okay, stop crying

kinji” yanda yayi maganan sai taji zuciyanta yamata wani irin sanyi ta gyadamaikai tareda kai cup din bakinta saida yaga ta kurba kadan sannan yawuce.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 24

Yadan jima acikin office din Dr Bugaje kafin su fito dukansu atare daidai lokacin kuma Baba Liman da danshi Musa na zuwa asibitin sun shigo cikin A&E din hango Rashida yasa suka taho wajen suma su Dr nazuwa wajen tareda su Riyad Baba Liman yace “ya jikin nata mai siyan gidaje wai baya gari saiya dawo ga abinda nahado dai daga masallaci” yaciro wasu kudi dabasukai 30k ba zai bata Riyad yace “kabarshi an sami kudin Baba” Dasauri Baba ya kalleshi daidai lokacin kuma an fito da Mama za’a wuce da ita operation room Rashida ta tashi dasauri zata kama hannun Mama that is unconscious Dr Bugaje ta hanata tace “wait here nan da 1hr zamu gama, sit and rest okay” komawa tayi tazauna tasake daura hannayenta kan idanunta Baba Liman yace “sai hakuri Allah yabama Zainabu lpy, Allah yabata lafiya, Allah yabata lpy” duk zama sukayi banda Riyad dake tsaye awajen, kusan 20min Baba Liman yayi sannan yatashi yace “bari naje Rashida, lokacin salla na gabatowa” ko dago kanta batayiba anatse Riyad yace “mungode” hannu Baba yabashi suka gaisa yawuce Musa biyedashi suka tafi ahankali Riyad ya zauna kan kujeran gefenta ya kalleta zaiyi magana kuma saiyayi shiru tabashi tausayi, it’s just she and her Mom. “Your Mom is going to be fine stop crying kaman this is the end” dago jajayen idanunta tayi ta kalleshi, ahankali yace “okay”? Gyadamai kai tayi.

After 2hrs aka fito da Mama but ba’a barsu sunje wajenta ma aka sake shigar da ita ICU aka connecting nata da machine again.

Har dare Riyad na hospital din nan, Rashida looks so miserable, mutane ma rahama ne, batada kowa, she’s just alone, kawai yaji he can’t leave her, koda bazai dinga mata wani magana ba but at least presence nashi is something, gashi batada karfi to handle anything, wasa wasa har 4 na asuba suna zaune wajen nan ita Rashidan ma bacci yadan kwasheta shiko idanunshi biyu, yana zaune awajen yana kallon yanda take bacci azaune idanunta sun kumbura suntum, he’s feeling just too many things towards her acikin zuciyansa.

Ahankali Mama ke bude idanunta, glass ne dakin ICU, na waje can see naciki, and naciki can see waje, ahankali idanunta suka sauka kan Riyad dake zaune kan kujeran dake facing room nata na zaman wayanda keda patient a ICU, kallon

Rashida dake bacci awahale kawai yake, kallo ne da duka abinda Mama tagani a idanunshi is so much care, love, tausayi, concern da affection daidai lokacin Dr Mumina tashigo, ganin Mama idanunta biyu yasa tace “how are you feeling Ma”? Oxygen din Mama tai yunkurin cirewa tana kokarin magana dasauri Dr Mumina tace “mekikeso tell me?” Waje Mama tanuna cikin muryan dabata fita sosai tace “I want to talk to My son” juyawa Dr tayi takalli Riyad da Mama ke nunama ta ta gyadamata kai tajuyo tafito hakan yasa Riyad yajuyo jin an bude kofa, da hannu tamai alamu yazo tashi yayi dasauri yana kallon ciki ganin Mama ta farka finally, scrub Dr Munina abashi yasaka da takalmi da hula da handglove sannan yabi Dr ciki Dr taduba komi kafin tadan zarema Mama oxygen mask din tace “kimai magana ahankali, don’t stress too much, I will be back to put it for you nan bada jimawa ba” tajuya tafita zama Riyad yayi kan kujeran gaban gadon cikeda so dakuma tausayi yakalli Mama da ko idanunta bata iya budewa da kyau yace “Mama ya jikinki”? Hannunta Mama ta mikamai alamun yabata nashi, bata hannunshi yayi da sauri Mama takama tarike gam tasake shiru tana numfashi ahankali kaman magana wahala yake mata, cikin muryan tsananin rashin lafiya dake fita da kyar tace “Riyad” ahankali Riyad yace “na’am Mama please stop talking, Mama it looks painful I’m here bazanje ko’inaba kinji”

Ahankali Mama takara cewa Riyad, kankame hannunta Riyad yayi sosai he’s just feeling Mama’s pain yace “Mama dan Allah stop talking” girgixamai kai tayi tace “Riyad lokacina yayi aduniya lokutan da Allah yadeba mini” Dasauri Riyad yace “Mama kidena magana haka zaki sami lafiya bagashi yanzu kin farfado ba eh Mama”? Dan murmushi tayi ta kankame hannunshi tana numfashi wani kala wani kala, chan tace “Riyad duk duniya dakai kadai na yarda! Kanada hankali, kanada amana ga taimako kaiba yaro bane sannan kanada iyali, ka taimakeni so da dama, thanks to you Rashida bata kwana a police cell ba” tayi shiru kuma tana sake kankame hannunshi tace “banso na rasu ban damkawa kowa amanar y’ata ba banda wanda zan bamawa, Riyad Yayana na jini ya koreni! Mijina ya koreni! Baba Liman matanshi basa sona, tsorona da tsoron ciwona kowa yake! Kaine mutum na farko daya shigo rayuwanmu baka kyamace muba baka tsorata damu ba” tasake shiru saikuma tace “kishiyata data kulle yarinyana a police station ka fito da ita nasan saita bata ma Rashida rayuwa, nasan saitayi wani abun, yanzu haka rayuwan Rashida nacikin hadari zata cutarmin da diya” hawaye ne suka gangaro daga gefen idanun Mama saikuma tafashe da kuka sosai tana kankame hannun Riyad tace “Riyad dan Allah dan Allah na rokeka da girman Allah ka auri Rashida! Sabida na samu na mutu in peace nasan na damka maka ita, wlh Rashida batada HIV kaman ni batada wani cuta ajikinta, Riyad ka taimaki yarinyana, kayi jahadi akanta, ka aureta kahadata da matarka su zauna lafiya, inaso na mutu bayan nadan tana under care naka da kukanwanka amatsayin matarka zaka karemin ita” Kai! Yanda Mama ke kuka sai yasa Riyad yaji kaman zaiyi kuka, Mama na son Rashida beyond

words, she’s on sick bed but still damuwan Rasheeda ne aranta, ahankali yakai hannunshi dayan that is free ya sharemata fuska muryanshi sounding so weak yace “stop begging me! And kidena damuwa, stop worrying Mama, Mama zan auri Rashida! And namiki alkawari zan kula da ita amana! Bazan taba cutar da ita ba! Zan tsayamata! I will be her shield! I will be her shade! Mama I will stand by her and with her, and zan so yarki and stay her husband till my last breath” wani irin murmushin kuka Mama tayi tace “bayan narasu nasan she will be shattered be there for her Riyad and make sure tayi completing karatunta na zama kwararriyan likita!” Gyadamata kai yayi yakasa magana, Mama tace “Rashida is a good sweet person wata rana you will see her other side, rayuwa ya maidata me taurin kan nan but my daughter is an Angel!” Gyadamata kai Riyad yayi yace “Mama stop talking ya isa” girgixamai kai Mama tayi tace “kaje kazo da yan uwanka zan kira Baba Liman inaso na aurar da Rashida dakaina anan kafin na rasu! Inaso naga yarinyana tai aure” “Mama bazaki rasu ba” Riyad yafadi da karfi jijiyan kanshi na fitowa daidai Dr na zuwa ganin Mama na kuka yasa tace “ohh noo, BP ta will shoot again, she needs to stay happy” ahankali Riyad yajuya yafita.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 25

Yana fitowa tsayawa yayi yakalli Rashida dake bacci kafin yawuce yafita yatafi parking space ya shiga motanshi yatada gida yawuce yana zuwa remote dake motanshi ya dauka ya danna gate yabudu ya shigo yayi parking motan ya sauko yana tafiya ahankali yawuce ciki yana bude kofa yaga Mom zaune kan kujera saida gabanshi yafadi ganinta tashi tayi tace “daga ina kake?” Rasa abinda zai fadi yayi cus ya tsani karya and ya tsani yinta da bakinshi Mom tace “did you know how important yesterday was for Royal Family kuwa? Kasan mekayi Riyad? An nemeka an rasa, Baffan ka Mai babban daki, su Kabeeru duk ansan baka gida narasa mezance? Wani dalili yasa mukaje Umara da wuri dan mudawo kayi salla da mutanenka ayi hawan salla dakai right? Kasan kalan tijaran da abin kunyan daka jamin kuwa”? Runtse idanu yayi yama rasa mezaice ahankali yace “I will handle it Mom wani important work ne yatasomin, I can create another event at my leasure time kiyakuri, its work” “important work da ake fita da sassafe adawo by 5 na asuba are you out of your mind Riyad!” Mom takirashi azafafe dayasa yasauke kanshi kasa tace “banso na zargeka the first time da matan ka tai accusing naka fushin dakayi yasa ban yarda ba but bari kaji idanma wata kake nema wlh wlh dukda kana sarki baka isa ka karomin aure ba!” Ahankali Riyad ya kalleta Mom tace “yes! Haleema is the only daughter Inlaw dana yarda da ita cus yarinyar nan worship me sama da uwarta data kawoni duniya, ban yarda da karo aure ba azo arabani da d’ana ba!

Aurenka is just a year now na auramaka yarinya datake da komi kyawun sura, good tsatso, oxford graduate, full package ce Haleema har yau ka kasa mata ciki ragon banza ragon hofi kaman ba jinin Baba Ali ba, nagaya maka idan baka dena all this abubuwan ba wlh zan mugun saba maka, yau Haleema na period still ka kasa mata ciki this month again yawo kake a duniya don't allow me to face you fa Riyad nafara bin lamarinka ina binciken ka, look at me nakasa bacci all because of you gadin dawowanka nake eh why are you doing this Riyad yaushe kadawo mara jin maganata"? Wani iri dayaji yasa ahankali yace "Mom kiyakuri" mugun kallo ta watsamai tawuce tafice daga flat din, shikuma ahankali yawuce bedroom dinshi wanka yayi yayi salla sannan yadan kwanta bawani bacci yayi ba around 8 yatashi yadauki wayanshi yakira Munir sannan yashiga wanka yafito yaji Munir a falo yana waya shiryawa yayi cikin wani mahaukacin farin gizna yasa hula ya Allah hula yamai kyau, yasaka wani bakin takalmin Berluti, ya daura agogon Vacheron Constantin a writs nashi, ya manna wani Carrera black glasses a idanunshi Ya Allah kaga Riyad saika kara kallonshi saukowa yashigayi Munir ya tsare shi da ido yace "wannan gayun ina zamu haka!?"

Kin magana Riyad yayi yana karasa zuwa falon ya jefamai car keys Munir ya chabe yana mikewa tsaye suka fito tare mota sukayi suka shiga Munir yatada motan yace "ina zamu"? Ahankali Riyad ya sauke ijiyan zuciya he's just torn between Mom dinshi and Mama, yana tausayin Mama and he feels obligated to help them, Rashida batada kowa, and he promised kanshi kafinma ya gano Rashida cewa he will helped the girl, he's doing this for the girl that saved life nashi, murya chan kasa yace "I'm sorry Mom" kallonshi Munir yayi jin abinda yafadi hakan yasa ahankali yace "wajen Baba Buba zamu" dasauri Munir ya kalleshi yace "Baba Buba? You mean Baban Ammi"? Dauke kai Riyad yayi ahankali yace "yes Kakana!" Tada motan Munir yashigayi mamaki yagama kasheshi yace "Riyad as far as I know I can't even remember the last time kaje ka gaidashi, ni banmasan kasan yana existing ba" wani iri fuskanshi yayi saikuma ahankali yace "i will change from now" fita sukayi saikuma chan Munir yace "mezai maka? You're sounding kaman you need something from him?" Shiru Riyad yayi na kusan 5minutes chan yace "aure nakeso ya karbanmin! I want to Marry Rashida!" Wani burki da Munir yaci kan titi saida yakusan creating hatsari yaja motan da gudu yana gangara wa gefe yakalli Riyad daya ciro wayanshi yana dubawa jin karan text message daya shigo wanda yaga na Haleema ne.

"Baby marana na ciwo? A ina ka kwana jiya?".

Ahankali Munir yace "Riyad looked at me! Zaka auri Rasheeda? Waya sani agida? Mom tasani? Gwaggo tasani? Baffan mu yasani? Waya sani?" Batare daya kalleshi ba yace "no one knows! Will tell when I feel like it" yasake shiru chan yadanna mata

“Kisha magani, Allah kara sauki” ya maida wayan aljihu sannan yadago ya kalleshi yace “I feel obligated to help them Munir, the girl is young, she’s a child, the Mom is very sick a ICU lets go” tada motan Munir yayi harsukakai wani kauye nan Outskirts na Kano bai kara magana ba gaban wani babban gida sukai parking ga rumfa da dalibai suka cika gawani tsoho kan kujera dake da haske kaman Riyad yaci manyan kaya na sauraransu yana hangosu ya tsare Riyad da idanu wanda ya manta rabon daya ganshi saikuma ya dauke kai sannan ya sallami yaran yama Munir alamu da hannu dasuzo.

Shiga rumfar sukayi suka zauna atare suka gaidashi ya amsa sannan yakalli Riyad da kansa ke kasa yace “yau katuna dani? Meya kawoka gidana”? Wani iri Riyad yaji amman ya daure yace “kayakuri Buba” ijiyan zuciya Buba yayi yakalli Munir yace “nasan wani abu yakawoku so tell me” kallon Riyad Munir yayi sannan yace “Buba Riyad keso ka bishi ka karbamai aure” kallon Riyad yayi yace “mesa baka nemi yan uwan mahaifinka ba kazo nan? Ko yan uwan wacce itace mahaifiyar ka yanzu?” Munir zai bude baki Buba yace “kamin shiru” yakalli Riyad yace “kamin magana koka tashi ka bar nan wajen” murya chan kasa Riyad yace “bazasu barni na aureta bane na gaya musu Buba sabida ciwon Mahaifiyarta” Buba na kallonshi yace “wani irin ciwo”? Ahankali Riyad yace “HIV” shiru Buba yayi chan yace “kanason yarinyar tsakaninka da Allah?” Shiru yayi chan yace “inaso na aureta, banso ta auri wani karya wulakantata” saikuma ahankali yace “ita ce ta ceci rayuwana lokacin da za’a kasheni” Buba yadan jima yana kallonshi sai chan yace “kutashi muje” Dasauri Riyad yadago kanshi ya kalli Buban yana dan murmushi daya karamai kyau Buba yace “saina chanza ra’ayina tunda ka tsaya kana kallona kaman yauka fara ganina a doron kasa” tashi da sauri Riyad yayi yana murmushi yawuce Munir ya bishi Buba yabisu da kallo Allah yasani yanason jikanshi sama da duk yanda zai kwatanta abin aduniya, tunda har yatuna dashi a lokacin dayakeda serious bukata haka he will support jikanshi, Babban Aminunshi yakira suka shiga bayan motan Munir da Riyad suka shiga gaba suka wuce.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 26

As usual wajajen 6 Rashida tabude idanunta da kyar sabida tsabagen gajiya da kuka, kaman ba itane tuntuni ake hayaniyan asibiti ana shiga da fice ba ko bude idanu batayi ba sabida nauyin baccinta, dasauri tamike tsaye ta tafi wajen glass door din ta jingina kanta tana leka Mama trying to see ko tana numfashi, taganta tana bacci and tana breathing, dan ijiyan zuciya tasauke takalli inda ta tashi tasan har tai bacci Riyad na nan koda yaushe yatafi oho wucewa tayi bayi tayo alwala

bayan taciro brush ajakanta tayi ta tafi masallaci tai salla tama Mama addu’a sosai tadauki Qur’ani yau ta karanta tasake ma Mama addu’a bayan tagama, tana dawowa Dr Mumina tace “Your Mom wants to see you” jikinta har rawa yake ta gyada matakai abubuwa aka bata tasaka sannan tashiga dakin idanun Mama abude kadan take kallonta dasauri taje gaban gadon ta duka takai fuskanta saitin na Mama tace “Mama ya jiki? Are you fine Mama? Kinji sauki? Sannu Mama na, sannu kinji Mama, Mama ina sonki kinji, mezakici”? Girgiza mata kai tayi bakinta nadan motsi hakan yasa dasauri takai kunnenta saitin bakin Mama, murya chan kasa Mama tace “inaso namiki aure yau!” Dasauri Rashida tajuyo takalli fuskan Mama kodai bata hayyacinta ne kodai she’s hellucinating ne? Ganin bakin Mama yacigaba da motsi yasa tasake kai kunnenta saitin bakinta ahankali Mama tace “I want someone that will take care of you koda zan mutu I want to die in peace, I told Riyad ya aureki!” Dawani irin sauri ta kalli Mama gabanta nawani irin faduwa naban tsoro murya chan kasa Mama tace “I trust Riyad! Yanada hankali zai hadaku ku biyu yarike amana! Rashida I need to hand you over to wani tun yanzu da raina kafin na rasu!” Hawaye ne yazubo daga idanun Rashida cikeda damuwa tace “Mama nace bazaki rasuba! Mama nothing will happen to you In sha Allah, Mama yaya zanyi idan kika tafi kika barni”? Kallonta Mama take saikuma tai yunkurin dago hannuwanta biyu dasauri Rashida takama hannuwanta takai fuskanta, hawaye na gangarowa daga idanunta cikin muryan Mama da baya fita da kyau tace “Rashida ina sonki, inasonki sosai my little Rauda, ina matukar kaunarki My Doctor my Rish Rish, my only baby, yarinya na kyakkyawa I love you” wani irin kama hannuwan Mama Rashida tayi saita fasheda kuka sosai, Mama itama hawaye gangarowa yayı daga gefen idanunta tace “I’m scared na mutu banyi handing naki over to anybody ba, Riyad is the only mutum da xuciyana ya yardashi aduniya! Riyad zabina ne Rashida! Riyad is my choice! Riyad is the only man dana kalla namiki sha’awansa as miji will you marry Riyad for me? For my sake? For my happiness”? Kankame hannun Mama Rashida tayi sosai tana kallon kwayan idanun Mama tana kuka itama Mama kuka take, cikin wani kalan murya Mama tace “wat if na mutum? Wakike dashi? I want to hand you over to Riyad kinji, zaki aureshi sabida inaso”? Gyadamata kai Rashida tayi at this point the only burin datake dashi aduniya is taga magaifiyarta ta warke jin kanta take idan Mama tacemata tai kisan kai zata iyayi tsabagen yanda takeso ta faranta mata rai and make her happy, cikin kuka tace “Mama I will marry Riyad sabida kince nayi! Nariga namiki alkawari bazan kara saki a damuwa ba, kome kikeso Mama shixan dingayi I will always keep you happy, Mama dan Allah karki mutu kinji, kinji Mama karki mutu ki banni kinji Mama? Kin tuna namiki alkawari zan zama likita and develop a cure for you? Mama you have to stay alive and wait for me! Mama kinga inaso kixama hope for mutanen dakeda HIV dudda already you’re, kinyi rayuwa da HIV for 23yrs, you fought Mama ba dare ba rana, kika haifeni, you protected me Mama look at me yau na girma but banda shi, Mama karki banni kitafi kinji help me fulfill this legacy nawa after all this battle yarki likita Dr Rashida found a cure and Mama is HIV FREE!!! Kimin alkawari you will live for me and zaki jirani har lokacin Mama”? Murmushi sosai Mama tayi kawai tajawo kan Rashida tadaura akan fuskanta ta kankameta sosai tama kasa magana, sun dade ahaka sannan

Mama tace “stop crying babu inda zani, I will stay for you, ranan graduation naki na saka exclusive super wax na kafa gwargwaro akai harda glass” dan murmushin kuka Rashida tayi tama kasa magana Mama tace “kiramin Baba Liman” gyadamata kai tayi tadauki wayan takirashi, yace “gashinan zuwa” around 8 Dr Bugaje tashigo duba Mama ahankali Mama tace “inaso nama diyata aure” shiru Mrs Bugaje tayi tana kallon Mama wanda somehow she understand Mama, she knows daga inda decision na Mama is coming from, gyadama Mama kai tayi tace “shine mutumin nan”? Gyadamata kai Mama tayi, Dr Bugaje tace “ba’a bari mutane su shigo ICU sukazo zansa akawoki office dina sai ayi awajen” gyadamata kai Mama tayi Mrs Bugaje zata tashi Mama tace “Mrs Bugaje” dasauri tajuyo takalli Mama, ahankali Mama tace “kina ganin zan warke?” Tambayan yazoma Mrs Bugaje wani iri amman ta daure tai murmushi tadawo tasake zama tace “Mama mutane na mutuwa amusu wanka akusan binnesu ma su farfado balle ciwo, the point is shi cuta da mutuwa duka suna hannun Allah Mama kuma Allah sai warkar dake in sha Allah kinji” daidai lokacin ta hango Riyad ya shigo tareda wani tsoho dakuma wani matashi, Mrs Bugaje tace “Ina Rashida”? Ahankali Mama tace “taje siyomin abinci dudda na ce mata banson cin komi” dasauri Mrs Bugaje tace “you need to eat Mama, bari na musu magana” fitowa tayi cikeda fara’a ta gaisa dasu tace “bismillahan ku a office dina za’ayi komi” ahankali Riyad yakalli Munir da Buba yace “kuje ina zuwa i need to get something in the car” yayi maganan yana juyawa sukuma sukabi Dr Bugaje.

Samin kanshi yayi da fitowa waje yana kalle kalle just to look for her lura da yayi batanan.

Daga cafeteria take, swallow tasai ma Mama da miyan kubewa sai bottle water ahankali take tafiya dukta rame batada karfi kawai gatanan ne, idanunta har yanzu basu washe ba sunyi ja sun kumbura, gashin idanunta sun tattare, tip na nose dinta is still looking very reddish sabida kuka, lips nata sun kara yin pinkish sosai sabida kuka, she’s is looking tiredly beautiful, daidai tazo ta wajajen A&E din taji an kwala mata kira. “Rashy” dasauri tajuyo Bilal ta hango yafito daga parking space yana tahowa wajen da dan gudu gudu sauri sauri yana sanye da riga da wando na jean da riga yazo daidai gabanta ya tsaya cikeda damuwa yace “tun jiya bana online ina jirgi coming back from Dubai ina dawowa kuma nahau baccin gajiya da asuban nan naga message dinki a group ya jikin Mama”? Yayi maganan cikeda so dakuma damuwa soyayyanta nawani dawomai fresh arai, ahankali dan batada karfin hayaniya yanzu ko fada tace “Alhamdulillah da sauki” dasauri yashiga tura hannu a aljihunshi yaciro wraps na kudi yan 500 guda biyu that’s 100k yana mata wani irin kallon soyayya smiling and feeling kanshi yamika mata yace “nazo nabaki this and to assure you cewa you’re not alone I’m here for you, Dad na UK but he will send his accountant to take care of all the bills kinji Rashy ko miliyan hundred ne Daddy will pay I got yo…….” Kasa karasa maganan yayi ganin wani hadadden guy yazo wajen ya tsaya dab da Rashida ga bakin shade a idanunshi yazuba hannu a aljihu kaman military, ko kadan Rashida bataji alamun tafiyanshi ba kawai taji tsayuwan mutum

kusada ita dakuma kamshin turarenshi daya cika mata hanci hakan yasa ta dago kanta ahankali ta kalleshi daidai shima yana kallonta batare daya kalli Bilal ba, cikin warm yet controlling voice yace “daga ina kike?” Ya Allah! Wani irin kyau Riyad yamata dayasa takasa daina kallonshi like a little girl innocently tace “abinci naje siyoma Mama” yana kallonta still batare daya dauke idanu daga kanta ba yace “and who is this?” asanyaye tace “dan ajinmu ne” bayabo ba fallasa Riyad yace “let’s go” ko musu batayiba tajuya tafara tafiya yama Bilal wani banzan kallo da hannunshi har yanzu yake position na bada komi sannan shima yajuya.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 27

Dawani irin full confidence Bilal yazo wajen ta yau but ganin wani lafiyayyen guy me kirarran jiki tareda ita and from the way he’s doing kaman saurayinta ne yasa yaji zuciyanshi na kumfa, daman Rashy nada saurayi ne? Who is he? Waye atare da ita? Waye dan wulakancin nan? Well yasan koma waye da wuya idan yakaishi kudi he will wait she will come begging for the money yana gama tunanin yajuya azuciye yayi motanshi ya shiga yabar hospital din.

Tare suka shigo ward din daidai lokacin shima Baba Liman na zuwa da ladanin masallaci su biyu, gaisawa suka tsaya yi da Riyad ita kuma Rashida ta wuce, shiga cikin ICU Nurse din da Mrs Bugaje ta turo tayi akasa Mama akan wani wheelchair aka gungurota har zuwa office din Mrs Bugaje Rashida na biyeda ita saikuma su Riyad da Baba liman da Ladanin is duk suka shiga ciki.

Already Mrs Bugaje tasa an saka kujeru duk aka zazzauna gawasu sababbin syringe agabanta guda biyu, anatse tace “welcome to my office” sannan tace “before muyi proceeding muyi asalin abinda yakawomu nan office din, as a medical Doctor i want do something for both Riyad and Rashida” ta taso dagakan kujeranta da kanta tazo gaban desk ta kalli Riyad ahankali tace “bani hannunka” bata hannunshi yayi ta kulle igiyan tajajininsa tasa a specimen box tarubuta suna sannan tama Rashida ma haka, sannan tabama wani Nurse dake wajen data kira musamman tace “Abbakar take it to the Lab I need Asap results on this two sample kan genotype blood group HIV, hepatitis da sauransu important blood test na aure” gyadamata kai yayi yace “Yes Ma” yawuce yafita takoma tazauna takalli Riyad tace “inaso kasan wakake aure ba kokanto ba zargi a zuciyanka ko na yan uwanka dake nan wajen” Baba Liman yace “kwarai” Rashida dai na wajen Mama kanta akasa takasa kallon kowa na dakin, almost 20min akayi aka kawo result din Mrs Bugaje ta karba tarike na Riyad a hannunta tamikama Riyad na Rashida tace “take open it” karba yayi ya

warware takardan ahankali, Mrs Bugaje tace “read it kowa yaji” dan shiru Riyad yayi chan yace “genotyp AA, blood group O+, HIV negative, HEP B Negative, HEP C Negative komima negative” yayi maganan ahankali, Mrs Bugaje ta bude na Riyad tana saka glass na idanunta like a professional tace “Genoyype na Riyad is AS Rashida is AA so you guys are compactable zaku iya aure, Blood group O+ shima, HIV, HepB and HepC da sauran komi negative, Masha Allah” tai maganan tana bama Baba Liman wanda kaman shine zai tsayama Rashida as uba, sannan tace “Alhamdulillah nayi part dina sai daura aure yanzu” faduwa gaban Rashida ya shigayi sosai, cikeda hikima na manya Buba yace “Alhamdulillah Masha Allah, muna addu’a muna kuma rokon Allah daya bawa mahaifiyarki lafiya Rashida Ameen Ameen, Mahaifin jikana ya rasu nine zan tsaya mishi a matsayin uba, sannan sunna ne atambayi yarinya nawa takeso amatsayin sadakinta, dan haka Riyad tambayi your wife to be nawa takeso a matsayin sadaki”. Dan murmushi Mama dake cikin ciwo tayi ahankali Riyad yakalli Rashida da kanta ke kasa ki fuskanta baka iya gani da kyau sabida yanda kan nata ke kasa cikin murya mai taushi yace “nawa kikeso na biyaki sadaki?” Kasa magana tayi kai ko motsi bata iyayi itama Mama batace komiba, Mrs Bugaje tai murmushi itama tai shiru, Baba Liman yace “tunda nine zan tsaya amatsayin waliyin Amarya bari na ari bakinsu” yakalli Rashida yana murmushi yace “yarmu me kyau ce! Ga ilimi boko da islamiyya ga hazaka gakuma son iyaye dan haka bazanmuma Riyad karamin kudi ba ko Zainabu”? Duk ciwon Mama saida tai murmushi sosai hakan ba karamin dadi yama kowa na dakin ba, Baba Liman yasake murmushi yace “dubu dari biyu mukeso akudin sadaki” harga Allah yafadi haka sabida yasan basuda kudi kuma dole amata Kayan daki dazaran Mama taji sauki an sallameta saisa yasa kudi haka, hannu Buba yasa acikin babban rigan dake jikinsa yaciro wrapper na 1k guda biyu yasa akan jikin Riyad yace “tashi kaje kabata sadakinta” kallon Buba yayi cikeda so sannan yatashi ahankali har zuwa inda Rashida ke zaune yamika mata kudin cikin wani kalan murya mai taushi yace “ga sadakin ki” hannu dasauri takai ta kulle fuskanta tana rike kukan datakeji gawani irin kunya Mrs Bugaje tace “ayiriri Amarya na kunya ijiye akan cinyanta” ijiyewa Riyad yayi yajuya yakoma ya zauna sannan aka fara daura aure agaban Buba da Aminin sa, Liman da Ladani, Munir da Riyad, Dr Bugaje da Dr Usama, Mama dakuma Rashida, agaban su aka daura aure tsakanin Riyad Baba Ali da Rashida Almustapha akan sadaki naira dubu dari biyu!.

Mama na ganin an shafe Fatihan daura aure sai kawai tajawo Rashida ta rungumeta tana wani irin emotional kuka bata taba sanin Allah zai nuna mata auren yarta Rashida haka ba, itama Rashida kuka take she can’t believe ita aka daurama aure just now, wai yanzu tazama matar Riyad? Dreaming takeyi ne, tasowa Buba yayi yazo wajen su yace “kidena kuka shi ciwo na Allah ne, hakama waraka ta Allah ce, komi yayi zafi maganinsa Allah, Allah zai baki lpy kinji” gyadamai kai tayi ahankali Mama tana sakin Rashida tace “Riyad” zuwa wajen yayi yadan saci kallon yanda

Rashida ke sharce hawaye Mama tace “nagode Riyad!” lumshe idanu yayi, Buba ya juyo ya kalli Rashida dake kuka sosai sai kawai yaduka agabanta hannunshi yakai yakama kuncinta hakan yasa Rashida takalleshi da jajayen idanunta, cikeda wani irin tausayin yarinyar da kaunarta dayaji Allah yasamai hakanan yace “dena kuka Allah zai bawa Mahaifiyarki lafiya kinji” gyadamai kai tayi ahankali cikeda kunya ganin tsoho dashi ya duka agabanta, murmushi yayi mata yasa yadauki byro daya gani akan table na Dr Bugaje yace “dan tsammini takarda Docta” paper Dr Bugaje tabashi rubuta number shi yayi yabama Rashida yace “duk randa Riyad yamiki wani laifi, koya bata miki rai, call me zanzo har gidanku na sabamishi, saina ciwa mijin naki mutunci” akunyace ta sunnar dakai Mama tai murmushi sosai Buba yace “karba” ahankali Rashida tasa hannu ta amsa sannan yatashi yakalli Munir yace “muje ka maidamu gida” dasauri Riyad yace “zan maidaku Buba” kallonshi Buba yayi yace “stay da iyalanka kabar Munir ya kaini” wani iri Rashida taji jin ance iyalanka shikuma Riyad saiya gyadamai kai suka wuce suka fita nurses sukazo suka wuce da Mama aka fita da ita, ganin Riyad har lokacin tsaye a office din itakuma Rashida takasa mikewa sai hawaye take gogewa yasa Dr Bugaje ta tashi itama tace “bari na bisu” gyadamata kai yayi tawuce tafice ganin haka yasa itama Rashida ta tashi da sauri tazo zata fice kawai taji yakama hannunta, mugun faduwa gabanta yayi da saida ya lura dasauri ta kalleshi hada idanu sukayi yamata wani irin kallo kaman baimasan yarike hannunta ba gently yace “who is that guy”? Yanda yamata maganan yana kallon kwayan idanunta dasuke ajike yasa takasa jure kallonshi takasa magana, dan jawota yayi sabida yanda take so light this days kawai ta taho dab dashi gabanta nafaduwa sosai mehaka yake mata, cikin whispering voice yace “me tsakaninku”? Heart dinta na racing sosai tace “bakomi classmate dina ne” “mesa yakawo miki kudi?” Dan kallonshi tayi yanda yau yake kallonta saitaga kaman ya banbanta da yanda yasaba kallonta ada, sake sauke kanta kasa tayi tace “nayi seeking help a group namu for Mama” hannunshi dake free ya mikamata yace “your phone” dan kallonshi tayi saikuma ba musu tasamai wayanta a hannunshi ya karba a aljihu taga yasaka wayan nata ahankali yace “the next time he approaches you tell him someone owns you now! And that person is Me!” dago kanta Rashida tayi da sauri ta kalleshi yanda yake maganan kaman yaci wani competition saikuma ta gyadamai kai yace “zanje and get you food and clothes you need to shower and change” sake gyadamai kai tayi takosa yasaki hannunta dataji yana mata kaman shock, ahankali yasaki hannun yace “let’s go” tare suka fito har zuwa ICU Mama da Mrs Bugaje dake tare duk suka kallesu murmushi Mama tayi Dr Bugaje tace “congratulations Mama, Allah ya sanya albarka, Mama yanzu saiki kwantar da hankalinki ayanda nake ganin yaron nan Riyad he will protect Rashida no matter what so dan Allah kiji sauki BP ki ya sauko” gyadamata kai Mama tayi tanajin wani karfi da lafiya na shiganta.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 28

Gyadamata kai Mama tayi cikeda farin ciki dudda maganan ta baya fitowa da kyau tace “Alhamdulillah Mrs Bugaje wlh ina cikin wani irin farin ciki da bazan iya misalta miki shi ba” murmushi tayi.

Wucewa Riyad yayi yatafi yabar Rasheeda awajen, fitowa Mrs Bugaje tayi takalli Rasheeda tace “scrub in kije wajen Mamanki” da sauri ta taso tayi cikin ICU din bayan tasaka abubuwan Mama na ganinta cikeda karfin hali tasa hannunta asaman hanci tace “ayiri…..” saikuma tahau tari da sauri Rashida tazo wajen tace “Mama stoppp” ijiyan zuciya ta sauke tace “Rashida kinsan yanda nake murna kuwa naga aurenki Alhamdulillah kinga na warke tass kalli kafafuna harsun soma sakewa” kafafun Rashida takalla saikuma takalli Mama yanda taketa murmushi is not like tanason auren nan, infact ita bamata taso da burin tai aure ba sannan one single feeling batada shi for Riyad kawai dai daga jiya saita fara kallonshi ta fuska daban compare to before data tsaneshi, jiya ta gane Riyad shi mai sonsu ne ba kyamatan su ba, yana kula da Mama, shine the first person that genuinely know them kuma yasosu ahaka sannan ya tsaya musu, kallonta Mama tayi tace “me mijin naki yace? Ina yaje”? Dasauri ta kalli Mama jin kalman mijin yamata wani banbaran, murya chan kasa tace “wai zaije yakawomin kaya da abinci nai wanka” wani irin blushing da Mama keyi saida Rashida kawai ta maida Mama tv tana kallo is this aure of a thing yakesa Mama farin ciki haka ko wani abun ne dabata sani ba to wani abuma? Is just auren nan, sai murna Mama keyi. Wajajen 4 Riyad yadawo tareda Munir dake rike da basket na abinci shikuma yana rikeda wani paper bag dan babba Mrs Bugaje ta kallesu tace “yauwa I was waiting for you to come inaso na maida Mama wani daki kodan this big occasion she seems very happy, her biggest fear and worry is yartane yanzu data damka maka ita kaman 90% of matsalanta sun tafi” anatse Riyad yace “I prefer private single room” gyadamai kai Dr Bugaje tayi tasa Nurse ta gunguro Mama daga dakin tana fadamusu dakin da za’a kaita, dan satan kallon Rashida Riyad yayi dayaga idanunta sundan soma sabewa, first floor aka kaisu wani single room mai kyau da komi ciki akai connecting Mama da machine na zuciyan still sannan Nurses din suka fita ijiye abincin Munir yayi shikuma Riyad ya kalli Rashida tareda bata bag din, dan kallonshi tayi saikuma tasa hannu asanyaye ta karba murya chan kasa ta yanda dagashi sai ita zasuji maganan yace “shower before I come back, zanje mosque” gyadamai kai tayi suka wuce mosque Mama tawani yunkuro ta tashi kaman maison gulma tace “zonan mugani meya kawo miki? Imaza jeki wankan ke to karya dawo ya ganki daka daka” kallon Mama kawai Rashida take with a huge suprise kaman ba Mama ba, farin cikinta yaki boyuwa, bag din tamikama Mama, Mama ta zazzage tana fito da abin ciki tana washe baki sosai abaya ne kala uku acikin jakan duka black black amman sun hadu duba tsayinsu tayi taga 58 wlh tsayin yarta, sai cream dakuma wasu lafiyayyun turare guda biyu, daya cikin abayan Mama tazaba tadauka tabata tace “ungo wannan zakisa jeki wankan, ki chanza breziya da wando kuma, akara wanke baki ba kyau

miji yaji wari” sokoko Rashida ke kallon Mama wai ba Mama ce mara lafiya ba take maganan wani miji? Ita Mama tadauka ta Riyad take she’s just after her taji sauki kawai shine burinta, just to make her happy ta karbi wanda ta zaba mata tawuce, akwatinsu tabude tadauki bra da pant tashiga bayin dakin that is very neat tai wanka ta shirya tai alwala tabude turarukan ta fesa wow saida ta lumshe idanu sunada wani irin feminine scent mai dadi, yafa gyalen tayi akai tafito Mama ta bita da kallo sabida yanda yarinyarta takoma tsaf kalan yar masu kudi tai murmushi itakuma ta shimfida dadduma tai salla Mama tace “zoki zubamin abincin bikin ki” dasauri ta juyo ta kalli Mama dake murmushi sai kawai ta tashi tawuce tadauki plate tana bude warners din ta debama Mama tuwo tazauna gaban gadon tana feeding Mama ahankali tace “Mama ai kin warke ko?” Gyadamata kai Mama tayi tace “na warke tass bakiga inacin abinci ba” murmushi tayi tace “thank you Mama dakika warke” tana cikin bata abincin suka shigo dakin duk yanda Riyad yaso ya daure karya kalleta kasawa yayi baitaba ganin abaya yama wata kyau kaman yanda yaga wannan yama Rashida kyau ba, dudda Mama bata cinye tuwon ba but taci rabi, sai satan kallon yanda Riyad ke kallon yarta take kaman tace yadauketa su tafi kawai dai dan rashin lafiya ne, Mama tace “deba kici kema” girgizama Mama kai tayi alamun bazata ci ba, Mama tace “Riyad kaga yarinyar nan batason cin abinci fa wlh sai kayi da gaske” murmushi Munir yayi duk suka zazzauna tareda Mama har magrib sannan suna tafi.

Yau kwanan Mama 3 a hospital she’s recovering like magic tun jiya sukai resuming amman kiri kiri taki zuwa taki maganan ma sabida kar Mama tace ta wuce tatafi, tana zaune tareda Mama around 8 na safe Mrs Bugaje tashigo dakin ganinta tareda Mama yasa tace “ba some of yan class naku naga a A&E ana wardround dasu ba? Wani department kike this week?” Ahankali Rashida tace “Gynae” hararanta Mrs Bugaje tayi tace “my friend stand up and go” Mama tace “wai dama sun koma?” Mrs Bugaje tace “tun jiya ma taki zuwa” dakanta Mama tayi abaya bada zafi sosai ba tace “wuce kafin na saba miki” tashi tayi tawuce wajen drawer daki tadauki jakanta taciro gogaggen lab coat dinta, daya daga cikin abayan da Riyad yasaimata ne ajikinta hakan yasa ta warware gyalen tai rolling aka sannan ta warware lab coat din tasaka tadauki stethoscope nata pink ta makala a wuya tadauki pink crocs nata tasa sannan ta dauki turaren ta fesa, tunda tana asibiti yasa bazata dauki jaka ba, pen ta dauka ta makala a pocket nata sannan tadau wani dan jotter tasa a aljihu, earpiece nata ta dauka zatasa a pocket ta tuna haryau Riyad bai bata wayanta ba kuma takasamai magana ahankali ta maida ear piece din jaka ta rufe, ta rufe wardrobe din sannan tajuyo takalli Mama da Dr Bugaje ke dubawa tace “natafi” “adawo lafiya Amarya” dan turo baki tayi tana kallon Mama sannan tabude kofan tafito tafara tafiya tawuce staircase daidai ta sauka kasa Riyad na zuwa wajen hada ido sukayi yana sanye da wani jumper dark brown daya haska fatanshi yasa bakin glasses a ido, ranan nan Mama tagayamai tanaso ya tsaya akanta tagama karatunta na likita hakan yasa yasan yes she’s doing medicine but today is the first

time yake ganinta cikin kayan dake nuna ita likita ce, ahankali yakai hannunshi ya zare glasses daga idanunshi yazuba mata mayun idanunshi, da sauri tasauke kanta kasa gabanta na faduwa azuciyanta tace bantaba ganin wanda baya kunyan kallon mace irinsa ba, murya chan kasa tace “ina kwana” batare daya amsaba koya dauke ido akanta ba yace “ina zaki?” Ahankali tace “department namu munyi resuming” yana kallonta still yace “which department” da dan kankanuwan murya kaman ba Rashida ba tace “this week ina outpatient department a gynae” gyadamata kai yayi yace “let’s go” dasauri ta kalleshi but haryayi gaba hakan yasa tabishi suka jera har ward dinsu yabita sannan ya tsaya yace “go” agabanshi tawuce tashiga consulting room 2 yadan jima tsaye saikuma yajuyo.

Mama na zaune ita kadai tai shiru tana tunani though good tunani yau take akai knocking kofan tareda sallama daga ciki tai murmushi jin Riyad ne tashigo “shigo d’ana” bude kofa yayi yashiga yana murmushi yawuce wajen gadon yaja kujera yana zama yace “you look good Mama, ya karfin jikin?” Murmushi tamai tace “Alhamdulillah ya iyalinka?” Ahankali yace “Alhamdulillah Mama” murmushi tamai tace “ka kwatanta adalci kaji, mata munada kishi dan haka ka lallashi matarka da kyau kaji Riyad” gyadamata kai yayi yace “toh Mama” cikin farin ciki tace “kaga nasoma samin sauki sosai ana sallamana muka koma gida sai afara shirye shiryen bikinku ko sabida Rashida ta tare gidan ka” gyadamata kai yayi feeling happy ganin how excited she’s with the whole wedding yace “Mama kome kikeso haka za’ayi” wani irin murmushi tayi harda dan kyalkyala dariya kadan tace “inaso ama Rashida lalle a hannu amata kwalliya saikuyi hoto kubani amaidashi frame nasaka a falona ina kallonku kullum” dan murmushi Riyad yayi yace “to Mama haka za’ayi” murmushi tayi sosai saikuma tace “tayani daga gadon na zauna” tashi yayi ya taba botur din dake dago gado gadon yataso Mama tai kwanciyan zama ya gyara mata bargo sannan yakoma ya zauna ganin tai shiru tana tunani yasa yace “tunanin me kike kuma Mama?” Ahankali tajuyo takalleshi cikin dan damuwa kadan tace “kana gani nakira mahaifinta na sanarda shi an daurama yarshi aure?” Shiru Riyad yayi, dan murmushi Mama tayi ganin baice komiba tace “I put you in a tight spot ko? Kona kirashi ma bazan sameshi ba yayi blocking dina tun lokacin amman nakan turamishi sakon waya duk ranan birthday Rashida na gayamai yarshi ta shiga shekara kaza kaza dakuma lokacin dataci jamb taci UTME aka bata admission medicine na aikamai sako amman haryau bansan ko yana ganin sakona ba ko baya gani ba” ijiyan zuciya ta sauke takalli Riyad tace “bari nabaka labari na yau Riyad”.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 29

Ahankali Mama tace “ni yar jigawa ce, anan kauyenmu yake ance kakan kakana daga Morocco yake wai saisa mukeda haske, iyayenmu dani da Yayana Sama’ila suka haifa, iyayena nada gonaki da dama a kauyen mu, Babana is a very very big farmer har su CNN sunyimai interview, banda nashi gonakin yanama mutane managing gonaki kaman gonakin sarkin kano nan marigayi Baba Ali naji yarasu, Allah ya jikanshi da rahama” Ahankali Riyad yace “Ameen” yana kallon Mama jin she just mentioned Babanshi, Mama tace “dudda a kauye muke Babana yasani makaranta yace yanaso na zama yar jarida nima namai interview wata rana, yayana Sama’ila shi baiyi boko ba tare suke komi na gona da Babana, kauyenmu ba school wani next village yakesa yayana Samaila na kaini makaranta kullum a machine dinsa saina dawo da dakaina” tai shiru tace “ina JSS 3 akwai wata rana nazo gida naga wasu maza guda biyu sunzo gidanmu na gaidasu natafi dakin Mamana, so daga bayane Baba kecemin ai sarkin kano ne da kaninsa Al Mustapha sunzo wajen Baba, nace Baba ina doki bangansu da kayan sarakuna ba, to alokacin nasan ashe sarakuna na private outing suyi normal shiga kaman kowa, gasu basu wani girma sosai ba Babana ya girmesu duka dan yadan manyanta, bayan kwana biyu Baba yacemin Kanin sarki na sona” Mama tadanyi murmushi tana kallon wani zoben dake hannunta tace “kafin kace me haka akamana aure anan kauye aka tafi dani gidan Sarautan Kano”.

Wani irin kallon Mama Riyad keyi to be honest besan Mama ba, dudda yasan labarin lokacin auren anata cewa Baffa yakaro aure daga kauye and Baba supported him shiyamai auren, shida baison shiga mutane, banda hakama yawancin idan zakaga matayensu da Alkyabba zaka gansu unless you’re very close to them ko kana zuwa bangarensu you hardly knows fuskansu, ko first wife na Baffan su is because tana zuwa wajen Mom akai akai yasa yasan ta daba hakaba dabai santa ba. Ahankali Mama tace “Riyad even though Mujitappa Baban Rashida yayi hurting dina deeply bazan taba iya ignoring the fact cewa that Man loves me and care for me kaman ba gobe ba, bai bar kowa ya hantareni ba, dakanshi yake koyamin etiquette na gidan Sarauta da sauransu, yasa aka cigaba da koyamin karatu a gıda, ya kuladani Riyad bai bar kowa yayi hurting dina ba hatta Jummai kishiyata” tadanyi murmushi tace “ance tana kishi dani alokacin sabida bata haihuba then nikuma bayan bayan 1yr da aurenmu saiga ciki watan cikin daya ajikina nafara ciwo sosai da saida aka kaini asibiti lokacin anmin all test but banda HIV banda komi nadawo gida yacigaba da kuladani yana nan nan dani itama Jummai surprisingly tana kula dani, tadena min kallon kishiya, she was so happy then zan haifa musu Baby” Mama tadanyi shiru kafin ahankali tace “ina around 5month Baba na da Mama na sukai hatsari a motan dazai kawosu Kano dubani, kawai abin yakara birkita jikina ina shiga 6month nai landing hospital ciwona was serious dahar ICU aka sani cus banajin magani, banci bansha na rame kaman tsinke, akamin test dayawa the next thing was inada HIV!” Mama tai shiru tareda fuzar da iska idanunta yayi ja tace “imagine ina around 1-2 months da ciki anmin all test ba’aga HIV ba ina 6 months da ciki ace inada shi dole

Muji ya yarda maza nakebi da cikina da aka fadamai inada HIV, an sashi yazo yayi test din shima da matarshi Jummai sukayi su negative abinda yasa yasake yarda da zargin inada HIV sabida laulayin ciki yasa babu abinda ya shiga tsakanina dashi tundaga watan farko harna 6 din nan cus bana iya komi Riyad mugun laulayi nayi” Mama tai shiru tace “haka nadanji sauki aka sallameni yatafi dani gida naje na samu an kira yayana Sama’ila an tara jama’a a fada dan Muji bai iya fushi ba” ta share fuskanta chan tace “koran cin mutunci, koran toxarci, koran tijara akamin agaban kowa ana nunani ana shiga barayina bayi na watso kayana waje wai sabida cikin nema ba’amin duka ba aka korani no one! No one Riyad, Babu wanda a masarautan nan ya tsayamin ba mai Martaba Baba Ali ba! Ba mai Babban daki ba! Ba sauran matan sarki ba! Babu ne kawai aka koramu ni da Sama’ila ana tunkudani” runtse idanu Riyad yayi Mama tace “munafita daga fada Sama’ila yahau zubamin Allah ya isa bai yafemin ba wannan tijaran dana jamai da cikina ina fasikanci karna sake na bishi, Riyad haka yatafi ya barni dan uwana na jini biyar babu a hannuna ni da aka sallameni daga asibiti da safen ranan, nahau tafiya a hanya yunwa menene menene naje wani gidan abinci na wanke kwanuka na kusan kwana goma sannan natara kudi natafi kauyenmu nan ma Samaila yace ban isa na zauna ba, bashi bani nace to araba gado abani yace yaji haka yaraba yabani miliyan biyu nadawo nazo ina neman gida ahaka na sami gidanmu dakake gani nasaya akan miliyan daya agine ahaka nasai yar katifa nadan natsu nafara tunanin rayuwan to me yafaru? HIV Taya zan samu? Banda Mujitapa babu namijin daya taba rikemin hannu aduniya sai Babana da Yayana.

Nai tunani nai tunani narasa tayaya nasamu, nama kaina fada natashi natafi general asibiti, na hadu da Mrs Bugaje tun tana matsayin resident Doctor ta taimakeni da shawarwari da abubuwa da dama, dakuma ilimi kan yanda ake rayuwa da HIV, duk yanda zanbi nabi dan na samu Muji ya saurareni yaki bansan ya akayiba ko bibiyata Jummai take haka ta gano gidan nan ita tazo ta fallasama kowa na anguwan mu inada HIV nice Matar kanin sarki aka koroni menene menene, dabadan nina sayi gidan ba da sun koreni tuni, ahaka cikin wahala na haifo Rashida duniya ta CS, ban bata nono ba gudun karna bata cutan, duka kudadena na gado suka kare a siyamata madara da sauransu hakan yasa na dage nafara aikatau still ina zuwa asibiti ina karban maganin HIV da ake bamu free sabida y’ata banso na mutu inaso nataso da ita inaso na rayu nayi accepting ni mutum me HiV ce, nacigaba da renonta harna soma gazawa ta karba aiki awajena tun tana primary school sabida Rashida nada kwazo” hannu Mama tasa ta share fuskanta tace “Gidan Sarauta wani irin gidane da bada kowa ya dace ba kaman ni yanzu I’m one, haryau bansan yanda na sami ciwon nan ba but nasan it’s connected to gidan, banason wani alaka da gidan nan har abada!”.

 SANYI DA ZAFI

✍M SHAKUR

EPISODE 30

Faduwa gaban Riyad yayi sosai jin abinda Mama tace, ahankali Mama tace “gidan nan gave my life tabo dabazai taba goguwa ba, gidan nan yasa y’ata is like this, ranan nan i told you karka shiga maganan nan sabida Jummai can hurt you Riyad basu da imani, look at yanda suka maida rayuwana yau, look at how far they’re willing to go tana kulle innocent yarinya a police cell” Mama tafashe da kuka tace “jibeni kaman tsinke nida keda kiba and Riyad nobody stood for me yayi defending dina, tsoro ne, menene oho but kowa stood there and watch me being humiliated, Riyad those people hurt me! An min sheri anmin kazafi, na wahala sannan poor child dina ta wahala look at Rashida, all her life washing plate da washing bayuka daban daban in different organizations takeyi just to feed me and sponsor school nata” Mama tai maganan tana fashewa da kuka dayasa Riyad yatashi daga kan kujera soyake yama cema Mama sorry yakasa saikawai yajuya yafita da sauri ya shiga sauka kasa yana karasa sauka beben yana cin karo da Munir dake kokarin hayowa rikeda Basket na abinci da sauri yakama hannun Munir yashiga tafiya da sauri da sauri Munir yabishi hankali tashe yace “Riyad what happened you’re scaring me, Meya faru?” Saida sukaje jikin mota Riyad ya tsaya tareda dafa kanshi Munir dasauri yace “Riyad menene wai”? Fuzar da iska Riyad yayi ahankali saikuma yakalli Munir yace “Rashida is our cousin! Yarinyar Baffa ce!” Dawani irin sauri Munir yace “wait wait, wat”? Ya ijiye basket na hannunshi yana kokarin connecting dot din yace “Mama ce daman matar Baffa daya kora me ciki?” Gyadamai kai Riyad yayi dasauri Munir yace “but ai ni nataba ganinta sau daya tazo gaida Ammi tanada kiba could it be sabida pregnancy ko maybe lokacin ban wani yin wayau nayi ba sosai ba I think ina around 10yrs lokacin saisa ban gane ta ba?” Lumshe idanu Riyad yayi yadafa mota yana sauke ijiyan zuciya sannan yadago yakalli Munir yace “Munir Mama don’t want anything to do with our family and I’m here na auri Rashida without knowing su waye su? I want to tell Mama wayeni!” Da sauri Munir yace “idan tace ka saki Rashida fa?” Dasauri yakalli Munir saikuma yakasa magana yadan duka ahankali awajen yayi shiru even though wani bangare na cemai karya fadama Mama yanzu yabari a sallameta but another part na zuciyanshi na cemai gwara yafada mata here and now she deserves to know waye ke auren yarta, tashi yayi yakalli Munir dake kallonshi yace “let’s go” Munir baicemai komiba yabi bayanshi suka tafi ahankali yabude dakin ya shiga yaga Mama na bacci peacefully.

Ijiye abincin Munir yayi yace “she’s sleeping zomuje muyi salla” fita sukai salla by 2:00PM Rashida ta dawo ganin Mama na bacci yasa ta duddubata tai murmushi tazauna tana kallon kulan abincin tadauki plate tabude kulan jellof rice tadeba kadan cikinta harya saba bata iyacin abinci she’s really missing her phone hakan

yasa ta faraci tana cikin ci aka bude kofan Riyad ne hada ido sukayi da sauri ta dauke kanta ya kalli abincin dake plate din datakeci saikuma yakaraso ya ijiye wani waya wanda ga dukkan alamu sabo ne but bai bata kwalin ba ya ijiye gefen gadon ahankali yace “be using this ur sim is inside” kallon wayan tayi iPhone ne dudda batasan iPhone nawa bane dan bata saba dasu ba bataso ta karba but kuma batasan yanda zatai rejecting wayan ba, abu tahadiye a wuyanta murya chan kasa tace “thank you” juyawa yayi haryakai kofa yace “bari naje if anything comes up call me my number is inside” gyadamai kai tayi ahankali sannan yabude kofa yafice itakuma ta tsaya tana kallon wayan kafin chan tasa hannu tadauka tana taba screen din yabude gallery tafara shiga taga all pictures nata na yar vivo nata na wajen wanda yawanci hotunan pages na textbooks datake karatu dasu a library ne sai few pictures nata da lab coat da picture nata da Mama saikuma tashiga wajen waka taga songs dinta duka akwai murmushi tasakeyi sai kawai ta ijiye plate na abincin da duka baifi 3spoons tayiba ta kwanta jikin Mama tana kallon hotuna ahaka har akai magrib Mama tadan tashi taci abinci saikuma tasake komawa bacci magungunan ta da alluran dama suna sata bacci sabida abun ka da mai BP.

Zaune suke cikin mota wuraren 8 nadare gaban A&E, bude bayan motan akayi aka shigo Jummai dataci lafiyayyen shadda tadago kai takalli officer data shigo tana murmushi tace “thanks for coming Grace” Grace tace “you’re welcome Hajiya but wat is so urgent dakika kirani asibiti” bandage dake saman hancin Grace Jummai ta kalla tace “I want to end this mutanen da yarsu tamiki this but I want to confirm something are you sure Sarkin Kano ne yazo yayi bailing yarinyar Grace?” Dasauri Garce tace “100%, Oga yafadi mana haka fa kinga yanda jikinshi ke rawa ne daya budeta” mamaki yakara kashe Hajiya Jummai tace “how did Riyad know Zainab? Lokaci da aka kori Zainab Riyad was maybe around 13 yrs, yanzu duka dukanshi he’s 36, Riyad da baya zama gida how ya sansu haryake ma’amala dasu?” Saikuma ta kalli Grace tace “yasa kayan sarki dayazo?” Dasauri tace “no Ma, nothing shows he’s a king banda bodyguard dake binshi” shiru Hajiya Jummai takarayi saikuma tadauki wayanta cus takasa yarda Riyad ne taciro hoton Riyad ta nunama Grace tace “shine?” Shiru Grace tayi bata wani kalli fuskanshi ba lokacin dazata shiga Rashida take kallo but kaman shi hakan yasa tace “eh kaman shi but I’m not sure kinsan da daddare yazo and bana officer dasuke fitowa ne nikuma nake shiga” gyadakai tayi tace “okay” sannan tadauki wata bakar ViVa leather tabata tace “use this hold body I will look for you soon when it’s time to cook the girl up” murmushi Grace tayi tana hango how thick ledan looks da kudi ta karba tace “Hajiya I will remain loyal forever and ever thank you Ma saida safe” tabude motan tafice ta maida ta rufe Hajiya Jummai takalli wata mata dake gaban motan bakakirin da ita fuskanta sai uban muni ga kujera tace “kin shirya aikin ki Yar Mussa?” Da sauri matan tace “kwarai Hajiya! Rayuwata taki ce” Hajiya Jummai tai murmushi tana kada kafa tace “sauka kije ki tabbatar kin zuba ko a abinsha ko a abin ci, saikinzo gida” Dasauri tace “toh” sauka tayi anan parking space tawuce tana gyara hijabin

jikinta sannan tawuce ta shiga cikin A&E tana sunnar da kai kasa, dakin cleaners tawuce dinsu tawuce anan ta dauki roban mop ta cire hijabi tasaka wani green riga da wando uniform sannan tafito ward tashiga gogewa tass kafin tawuce sama first floor lokacin 9:00 knocking gaban kofan 211 tayi but shiru hakan yasa tabude tashiga ciki Mama na bacci ga drip ga komi na aiki, Rashida itama tana zaune kan kujera but ta kifa kanta kan gadon takama hannun Mama tana bacci tana minshari kadan kadan dan bata gaji sosai yau ba, maida kofan Yar Mussa tayi tarufe tace “laaa nazo goge goge suna bacci” ta tsaya takalli dakin tass babu CCtV, bude idanu Mama tayi kadan dan ta dade tana bacci da sauri Yar Mussa ta juya taciro mop tashiga goge gogenta, dan tari Mama tayi jin wuyanta ya bushe sosai murya chan kasa tana kallon mai moping tace “dan taimakamin da ruwa” ijiye mop din Yar Mussa tayi ta juyo da sauri ta taho tace “to” dukawa tayi tadauki bottle water guda daya daga jakan bottle water dake wajen tanajin dadi azuciyanta tace “perfect opportunity” tabude goran tana tura hannu a aljihunta da sauri taciro wani syringe dake dauke dawani substance ta matsa da sauri aruwan tana jijjigawa, ahankali Mama dataji shiru tace “bakiga ruwan bane ko Rashida ta chanza musu wuri ne? Bude fridge kika dan Allah” Da sauri ta taso tana murmushi tace “a’a nagani” tamikama Mama goran tana ijiye marfin goran saman gadon sannan tajuya tacigaba da moping din da sauri da sauri, sosai Mama tasha ruwan thirsty kusan rabin goran tasha sannan tadauki marfin ta rufe, Yar Mussa tagama moping tazo gaban gadon takalli ruwan da Mama tarage tace “dan Allah dan bani Insha nima kishin nakeji” Mama tace “kidauka karkisha ragowana” dasauri matan tasa hannu ta fizge ruwan har saida gaban Mama yafadi hakanan hakan Yar Mussa tace “nadau sabo bazan shanye ba wannan ya isa karmuyi asara bari naje kiyi bacci abinki” tana maganan tayi kofa bayan tadauki mop da bucket tabude kofan tafita tashiga next room tacigaba da aikacenta.

Mama tabita da kallo saikuma tace “hala batasan inada HiV ba” saikuma takalli Rashida da yau bata minshari sosai sabida batai aikin wahala sosai ba tashafa kanta tana murmushi tace “Amaryan Riyad” knocking akayi aka shigo office din Dr Bugaje ce sanye da scrub tana kallon Mama tace “kinga sai yanzu nafito daga surgery nan dana gayamiki wlh nace nadubaki kafin natafi, akwai wani abu dake miki ciwo?” Tayi maganan tana makala stethoscope dan duba heartbeat na Mama, Mama tace “lafiyana kalau wlh kaman ki sallame ni gobe ma naje nafara shirye shiryen bikin Rashida” dan dariya Mrs Bugaje tayi tace “mother Inlaw of the year Mama” kafafun Mama ta kalla da sun sabe kusan rabi tace “Alhamdulillah Mama kin sami lafiya sosai Welldone Mama, you’re a superwoman, wannan hartai bacci” tanuna Rashida, Mama tace “ai Rashida gatada nauyin bacci kamanme” Mrs Bugaje tace “tom bari naje Mama saida safe, banda tunani kinji ko” murmushi Mama tayi tace “to nagode, a gaida yara” juyawa Mrs Bugaje tayi hartakai kofa Mama tace “Doctor” juyowa Mrs Bugaje tayi Mama tace “ina alfahari na sanki, nasan ko bani Rashida nada wata uwa da mentor, thank you for everything” dan blushing tayi tace “Mama stop thanking

me ki warke sabida ki koma gida nan da jibi ko gata” Mama tace “shikenan a kiyi tuki ahankali dare yayi” “toh” tafadi tana fita Mama kuma tashiga shafa fuskan Rashida har bacci yasoma kwasheta kafin chan bacci yayi nasaran dauketa.

Jijjiga da bed keyi up and down yasa cikin nauyayyen bacci Rashida tadan bude idanunta sabida yanda motsin ke mugun damun kanta, kafin chan motsin yayi yawa tabude idanun gabaki daya tana tashi zaune, Mama tagani tana wani bankarewa tana kama cikinta tana. “Hasbunaallahu wa ni’imal wakeel, Lailaha illallah wayyooo cikina wayyooo cikina” dawani irin sauri Rashida tai ihu. “Mama” daidai Mama tawani irin mirgino zata fado daga gado Rashida ta tareta takamata ajikinta tama rasa mezatayi, bata taba ganin Mama in this pain and agony ba cus tanada dauriya na ban mamaki, kankame Mama tayi datake abu kaman zata tashi ga kafafunta basa motsi tsabagen azaba tace “Rashida cikina wayyooo Rashida cikina, Rashida cikina” “somebody help me Doctorsssss!” Rashida tai wani irin ihu daya dauka ako’ina daidai lokacin kawai hancin Mama yafara fitowa da jini dayasa tasake buga wani uban ihu. “Doctors” daidai nan Dr Mumina dawasu nurses suka shigo ganin Rashida da Mama akasa yasa tace “meya sameta”? Jikin Rashida kawai rawa take bamata iya magana ba, kankame Mama tayi a hannunta Dr Mumina tashiga saka handglove hakama Nurses din wasu Drs ma na shigowa aka daga Mama daga jikinta aka daura akan gado Rashida na wani irin kuka tace “wat happened to her? Why is she bleeding daga hanci” Dr Mumina tama Nurse alamu tafita da Rashida wayanta Rashida ta dauka Nurse tafita da ita, rawa jikinta yake tana tsaye awajen Doctors sai zuwa suke ana shiga dakin da Mama ke, tanajin wayyyoo Allah cikina, cikina abinda Mama ke fadi kenan, tunda ta taso bata taba ganin Mama tai ihu tana kururuwa for ciwo ba sai yau, chan Rashida taji ana call Professor call him fast, taga nurses sun fito da gudun gaske sai kawai taji kafafunta na lankwashewa ta zube akasan wajen flat hannunta ya shiga rawa tabude wayan nata tashiga contact taga Riyad hakan yasa tai dialing number.

Yau sabida damuwa yamai yawa koda yagama abinda zaiyi da Haleema anan kan gadon ya kwanta bayan yayo wanka, wayanshi yahau kara hakan yasa yabude ido is so odd akirashi da night wayan yatashi yadauka Rashida tafito jikin screen din dayasa kawai yaji gabanshi yafadi fita yayi daga dakin yasauko kasa daidai wayan na katsewa yayi dialing number back yana ringing ya daga. Anatse yace “meke faruwa?”Nunfashinta kawai yakeji bata iya magana da kyar tace “zan…..zan mutu” katse wayan kawai yayi yakoma sama yashiga saka kaya Haleema na tashi dan tun ringing na wayan ta tashi tace “ina zaka Baby”? Ahankali yace “sleep fita zanyi” zatai magana yadauki car key yafita da sauri yashiga motanshi yana danna remote gate yabudu yaja motan aguje dayake dare ne wlh cikin 5 good minutes ya iso asibitin sama yahayo aguje, tana zaune a inda take akasa ta hangoshi yana tahowa yana kallonta she felt as if her strength is coming towards her, dawani irin gudu

cikin kuka ta tashi tai wajenshi batai wata wata ba tawani irin fada cikin kirjinshi ta kankameshi gamgam kaman wani zai rabata dashi tana wani irin kuka tama kasa magana, ahankali yasa hannunshi on her back yariketa yama kasa magana sai breathing fast, suna ahaka saiga Mrs Bugaje da hijabi tana gudu sosai tawuce su tai dakin kawai his mind tell him something hakan yasa yayi hugging nata so tight tareda manna mata peck a wuya, cikin wani irin murya na lallashi yace “stop crying Jewel, come” yadagota hannu yasa ya sharemata fuska yace “I’m here now Mama will be fine kinji”? Gyadamai kai tayi yakama hannunta saiya sauka kasa da ita yayi wajajen wasu kujeru ya zaunar da ita yaduka agabanta yace “stay here bari naje sama naga meke faruwa” gyadamai kai tayi yatashi yajuya yakoma sama gabanshi faduwa kawai yake non stop, direct yabude kofan dakin daidai lokacin da babban professor kecewa ke daga hannunshi yana kallon wristwatch dinsa yace “Time of death 4:57AM” chak Riyad ya tsaya kanshi na wani irin making bell sound yashigabin kowa na dakin da kallo tundaga kan Mrs Bugaje datai mutuwan tsaye tanama Mama wani irin kallo da idanunta ke kallon sama ga jini a hancinta da bakinta na gangara har lokacin, kafin ahankali Professor yakai hannunshi dake sanye da glove ya rufemata idanu sannan yaja farin zanin gadon yarufeta.

EPISODE 31

Sarawa kawai kan Riyad keyi, Mama dasuka gama hira jiya, he left this hospital shida Munir jiya around 7 Mama was absolutely fine tana bacci, Mama was out of danger, kafafunta kumburin sun soma sauka, now tarasu? Yakasa anything tunanin, ahankali Mrs Bugaje tasa hannu tadauki wayan Mama data gani saman fridge tajuyo takalli Riyad that looks terrible tabashi wayan anatse tace “call Baba Liman!” Saikuma muryanta na rawa tace “how do I face Rashida?” Hannu yasa ya karbi wayan cikeda taurin zuciya na maza yadanna wayan yaga Baba Liman a dial calls yakira asuba tayi so wayan na ringing yadaga da sallama me sanyi ganin lokacin da ake kiranshi da wayan Zainab, ahankali Riyad yace “Baba Riyad ne Allah yayima Mama cikawa!” “Innalillahi wa Innailaihi raji’un! Allah ya gafartama Zainab! Zainab Allah yasa karshen wahalan kenan! Nazo ne ko zaku taho da ita? Ahankali Riyad yace “zamu taho da ita” Baba Liman yace “toh! Allahu Akbar akwai lokacin da Zainab ta taba bani number dan uwanta Sama’ila tace duk randa ta mutu nakirashi nagayamai shi kadai ne jininta daya rage aduniya, hakkine agari ni nayi hakan bari nakirashi” ahankali Riyad tace “toh” yadaga wayanshi yakira Buba yakira Munir duk sukace gasunan zuwa, yakalli Dr Bugaje yace “lemme get Rashida” gyadamai kai tayi tana hawaye maganan da Mama tamata dazu na dawomata sabo azuciya.

Rashida na zaune inda ya ijiye ta gabanta sai faduwa yake none stop bini bini tana goge hawaye, kamshinshi kadai taji hakan yasa tadago takalleshi wani irin tsawaa kirjinta yayi sabida yanda taga idanunshi sunyi jaaa, amman ta daure tana dafa

kujera tamike tsaye ta tako zuwa gabanshi ta tsaya tahau bude baki tanaso tai wani specific tambaya but tambayan yaki fitowa daga bakinta, Riyad jiyayi zai fashe da kuka ganin reaction na Rashida, runtse idanunshi yayi dayasa Rashida tawani irin kurma ihu a inda suke tace “nooooooooooo!” Saikuma tabi ta gefenshi ta kwasa da gudu tai sama yabita shima, ahankali tabude kofan Mrs Bugaje tafara gani tsaye idanunta sunyi jaaaaa hakan yasa tafara kokarin daga kanta tanaso takalli gadon dakin amman tana tsoron kallo kafin ta daure ta kalla taga Mama kwance an lullubeta da farin zani, wani kalan lankwasewa kafafun Rashida sukayi nan daidai Riyad na shigowa yazo gabanta ya duka gadon tamai pointing tana nunawa da hannu still takasa magana sai kuma tafara wani irin jiniya tace “Ma…….. Ma……..Mama na……..ni……” kaman ta zare ta nuna kanta tace “ni…… Mama…..Mamana……Maman Rashida…..ni….ni…..Mama na ni, nawa My Mama achan”? Kai! Wani irin fadowa hawaye sukayi daga idanun Riyad yanda kalaman ke fita daga bakinta adaburce, akuma hargitse, ya gyadamata kai gently yace “Mama ta ras……..” “Noooooooo!” Rashida tai wani irin ihu tafashe da wani irin kuka da majina yafeso daga hancinta har zuwa baki tana wani irin babbaka kuka tana dukan kirjin Riyad da babu karfi a hannunwanta, daidai Munir ya iso shima yaci birki ya tsaya yana kallon yanda Rashida ke kuka beating Riyad chest, kuka Rashida take dake tsumarai daidai nan shima Buba ya iso da manyan abokanenshi mota guda sukayo dawata mota doguwa cikeda hikima da dabara yace “Munir kayi procedures kabiya komi abamu gawanta mutafi dashi” yakalli Riyad yace “Riyad take her to the car kujiramu tunda bamusan gidansu ba” ahankali Mrs Bugaje tace “I will go with you Riyad nima bansan gidan ba” daga Rashida dake kuka yayi kawai ta sheme a suma daukan ta yayi chak yawuce mota ya ijiyeta abaya.

SANYI DA ZAFI

EPISODE 32

Cikin minutes Buba yayiarranging canopy ganin ranayasoma fitowa ga jama'a atsaye, aka kawo taburmaitundaga makarantan sa akashimfida awaje, Munir daRiyad suka kawo likafani dahandglove da turare dasuaudugu Matan anguwa dukababu wacce tai attempting yimaMama wanka da Mrs Bugaje ketambaya duk sunki karsu samiHIV, wai tsoro, hakan yasa MrsBugaje ta karbi komi tashiga kairuwa ciki ita zatayi.

Ahankali Rashida ke budeidanunta takalli Mrs Bugajedake kanta anatse tace"Rashida!" Tashi tayi zaune dagudu tana kallon matan layinsuda hijabai da suka cika falonwasu na kuka suna kallontawasu na mata kallon tausayisai kawai ta tashi

